BURINA

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

Ya Allah kabani ikon kammala wannan littafi lafiya, yanda nagama DANA SANI lafiya, Allah kabamu ikon yin amfani da abinda yake cikinsa mai kyau

1

KARAAM !

Cikin sauri yadago golden eyes dinsa, wanda kallo daya zaiyi ma dasu ka rikice, kafita hayyacinka, musanman yanmata saboda tsabar kwarjininsa da kyau irin nasa, meyasa Abba zai kirashi da wannan sunan? Koya manta da matsayin mai sunan agareshi ne?

Ka tsareni da ido kana kallo na inayin magana, cikin sauri ya sunkuyar da kansa, saboda girma da tsananin biyaiyar dayakewa iyayen nasa

Hajiya juwairah dataga kamar alhajin yanajin shakkar yiwa karaam magana nan da nan tayi gyaran murya, taga alama alhaji kunyar sa yakeji, ita kuwa har gobe ganinsa take Kar, to me zaisa taji shakkar yiwa danda ta Haifa acikinta magana, akoda yaushe kallan yaro take masa

Kafin tayi magana Sai Abba yabata mamaki wajan fadin

Karaam ko bakada lafiya ne in shiga duniya da kaina in nemama magani? Kokuma insa anema Maka? Meyake damunka ne?

Kallan mahaifan nasa yayi, alamar bai Gane inda maganar tasu ta dosa ba

Ganin haka yasa hajiya juwairah tace, yau shekarka shida da aure, inban manta ba kana 28 years mukayi Maka aure, gashi har kun shekara shida har yanzu bamuji wani labari ba

, shine muka yanke shawarar yima ka magana muji idan bakada lafiyar Tarawa da iyalinka ne, sai mu bada umarni anemo Maka magani karam

Taqarasa maganar idonta cikin nasa

Ya Allah, Wai meyasa suke kiransa da wannan sunan ne? Bayan sunsan dacewa bai saba dashiba

Cikin sauri yasauke Dara daran idanunsa qasa daya Gane inda zancan nasu yasa gaba

Keyarsa yafara sosawa da key din hannunsa, cikin qasaita da birgewa yafara yiwa iyayen nasa magana

"Am... Abba ni lafiya ta kalau, kawai Allah ne bai kawo ba, Amma Ina bakin kokari na, Abba BURINA a duniya shine inyi abinda kukeso "

Yanda yake maganar cikin shagwaba hakanne zaisa mai karatu yaji aransa cewa kode shi kadai ne awajan iyayensa? Kokuma tsabar hutu ne da Jin dadi yasa shi wannan maganar

Abba ya daga Kai sama, kawai de yana jinsa ne, Amma maganar tasa ta kunnan sa na dama take shiga tafita Ana hagu

Domin shi har yanzu aransa bai yarda karaam yanada lafiya ba

Hajiya juwairah aranta tace ga mutum har mutum, Amma ace har yanzu tsawon wannan lokacin bashida magaji

Itafa dande tasan babu yanda za'ai mace tabawa kanta ciki ne, tasan dole wannan aikin danta ne, daba hakaba da tuni tasashi ya yankarwa matarsa red card

Haba wannan masifa har Ina

Jijjiga kafarta takeyi, wanda ta kasance daya Akan daya

Tace shikkenan tashi kaje, zamusan abin yi

Cikin gentle yatashi ya tattara wayoyinsa da car keys dinsa yafita, iyayen nasa suka bishi da kallo

Gumi Abba yafara, duk da esin dasuke zube acikin qayataccen falon nasu, yakai dubansa ga hajiya juwairah itama hakan take awajanta, yagane hakanne ta hanyar wuyanta, domin kuwa hamshaqiyar sarqar gold din dake wuyanta ruwa ne ya mamayeta

Yace hajiya Yaya zamuyiwa yaron nan ne?

Nannauyar ajiyar zuciya ta sauka tace alhaji kawai inaga agwada nema masa maganin, Dan Naga alamun in muka daka tatasa har jaki zaiyi qaho bamuga result ba

Abba yace hakan za'a yi

*** *** ***

Garin bauchi qaramar hukumar ALKALERI

Mai girma Abdallah karaam, Dan asalin Garin ne, anan yataso yayi karatun sa dakomai, inda yasamu tarbiya daidai misali daga wajan iyayen sa kafin Allah yayi musu rasuwa, har Allah ya hadashi da hajiya juwairah sukai aurensu na soyaiya, ta kasance itace danginsa, domin kuwa Bayan rasuwar iyayensa kowa watsi yayi dashi, government school yayi, Bayan ya kammala digirinsa na farko, mahaifan hajia juwairah suka tsaya masa kaida da kafarsu yafada harkar siyasa

Yariqe maqamai da dama ta fannin siyasa

, wahalar daya fuskanta a rayuwa itace tasashi yin adalci Akan harkokin siyasar sa, domin kuwa yaji abin babu dadi

Sosai yake da temakon talakawansa, hakanne yasa yayi farin jini afadin nigeria baki daya

Bai Bata lokaci da fara mulki ba, yakoma cikin bauchi da zama, har Allah yabashi muqami na governor of bauchi state, yanemi iyayen hajia juwairah dasu dawo bauchi dazama, Amma sukaqi amincewa, acewarsu sunyi masa temako ne saboda Allah

Ahaka harda gama tenure sa, inda suka ci gaba da zama abauchi shida iyalansa,

Bayan wani lokaci iyayen hajia juwairah suka rasu

Hakan yasanyasu acikin damuwa, ganin basuda wani gata Sai Allah, wannan dalilin ne yasa suke da mutuqar San yara, Allah Allah suke Allah yabawa karaam yara nagari

Saide kudin da maigirma Abdallah yake wadaqa dasu yasa hajia juwairah daukar ita din wata ce, ta manta da baya, mace ce mai izza da son nata, inde Akan yaran tane to fa zata iyayin komai

Amma a bangaren maigirma Abdallah bahaka abin yakeba, shi mutum ne na mutane, kowa nasa ne, talaka Dame kudi duk Abu daya yake daukarsu, wannan dalilin ne yasa jama'ar Garin bauchi har yau basu dena mararinsa ba

Basuqi ace yadauwama yana kan karagar mulki ba

Yayansu uku rak adunia, Anty mufeeda, tana aure agarin Abuja, inda ta auri Dan wani attajirin Dan kasuwa, suna kiranta da anty mufy, batada matsala da kowa halinta kamar na ubanta, kowa natane, tanada faram faram da jama'ah, shekaru dayawa dayin auren ta, Amma danta daya, tasa masa sunan qaninta karaam Ana kiransa da junior

Sai karaam, wanda yaci sunan kakansa, suna kiransa da daddy, miskili ne na gaske, saikayi Zaman 30 minutes dashi Amma maganar sa batafi biyu ba, hadaddan gaye ne nabugawa ajarida, bayasan qazanta, Koda yaushe yana cikin qamshi

Sumar kansa kullum tana sheqi saboda tsabar kudin dayake kashe mata

Karaam ya hadu qarshe, dangaye ne na gaske ,fatarsa mai kyau ce, wankar tarwada ne, Amma hutu da Jin dadi yasa yazama fari, yanada dogon hanci, da Dan qaramin baki, idanunsa daidai misali ne

Yayinda yake da yalwar gashin Gira, bangaren tsawo kuwa karaam ba gajere bane, yana tsayi, haka hannayensa a mummurde suke, Koda yaushe idan yana gida safe da yamma to gym yazame masa wajibi

Kullum cikin motsa jiki yake

Yayi karatu sosai, yataka matakin masters degree saida yahuta sannan yayi phd dinsa a fannin medicine

Cikekken doctor ne, but baya aikin komai, kawai a zaune yake yana hutawa

Hakan ne yasa mahaifinsa yasakashi cikin har Kar siyasa Shima, Amma tunda yayi sanata

Bai qara marmarin siyasa ba, daga nan ya watsar yake hutawarsa, domin kuwa shi bayasan hayaniya, Shide barshi yazauna yana daddanna waya abinsa

Kuma iyayen basu yi masa maganaba Akan hakan, ko me ne dalili oho

tun yana 28 years iyayen sa, suka hadashi aure da wata yar minister mai suna salma

Suna San junansu sosai babu laifi

Yanzu yana 34 year's Amma Ba haihuwa babu alamar ta, hakan ne yasa hankalin iyayensa yatashi, saboda su Allah yadora musu kaunar yara, tunda basu dasu gaba dayansu familyn bawani yawa ne dasuba

Shima yana zaune acikin bauchi shida matarsa salma, but gidansa yana kusa da gidan iyayen sa, wanda idan kika shiga bazakice anahiyar Nigerian kikeba

Sai yar auta Shahida,batajin magana, tsaf takwaso halin momynsu hajiya juwairah, duk samarinta manyan guy's ne, kullum tana cikin yawo da qawayanta, Bata ganin mutuncin mutum taka kowa take son ranta, kuma hakan yasamo asali ne da daurin gindin data samu awajan momy juwairah

Farace sosai, tanada doguwar face, hips dinta yan dede, batada kayan Sawa daya wuce Riga da wando, da wahala ka ganta da atamfa

Rayuwarsu tana tafiya normal basuda matsalar komai, face rashin haihuwar karaam (dady) dayake damun su

Back to story

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

2

Nahiyar Niger

Yankin zinder wato damagaram nada girman murabba'in kilo mita 145,430,kuma kidayar da akayi a shekara ta 2001 ta nuna yawan yawan jama'ar Yankin sun Kai 2,080,250.

Kabilun dake zaune a damagaram sun hada da hausawa, fulani, larabawa da kuma abzinawa har zuwa shekara ta 1926 birnin zinder ne babban birnin Niger

Yawancin tattalin arziqin Yankin damagaram ya dogara ne Akan noma da kiwo dakuma kasuwanci

Yankin zinder na makwabtaka da wasu jihohin nigeria, kamar jihar jigawa ta kudu, sai jihar katsina ta kudu maso yamma

Acikin gida kuwa Yankin zinder na iyaka da agadez ta Arewaci da diffa ta gabashi da maradi ta yammaci

Malam Hamani danda daga wannan Yankin yake, matarsa daya mai suna Samia, Allah ya hore masa ilimi ta fanni daban daban, har hakan yasa yaransa suma suka koyi wani Abu daga cikin ilminsa, yagaji ilmi tun daga kakanni, dagashi sai dan'uwansa ibrahima Wanda Allah yayi masa cikawa tun bai dade da aure ba

Bayan iyayensa sun rasu ne, yatattara komai nasa,yahada kan yaransa sukayi qaura suka dawo nigeria da zama

Inde magani kake nema, basai nafadaba, kasan mutanan Niger suna da wannan baiwar

Cikakken bafulatanine na damagaram

Garin jigawa, qaramar hukumar maigatari, unguwar kofar fada, acan Bayan Gari sunada gidaje sababbi, cikinsu harda wani qerarran gidan wani dansanda dayake zaune a Abuja

Anan Malam Hamani yayi yasauka

Suna zaune lafiya shida iyalansa, haka kuma Koda yaushe gidan ba'a rabashi da mutane, masu siyan magani

Cikakken Hervarlist ne, haka kuma yanada Islamic chemist

Wanda dansa yake kula dashi

Yaransa biyu rak a duniya, Shahid da kuma Amal

Malam Hamani yana San yaransa, baya kaunar abinda zai taba lafiyarsu, yanzun nan zai zari takalmin sa yaje har gida yaci ma mutunci yadawo

Sabanin matarsa Samia datake da sanyin Hali

Shahid hadadden gaye ne na karshe, fari ne tass, yanada cikar gashin gira, hancinsa Dan daidai, bakinsa mai kyau, mai karatu duk yanda zan fasalta muku Shahid bazaku ganeba, Amma zaku fahinceni idan kukai tozali da pic dinsa abangon littafi na

Yanada fara'ah ga yar'uwarsa Amal, Amma inka dauketa da wahala kaga yasaki jiki da mutum awaje

Shaquwace ta gaske atsakanin su

Sosai yanada magana, Amma fa idan yaso, rashin karfin mahaifinsu ne yasa sauran kyansa rashin futowa

Amal kyakkyawar yarinya, yar lelen yayanta tare da babanta, ba siririya bace, ba kuma me irin qibar Nan bace

A a dede misali ne, jikinta amurje yake, batada wata alamar yunwa

Allah yayi Mata sura mai kyau da daukar hankali, akwai diri ajikin Amal, hips dinta abaje yake, yayinda boobs dinta suke madaidaita a tsaye

Kowanne irin kaya tasa kyau take, farace tass, Babu alamar quraje ko tabo ajikinta

Gashin kanta kuwa dogo ne sosai, mai shegen santsi, da cika, Amal kenan

Akan kataba Amal gara kaje kaciwa Malam Hamani mutunci, yaqi jinin ataba masa ita, yana kaunarta sosai

Kwata kwata shekarun ta basu wuce 19 year's ba

*** *** ***

Tana zaune a qayataccen falon nasu, atamfa ce ajikinta Holland mai tsadar gaske, lemuka ne agabanta tana Sha tana kallan labarai

Abba ne yashigo, jama'ah suna take masa baya, saida suka rakoshi cikin falon sannan suka juya

Zama yayi tare da kallan hajia juwairah, uwargida sarautar mata, kede Koda yaushe bakya rabo da kwalliya

Murmushi tasaki Wanda da gani kasan taji dadin maganar tasa har cikin ranta

Alhaji ai Kaine sirrin

Murmushi yasaki yace Allah ko

Batare datace komai ba,tace yanzu de sannu da zuwa, yakamata muje kayi wanka ka shirya Kasa wani Abu acikinka

Lemon dake gabanta yadauka yace a a aqoshe nake , wannan kwalliyar kadai ma aini ta wadatar Dani

Alhaji kaide bakada dama wallahi, Koda yaushe cikin zolaya kake

A a to kinga laifi na dannayi wasa da iyali na? Tace a a

Yace yauwa namanta ban fadamiki ba, nasa abincika min maganin wannan Yaron, agwada ko za'a dace

Fuskarta ce tabayyanar da fara'ah, tace to alhaji Allah yasa adace, tunda anyi na asbiti babu cigaba ai gara akoma na Islamic din

Lemon hannun sa ya ajiye yace hakane Kam hajiyata

Gaba dayansu sukasa daria, domin kuwa maganar Tasa, tabata daria

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

3

Dukanta yake da dorinar datake hannun sa, tana tsugunne idanunta jajir saboda tsabar kukan datasha, bazaki fadamin dalili ba?

To ita Wai meyakeso tace masa?

Cigaba yayi da dukanta har hakan yayi sanadiyar ficewar niqab din dake Fuskarta

Ido yazuba mata, saboda shi harga Allah kawai de yana ganinta tana zuwa school dinne, Amma baitaba ganin Fuskarta ba, saboda Koda yaushe tana cikin niqab

Jikinsa ne yayi sanyi, lokacin daya dakata da dukanta

Batace masa komai ba tamiqe tana goge idanunta da niqab din hannun ta

Borin kunya ne yasashi cigaba da fada gudun kada sauran dalibai su fahimci halin daya shiga

Da dorinar hannun sa yake nunata yace kiqara yi mana acuci maza kiga irin hukuncin dazan sake yimiki

Dan iskanci yara Dan kunga kun girma shine ba'a isa afada muku kuji ba, acuci maza do kace Awannan makarantar idan mutum bazai iya kiyaye wa ba, to karya sake dawowa

Yana gama fadar haka yajuya yabar cikin ajin

Malam nura kenan

Dasauri Rumaisa tazo ta rungume ta, tana goge mata hawayen idonta

Itama idanunta sun ciko da qwalla, tace

Kiyi hakuri Amal, kinsan Malam nura baida mutunci

Cikin sheshshekar kuka nace to Rumaisa yayakeso nayi? Gashin kaina yake so na aske kokuma so yake na Bude kaina yagani

Ki yi hakuri Amal, zomuje mu zauna

Suna zama malama tashigo suka fara daukar karatu, dayake islamiya ce ta yamma, basu wani dau lokaci ba aka tashesu

Suna tafiya ahanya Rumaisa tana qara Bata hakuri Akan abinda Malam nura yayi Mata, tace Dan Allah karki bari baba hamani yaji

Amal tace karki damu Rumaisa nayi miki alqawari

Dahaka suka rabu kowa yayi gida

Tana shiga gida da sallama tayi dakinta, umma da Shahid suna zaune a tsakar gida, dayaga zata shige daki nan da nan yafara tsokanarta kamar yanda yasaba

Amalun aiki!

Dasauri ta juyo cikin sigar shagwaba tace umma kin ganshi ko?

Kawai sai Tasa kuka, basusan dama akusa take ba

Ba umma kadai ba hatta Shahid saida jikinsa yayi sanyi, saboda yasan cewa ba wannan ne Karo nafarko dayake tsokanarta ba, tunda tariga da tasan bahaka sunan nata yake nufi ba ko kula shi batayi

Amma yau abin harda kuka

Littafin hannun sa ya ajiye yaqaraso wajan ta, har sunajin numfashin juna

Yakama hannun ta yace keda waye?

Tace ni Yaya ba komai,

Tsareta yayi da idanunsa, cikin rashin wasa yace nace miki keda waye?

Kyaleshi tayi tashige falonsu

Shima binta yayi da kallo, tare da take mata baya

Zama yayi Akan kujera ya shareta, ganin ya shareta ne yasa tataso ahankali tafada jikinsa tasaki kuka

Yanajin ta ya shareta

Saita yaga kukan nata sosai takeyinsa alamar tana tare da damuwa hakan ne yabashi damar rungume ta ajikinsa

Umma tana daga waje tana kallansu batace komai ba kawai de ta girgiza kanta

"keda waye? "

Abinda yace kenan

Cikin hawaye tabashi labarin Malam nura

Dasauri Yakama hijab dinta yacire aikuwa farar fatarta ce ta nuna shedar dukan datasha

Da mamaki yace shi nuran ne yayi miki wannan dukan?

Karaf akunnan baba hamani

Dagatawa yayi da shigowa falon

Cikin kuka Tace wallahi Yaya shine, Wai nayi acuci maza, ni wallahi Yaya bansan acuci mazaba

Kinga yi shiru, zan sameshi anjima har gidan iyayensa zanje

Yanzu bari inje indora miki ruwan dumi ki gasa jikinki ko?

Hawayen idonta ta goge tace yawwa Yaya to jeka

Kallanta taga yanayi tace mene?

Da ido yayi Mata Nuni da ita, Dan haka cikin sauri ta dagashi tana daria, Shima fita yayi, yafara neman tukunya

Umma cikin ranta tace haka de kuka iya, dagakai harshi

Shi yaji andaketa kokulani baiyi ba yafita

Kaikuma Kaine mai dafa mata ruwan wanka

Lokacin datayi aure aisai kubita gidan mijin kuci gaba dayi mata bauta

Da gaske yake wanke tukunyar, yaje fanfo yana tara ruwa, dagokan dazaiyi yaga tana masa daria

Kallan sa ya maida kan umma yace umma kiga yanda take min daria

Allah zan jiqaki

Lalle Yaya matarka ta huta da wanke wanke taci gaba da dariyar ta, aikuwa ruwan yatara a kofi ya watsa mata

Lalala Yaya shine ka jiqani

Aikuwa tana futowa ta dauki tiyo tatara, ta setashi nan da nan ya jiqe

Tiyon ya qwace ahannunta, tana kokarin karba shikuma yadaga kan tiyon sama aikuwa Sai saukar ruwan Sukaji akansu

*** *** ***

Cikin sauri yake tafiya,yaci baqar suit daka ganshi kaga cikakken S.S daya daga cikin security din gidan ne, yana zuwa falon ya tardasu a zaune Abba da momy juwairah

Rissinawa yayi yace yallabai angama binciken komai, komai da komai yana cikin wannan takardar

Takardar ya karba yabude, what!

Jigawa fa nagani

Ai yayi Nisa dayawa

Shide aqame yake baice komai ba

Glass din idonsa yacire yace zaka iya tafiya

Cikin sauri yajuya yafita

Momy juwairah tace yanzu de alhaji Muda muke nema aiko birnin sin ne maje

Yace hakane, Toshiknn zansa aje a karbo

Cikin sauri tace a a alhaji, Wai Yaya mun samu dama zakayi sakaci da ita, kawai kaje da kanka kokuma ni inje

Yace haba, taya zan barki kije, Babu damuwa insha Allah gobe zansa ashirya mana tafiya Sai muje, saide fatan Allah yasa adace

Tace amin

*** *** ***

Sallama yake kwadawa a kofar gidan

Salamu Alaikum!!

Daga ciki matar gidan tace Kai wannan wacce irin sallama ce haka Kamar Wanda yazo gidan makafi

Daga ciki tadaga murya tace Ana zuwa

Shima daga nesan yace basai kinzo ba, kituromin uban nura

Ha'ba ta riqe tace to uban nura kuma, wannan kuwa waye?

Mijin ta taje tasanarwa Ana sallama dashi, yana fita, yameqawa Malam hamani hannu, Badan yasan darajar amsa gaisuwaba da bazai meqa masa hannun ba

Suna gaisawa yace ba zama yakawoniba, Malam lado kajawa danka nura kunne karya kuskura yaqara taba yarmu

Kullum bashida burin daya wuce yadauki hannu yadaki Amal, Akan acuci maza, to yarmu Bata cutar maza saide su cuceta, kafada masa haka kawai

Malam lado yace aransa yace ikon Allah yau kuma tijarar akaina ta sauka

Afili yace masa Toshiknn, za'a kiyaye insha Allah

Baba hamani baice masa komaiba yakada binjimar sa yayi gaba

*** *** ***

11:30 am A dutse international Airport jirgin su yayi landing

Kai tsaye government house suka wuce shida jama'ar sa

Suka gaisa da governor of jigawa state, inda suka samu tarba mai kyau, sai Bayan sun huta ne, aka hadasu damanyan motoci guda uku qirar Benz, dukansu glass dinsu tinted ne, basu Bata lokaci ba suka dau hanyar maigatari

*** *** ***

Oya Bude bakin

Babu musu tabude Bakinta, yacigaba da bata abincin

Sake debowa yayi a spoon din yanufo bakinta, kawar da kanta tayi tace Yaya please naqoshi

No banyarda ba yarinya, oya Bude

Haka yadinga dura mata abinci, agogon hannun ta ta kalla mai sauqin kudi, tace Yaya lokaci yaja, karna makara islamiya, zuba mata shanyaiyun idanunsa yayi, yayi qasa da murya yace ni bazan samu abani ba kenan?

Yanda yayi maganar cikin sigar dabata saba ganiba hakan ne yasa ta kalleshi cikin sauri

Danya kawar da tunanin ta yasa Shima cikin sauri yace shikkenan to, tunda bazan samuba

Amal tace to Yayanah karka damu nida kaina zan baka dinner saikace kakoshi

Promise?

I promise Yayanah

Dahaka ta tashi cikin sauri ta zumbula qaton hijabin islamiyar ta, gabanta yana faduwa tana darurar haduwarta da Malam nura, ko yau Yaya zasu qare?

Saurin datake ne yasa tariqe niqab dinta ahannu

Tana futowa kofar gida tayi turus ganin wasu manya manyan motoci a kofar gidansu

Gawasu mutane sunci baqaqen suit kowa yasa baqin Glass alamar ba mutunci

Motar tsakiya taga sun nufi sun Bude kofar ta, aikuwa wani babban mutum yafuto

Da ita yafara tozali, ganin kallan datake musu ne yasa yace yarinya zo mana

Ahankali cikin nutsuwarta taqarasa har inda yake ta rissina tare da fadin Ina wuni?

Fuskarsa dauke da murmushi yace lafiya Lau

Nan ne gidan Malam hamani danda?

Yafadi haka yana mai Nuni da gidansu tace eh nan ne

Yace yauwa maza jekice yayi baqi

Dayake akwai kofar shiga ta waje, tanan tashiga aikuwa yana zaune yanajin radio

Tana fada masa yace tashiga gida ta dauko musu ruwa

Tana kawo musu ruwan, tagansu harya shigo dasu cikin falon, ss din suna tsaye, maigirma Abdallah ne kawai a zaune

Ruwan nazuba musu, Babu alamar qyanqyami yadauka yasha

Baba ne yace Amal jeki dauki wancan qwan kiyi addu'ar samun qaruwa ajiki ki kawomin

Ajiye jakar makarantar tayi tare da niqab din yadauki qwan Takoma gefe tafara rubutun da tawada cikin nutsuwa

Maigirma Abdallah ya kalli baba hamani da mamaki aransa yace yanzu wannan qanqanuwar yarinyar ce zatayi wannan aikin?

Baba hamani kamar yasan abinda yake tunani yace masa alhaji karka damu

Yaron wajanki zai haihu

Um karka damu, zai haihu da yardar Allah

Tana gama rubutun ta maiqowa baba hamani qwan

Tace baba natafi islamiya yace Amal

Tajuyo yace daura niqabin naki mana

Murmushi tasaki tace to baba

Tsayawa tayi tadaura tafice, gabanta yana faduwa saboda makarar datayi da kuma shakkar haduwarta da Malam nura

Abba yana zaune yana kallan ikon Allah, sai yaji sun birgeshi da alama mutumin akwai tarbiya agidansa

Baba hamani ya katse masa tunani da fadin to gashi alhaji

Wannan qwan guda daya ka ganshi?

Abba yace eh

Yace to afasashi asoya, abawa Yaron da matarsa sucinye

Abba yace duka su biyun qwai daya?

Baba hamani yace alhaji muna baka kana Qin karba

Inbakaso tashi jeka

Abba yace a a muna so ya karba yayi godia

Yace nawane kudin maganin?

Baba hamani yace dubu hudu, Amma nama ragi kakawo dubu biyu

Abba yace to mungode, yadauko bandir din kudi guda biyu,har dubu Dari biyu

Yace to gashi mungode

Baba hamani yadauka yacire dubu biyunsa yace jeka da kudinka mu Bama karbar cin hanci irin naku yan nigeria

Abba Abdallah yayi murmushi yace to nabawa yata Amal kyauta

Murmushi baba hamani yayi yace to Amal tana godia alhaji, za'a Bata

Daganan su maigirma Abdallah sukai godia tare da sallama suka tafi

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

4

Ahankali take tafiya kamar yanda tasaba cikin nutsuwa, da zumbulelen hijabinta

Tana shiga harabar makarantar taga malamansu maza awaje, gabanta ne yayi mugun faduwa lokacin datayi ido biyu da Malam nura ta cikin niqabinta

Har qasa ta tsugunna ta gaidasu Amma abinda yabata mamaki shine yanda ko maganar makara babu Wanda yayi Mata acikinsu

Tana qarasawa ajin, ta zauna kusa maisah, kallan ta tayi tace Kai Amal yau kin makara dayawa, Bayan kinsan halin Malam nura bashida 'm'

Wlh Rumaisa baba ne yasani aiki

Shiyasa nayi latti, maisah tace Ayya, aikuwa aikin iyaye shine gaba Akan komai

Safna abdulrashid daya daga cikin daliban tace Amal, ashe jiya baban ku yaje har gida yayiwa Malam nura kashedi Akan kinayin acuci maza

Yuuuuu kallo yadawo kan Amal, cikin mamaki tace baba kokuma Yaya Shahid? Ni ban fadawa kowaba Sai yayanah

Safna cikin sanjin gulma tace um aikuwa ya kyauta Dan yayi mana maganin wulaqancin Malam nura

Kafin inyi magana shugaban makarantar yashigo tare da wasu daga cikin malamai cikinsu kuwa harda Malam nura, idonsa qur akaina

Dana lura ni yake kallo saina sunkuyar da kaina

Ba'a dauki tsawon lokaci mai tsawo ba, shugaban makarantar ya shaida mana cewa kowa yaqara dagewa yayi gyaran karatun sa dakyau saboda Ana gab dayi mana bikin sauka

*** *** ***

Wai alhaji kunsha hanya, sannunku

Tafadi haka yayinda take kokarin cire masa malun malun din jikinsa

Abba yace ai hajiya tafiyar akwai Nisa, Wai ahakan ma danma ba'a Mota mukaje ba, Amma tsakanin Garin da inda muka sauka tafiyar akwai yawa, gashi hanyar tasu tana buqatar gyara

Momy juwairah tace to sannunku alhaji muje kayi wanka kahuta, kafin ya miqe yace ga wannan

Kallan hannun nasa tayi tace alhaji qwan menene wannan? Yace shine abinda muka Sha wannan baqar wahalar akansa

Yace suci shida matarsa, da iznin Allah za'a samu abinda ake so, momy ta dinga juya qwan tace ikon Allah

To Bari gobe Sai akai musu, daga mata hannu yayi yace haba hajiya, kirasu yanzu kisa masu aiki su dafa suci su tafi

Nizan shiga ciki in watsa ruwa in kwanta

Babu abinda zan musu ayanxu alhaji Sai Bayan munje nayiwa mijina hidima tukunna

Da murmushi ya kalleta, itade akoda yaushe cikin kula dashi take, Bata nuna gajiyar ta Akan hakan, Koda yaushe tana cikin kwalliya da kalamai masu dadi ga mijinta

*** *** ***

Amal gashi inji Malam nura yace nabaki, takardar hannun ta na kalla nadafe kirjina da hannun na, tace nashiga uku maisah ko takardar korata ne daga makaranta? Nashiga mezan cewa baba

Nafadi haka idonta na cikowa da qwallah

Takardar ta fizge zata Bude ta karanta, maisah ta dakatar da ita da fadin a a karki Bude a gabana idan kinje gida kin nutsu saiki karanta idan munsake haduwa saiki ban labari, Amma ki kwantar da hankalin ki, insha Allah Babu matsala

Ajiyar zuciya nasauke nace to maisah, nagode qawata ta Gari

Hararata tayi tace ni muje, baquwar haure kawai, qilama zuwa kikai ki zautar mana damalami

Ku dama yan agadaz dinnan haka kuke, da anganku shikkenan nutsuwar bawa tatafi

To yar qasa, munji, kuma babu inda zamu, kullum Ina fada miki damagaram kina kaini agadaz

Tace edin can zan kaiki, Gaba nayi nace kanki akeji

Takusa qarasawa gidansu kawai sai ganin mutum tayi agabanta, subhanallah

Haba Yaya sham, wallahi kaban tsoro

To yakike so inyi tauraruwata?

Koda yaushe bamuda ikon yin magana agida saide aboye?

Kinga Amal wallahi nagaji, sanki yana neman zautar Dani, kibani dama inturo iyayena gidanku ayi magana

Yaya sham, kasan de banda ikon yin hakan ayanxu ko? Meyasa Amal? Yafadi hakan kamar zaiyi kuka

Tace saboda yayanah yahanani sauraron kowa, sannan Yaya sham yanzu Ina tulawa bamuyi saukaba, tayaya kake tunanin zanje wa da baba wannan maganar?

Kallanta yayi da mamaki yace Amal Anya kuwa kina sona kamar yanda nake sonki? Yaya sham trust me wallahi I really love you

Amma kabani dama zuwa Bayan saukarmu, insha Allah zan gabatar dakai awajan baba, nasan cewa baba yana sona, zaiso abinda nakeso

Yauwa kokefa, to yanzu Sai yaushe? Very soon zamu hadu karka damu kaji Yaya sham din Amal

Murmushi yasaki Dan yaji dadin sunan sosai

Yace shikkenan bye bye

Dahaka suka rabu

*** *** ***

Salma banaso, please kibani fillo nah

Gwalo tayi masa tace ow nahanashi kazo ka qwace, in kacika mai karfi, kokuma duk wannan dantsan kawai na adone?

Kallanta yayi, shide yasan idan yace karfi zai sa mata to da tuni ya qwace

Fillon ta sake dauka ta wulla masa, Shima yadauka yarama, sunata nishadi abin su, ta jefo masa Shima yarama, tace ko yanzu de nasa kadan motsa bakinka, haba mutum ya zauna shiru haka

Kallanta yake da tsadaddan murmushinsa mai kashe mata gabban jiki, yace aikuwa mai ganin surutu na, sai sabuwar amaryata

Nan da nan ta dauki fillon ta jefeshi dashi tace Allah a a, baka isaba

Yana kokarin ramawa, momy ta futo da filet ahannunta

Nan da nan suka nutsu gaba dayansu

Salma ta sauka qasa cikin sauri tace momy barka da futowa

Ba yabo ba fallasa ta amsa da "yauwa"

Shima ya gaida ta,ta meqo musu filet din tace gashinan kuci

Daddy ne yakarbi filet din, ganin wainar yar kadan ce yasa shi maiqawa salma

Tome zaici meze Bata anan?

Salma tayi bissmilla tafara ci

Kallansa tayi babu alamar wasa afuskarta tace Kai karaam bazakaci bane?

Yau baiga fuskar dazaiyi shagwaba ko tambaya ba, Dan haka baiyi wata wata ba yasa hannun suka cinye qwan

Amma cikin ransa fadi yake qwai Dan millili haka saikace gidan yunwa

Kuma ace mutum bai Isa yayi maganaba?

*** *** ***

Gaskya abinda na fahimta gameda kalamansa shine, yana baki hakuri ne Akan wani laifi dayayi miki, sannan Kuma yana buqatar ku qulla qawance tsakanin ku

Tace to dama Ana qawa da namiji Yaya?

To shide ga abinda yace nan, meyasa kike cire niqab dinki Bayan kinbar gida? Cikin tsoro tace Allah yaya bancire ba

To baki cireba tayaya akai yaganki har zai turo miki da wasiqa?

Ai shikkenan kiyi yanda kikeso rayuwarki ce, niyyarki ne ki amince, kokuma akasin haka

Tashi yayi yashiga ciki, gabansa yana mugun faduwa

To Wai ita Dan Allah me Yaya Shahid yake so tayi? Itada tazo domin aqara yimata bayani Akan hausar, kuma zaiyi fishi yatafi?

Kuma yace ta amince ko karta amince

Wullar da wasiqar tayi, tabishi abaya

*** *** ***

After 3week

Salma!

Yakamata ki tashi ki hada mana break fa inaso zan fita

Juyi tayi daga cikin lallausan blanket dinsu, domin kuwa basu taba Raba wajan kwana

My dear wlh banjin karfin jikina, bazan iya tashiba, please zo

Matsowa yayi wajan ta da mamaki, kafin yayi magana ta janyo shi jikinta tana shaqar turaren daya fesa

Jikinta yaji zafi rau, da sauri yace subhanallah, wayarsa yadauka yakira family doctor dinsu, ita kuwa tana jinsa tayi luf ajikinsa

Doctor yana zuwa yaduba ta, ya tabbatar masa da cewa tana daukeda juna biyu na Tsawon sati biyu

Daddy daskarewa yayi awajan, Yama rasa da bakin dazaiyi magana

Doctor ma yalura da halin dayake ciki Dan haka yadafa kafadarsa yana murmushi yajuya yafita

Yana fita daddy yakaiwa Salma wata wawar runguma

Yasake ta yayi sujjada yagodewa Allah, yasake dawowa ya rungume ta, ita Yama Bata daria wallahi, Gaba daya ya cukwikuya babbar rigar sa

*** *** ***

Malam dama zuwa nayi in qarama godia Akan maganin daka bani, gaskya naji dadi sosai, OKASHA yana Nan yashiryu yadena shaye shaye, Babu ruwansa yanzu wlhy Abu yayi kyau sosai yanzu hakama karatu nake San turashi qasar waje

Baba hamani yace ahhh Abu yayi kyau alhaji, haka ake so ai

Shahid ne yashigo Bayan ya gaida alhaji yace baba ga mukullin shago zanje filin ball

Yace to Shahid saika dawo

Yana fita alhaji sidi yace a a Malam dama kanada yaro babba haka?

Baba hamani yace danmu biyu ne ai alhaji, Shahid ne babba Sai Amal, itada Tayi diploma, shikuma yayi NCE anan kusa damu Gumel

Alhaji sidi yace gaskya nayaba da hankalin sa sosai Malam, inaso kabani takardunsa sannan Kuma kabani dama inturashi Indonesia karatu shida Dan wajena okasha

Fara'ah ce ta bayyana afuskar baba hamani, yadinga yiwa alhaji sidi godia

Alhaji sidi yace ainine da godia Malam, okasha shi kadai na mallaka, ta Sanadin ka dakuma temakon Allah Yarona yazama cikakken mutum

Ai babu abinda zance dakai Malam Sai godia

Sannan shikuma Shahid kafada masa yazama ready, banaso su qara one week a qasar nan

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

5

Alhaji sidi bai Bata lokaci ba wajan karbar takardun shahid yatafi dasu gida wato Kanon Dabo, inda yafara cuku cukun nema musu school shida dansa

Baba hamani yana shiga gida yafadawa samiya wannan labarin, bakinta har kunne saboda tsabar murna

Amal ce ta futo daga daki Jin umma Sai hamdala take tun dazu

Tace umma me a kayi ne yau?

Nan umma tabata labari, Amma abin mamaki maimakon tayi murna kawai saita juya daki, iyayan babu Wanda ya lura da halin datake ciki, kasancewar suna cikin farin ciki

Tana shiga daki tafada kan yar madedeciyar katifarta tadinga kuka, Yaya Shahid zai tafi karatu, to dawa akeso taci gaba da rayuwa?

Kafin zuwa magrib zazzabi mai zafi yarufeta

*** *** ***

Yauwa hajia maimuna kawai kowanne kikawo dozin daidai mugansu, eh namaza dozin daya na matan ma haka, tunda bamusan me za'a Haifa ba

Abba yayi sakare yana kallanta da mamaki

Tana ajiye wayar datake tajuyo tace alhaji barka da dawowa

Wai hajiya, mezakiyi da kayan yara ne naji kina cewa akawo miki dozin dozin

A a haba alhaji, ya zakace me zamuyi da kayan yara

Ai gara mufara tarawa tun yanzu,

Abba yace wai kina nufin cikin sati biyun za'a fara yiwa siyaiya?

A a to alhaji so kake Sai an haifeshi sannan mufara siya

Dariya yasaki yace gaskya wannan jika naki zaiga gata

Tace ai alhaji kaide kawai Allah yakawo shi lafiya

Abba yace amin hajiya

Daga daki ta futo taci Riga da wando, kayan sun kama mata jikinta sosai, kasancewar batada jiki sosai Sai kayan sukai mata Das ajikin ta, tayi fakin gashin kanta dayasha gyara, tana zuwa tafada Jikin momy juwairah, cikin shagwaba tace momy Dan Allah kifada masa kinji

Hajiya tajuya tace to alhaji kaji, Wai yar lelen nawa tace adan daga mata kafa zuwa next week saita koma hutu

Abba yace hajiya yarinyar nan kina sangartata dayawa, mezatayi inta zauna agidan? Banasan sakarci ta tattara yanata yanata Takoma school jibi, already sun fara lecture, daga kanta tayi daga Jikin momy juwairah tace Allah Abba basa farawa da wuri, yace banasan Jin komai, tunma kafin daddy yasamu labari ki shirya kibi flight din dazai tashi jibi, banda yawo da qawaye babu abinda kika iya, Dan haka karna sakejin maganar cewa Wai bazaki school ba

*** *** ***

Yana dawowa daga filin ball, wanka yashiga, yaje masallaci sallah, sai Bayan an idar ne ya hadu da baba hamani, baba hamani bai Bata lokaci ba wajan fada masa yanda sukai da alhajin dayazo dazu, yace to baba Allah yasa hakane yafi alkhairi, daga haka bai qaracewa komai ba, suna shiga gida yayi cikin dakinsa, yarasa me yake masa dadi, Anya kuwa zai iya rayuwa batare da Amal ba? Yarinyar daya reni qaunarta acikin zuciyar sa tun batasan kanta ba, Rana daya kwatsam ace yaje yayi wata rayuwa batare da ita ba? Anya yayiwa zuciyar sa adalci kuwa?

Zumbur yamiqe tsaye yayi dakinta, gara yaje yaga halin datake ciki, duk da yar tsamar dasuke da ita Akan wasiqar Malam nura

Yana zuwa kofar Dakin yace in shigo? Yaji shiru yasake fada second time, still yaji shiru, Dan haka yasa kansa ciki

Yana shiga kuwa yaganta akwance, Dasauri ya qarasa gareta, yace qanwata

Dakyar ta Bude lumsassun idanunta ta kallashi, hakan datayi shiya haddasa masa shiga cikin wani Hali

Matsawa yayi ya zauna a gefe daya daga kan katifar Tata yace ki tashi zamuyi magana

Tana tashi data ganshi Sai maganar ummah ta Fado mata arai, aikuwa batayi wata wata ba ta fada jikinsa tasaki wani kasalallan kuka

Yasalam!

Abinda yafada aransa kenan, wannan yarinyar karta hauka tashi

Bayanta yake bubbugawa alamar rarrashi, tayi luf acikin kirjinsa, idanunsa a lumshe, yace kiyi shiru mana

Koso kike Nima kisani kuka? Bata iya maganaba illa girgiza Kai datayi

Yace meyasa kika shigo daki ke kadai kikabar umma afalo?

Cikin sigar shagwaba tace Yaya Wai tafiya zakai nanda sati daya? Yaya please karka tafi kabarni, dago da kanta yayi still tana kwance ajikinsa

Suka qurawa juna ido

Kenan taji maganar tafiyarsa shiyasa itama tashiga wannan halin

Ahankali yabude kyakkyawan lips dinsa, ya matso da bakinsa daidai nata, tamkar zai hade bakinsu waje daya

Cikin kasala yace bakyaso intafi?

Lumshe idonta tayi ta Bude alamar hakane

Yace to kiyi hakuri kinji qanwata, insha Allah duk inda naje zaki kasance anan dina

Yafadi haka yana yi Mata nuni da kirjinsa gefen da zuciyar sa take

Amal BURINAH akoda yaushe shine inkasan ce tare dake, infaranta miki, insaki walwala

Amal

Tace na'am Yaya

Yace kiyimin alqawarin har in dawo bazaki saurari kowaba, har yanzu ke yarinya ce, baki Kai matsayin dazakiyi soyaiya ba

Dakaina zan nema miki mijin daya dace dake kinji?

Jikinta ne yayi sanyi Jin kalaman sa, dayaji tana kula Yaya sham to inajin da saiya daketa

Yaya nayima alqawari babu Wanda zan saurara, Nima BURINAH shine in yima abinda ranka yakeso

Kinyi alqawari? Nayi ma yayanah

To muje inbaki abinci, Kisha magani

To yayanah, Sarai ta ware suka fita daga Dakin

*** *** ***

After 2 weeks

Tafiyar su Shahid ta tabbata, inda aka gama musu komai da komai shida okasha

Umma da baba da Amal ne suka rakashi har airport

Okasha yana kallansu, shiko ajikinsa, asalima Bluetooth ne akunnansa yanajin waqa

Lokacin da aka kirasu shiga jirgi Amal kuka Shahid kuka

Umma cikin ranta tanajin tsoron wannan al'amari na Shahid da Amal

Amma Allah yasa ba abinda take tunani bane

Suna shiga jirgi, Babu Bata lokaci suka Lula Indonesia, saida su Amal sukaga tashinsu sannan suma suka dau hanyar dawowa gida, suna shiga Mota ta riqe kanta da hannun ta dayake barazanar tsagewa,

Bayan sun dawo gida saida umma tayi da gaske sannan Amal tadan saki jikinta kadan, shikkenan babu Yaya Shahid, Babu meyi mata wasa, Babu me rarrashinta, Babu me tsokanar ta, sai hawaye

, Allah ya kyauta, abinda umma tace kenan taci gaba da abin gabanta, duk da itama taji ajikinta wannan Tafiyar ta Shahid

*** *** ***

Suna sauka suka hau taxi ta kaisu gidan dazasu zauna kusa yake da school, kasancewar okasha kansa awaye yake basa shan wahalar komai, darana suka sauka Dan haka suka shirya zasuje makaranta su qarasa registration daga nan kuma suje su siyo Sim card domin Kiran yan gida

Bayan sunyi wanka, okasha yashirya dawuri ya zauna yana jiran Shahid, yayi kyau cikin qananun kaya

Yana Zaman jiransa Sai gashi yafuto da yadi ajikinsa Riga da wando rigar tsawon ta har qasa, ko hula babu yace masa muje

Okasha baisan lokacin daya tuntsure da daria ba, yafara nuna shi da hannu, haba gaye, ya za'ai Kasa wannan kayan Dan Allah

Shahid dayakejin wani daci aransa saboda rabuwarsa da Amal yace okasha please tashi mu tafi Dan Allah

Okasha yace to kaga Ina zuwa, dakinsu yaje yabude jakarsa yadauko wasu arnun kaya qanana, jar Riga, baqin wando, yace gashi Kasa wannan kafin muhuta zuwa gobe muje shopping Dan Nima banzo da wasu kayaba

Shahid yace kagani babu wani kaya dazansa Malam kawai muje

Dakyar okasha yasa Shahid yasaka kayan, sannan yabashi wani agogo yasa qirar Gucci, saiga Shahid harta taje lallausar sumar kansa ta buzaye mai kama da ta yan hindi

Dasauri suka futo saboda basaso suyi latti basu tsaya ko Inaba Sai University of Indonesia

Suna shiga harabar makarantar sukaga mutane atsaitsaye wasu a zaune kowa yana harkar gabansa

Abinka da basabanba nan Shahid yadaga Kai yana ta kallan yanayin makarantar

Garam yaji yayi Karo da mutum har hakan yayi sanadiyar faduwar wayarta

Cikin sauri yace yasalam ya tsugunna yana dauko mata wayar

Jin hausa a bakinsa yasa cikin masifa da bacin rai tace Malam wannan wanne irin shirme ne?

Dagowa yayi ahankali yana qare mata kallo daga sama har qasa dama wannan yarinyar bahaushiya ce?

Aishi jiyake arniya ce, saboda dasu shigarta take kama

Wayarta yabata yace kiyi hakuri Dan Allah ban lura bane

Wayar takarba takasa cewa komai, yace kiyi hakuri

Yaji tasake yin shiru, akaro na uku yace kiyi hakuri

Kawai yajuya yatafi

Qawarta ce ta girgiza ta tace SHAHIDA me kike tunani ne?

Jamcy wallahi wannan gayen yatafi da Imani na

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

6

Shahida me kike fada haka? daga ganin mutum? Kobaki ganshi bane? Babu alamar wayewa awajansa

Kinga jamcy idan bazaki soshiba, kada ki qara kusheshi agabana, tana fadar haka tayi gaba

*** *** ***

Hello ummatah, na'am Shahid din umma

Yaya kukaje?

Kafin tabashi amsa Amal ta fizge wayar tayi daki cikin murna da zumudi tace yayanaaaah!

Baisan lokacin daya lumshe idonsa ba, Amal din Yayanta

Yaya yakaga Garin, Yaya tunda katafi nake kuka wallahi har kaina saida yayi ciwo

Haba yammatan Yaya karkisa yayanki yakasa yafewa kansa a dalilin rashin lafiyarki, ki kwantar da hankalin ki babyn Yaya, shekara biyu zanyi in dawo kinji

Allah yaya da gaske, serious Amal, ai kinsan an jonamin da result dina ne na n.c.e, Dan haka Shahid bazai dadeba zai dawo wajan...

Kafin yaqarasa tace wayyo yayanah, Allah yakawo ka lafiya, harna fara qirgawa azuciyata

Karki manta de da alqawarin dakika daukarwa yayanki

Yaya karka damu, bari nakaiwa umma wayar muahh tasakar masa kiss tawayar

Mutuwar kwance ce kawai Shahid baiyiba

Bayan sun gaisa da umma da baba ne yayi musu sallama

*** *** ***

After 6 months

Karatun su Shahid yayi Nisa sosai, sun hadu da wani dan nigeria guda maisuna nazir, suna kiransa da nazy

Sosai suke mu'amularsu, Babu ruwansu da kowa, su ukun nan de Koda yaushe haka zaka gansu, haduwa Shahid da nazy da okasha shine dalilin gogewarsa

Yaqara wani kyau na tashin hankali, har yakasance duk inda yashiga saiya tafi da imanin yanmmata, sau dayawan lokaci haka kawai yana zaune zakaga yanmata sunzo sunce masa su nasan yin pictures dashi

Haka zai tsaya suyi

Sosai Shahid yagoge yaqara wayewa

Dayayi pictures zai watsa shi a media

Jama'ah kuwa kamar babu gobe, yanda suke tururuwar yimasa magana, musanman yanmata

Abangaren shahida kuwa tun tana daukar al'amarin da wasa, sai gashi abin yafara damun ta, har hakan yana nema yashafi karatun ta, inda ta yanke wa kanta hukuncin zata dinga bibiyarsa hartasan shi din waye, daga baya kuma ta labarta masa abinda take ji game dashi

*** *** ***

Tana zaune Akan gado, Shima yana kwance yadora kansa Akan cinyarta, yana shafa cikinta, sumar kansa take shafawa ahankali, my dear baka gajiya da shafa cikin nan, kaide Koda yaushe ka zauna Kanata aikin shafawa

Salma kenan, bakisan yanda na matsu Inga dana danaki bane, salma Ina fatan Inga munci gaba da rayuwa nida ke har abada tare da abinda zamu Haifa

Zuba masa ido tayi, yanda yake magana cikin, ashe akwai ranar dazata ganta daddy yana zuba mata kalamai haka

Batasan lokacin data qara rungume Shiba

Tace su hajia suna farin ciki da zuwan wannan babyn, kowama haka, nide fatana inhaifeshi lafiya,

Karki damu salma, insha Allah lafiya kalau zaki Haifa mana babyn mu

Tace karaam kayimin alqawarin zakaci gaba da sona har abada, idan namutu zaka riqe mana babynmu dakyau

Yayi mamakin kalamanta, yace salma karki sake irin wannan maganar please

Tace Toshiknn my dear nadena, haka taci gaba da shafa kansa har bacci ya dauke shi, ido ta zuba masa, itade tana kaunar mijinta, tana fata su kasance tare har qarshan rayuwar su

Cikinta ta shafa Wanda take kusa da haifarsa, tace Allah yakawo ka lafiya baby na,da Murmushi sosai asaman Fuskarta

*** *** ***

Samia bani shayi,

Daukar butar shayin tayi, tace Malam yaude Naga alama shayin nan yanayi ma dadi

Aidole Samia

Bakiga yau rawaninmu ba irin na kullum bane?

To saboda murnar saukar yata Amal ne

Ki duba fa kiga duk wannan kyautukan natane, haba Samia wannan ai abin alfahri ne, umma tace gaskiya ne, danma yayanta baya nan, aida saiyafi kowa murna

Baba yace gaskiyar ki Samia, zaiyi murna

Acan daki kuwa

Amal ce da Qawarta maisah

Sunata firar yanda saukar su ta kasance

Maisah tace Wai Dan Allah meyasa bazaki bawa Malam nura dama yafuto ba?

A a maisah, baimin ba, koba haka Bama ni yayanah yahanani kula kowa har Sai yadawo gida

Zaimin miji da kansa

Nikuwa Amal in tambayeki, Dan Allah yaya kuke da Yaya Shahid? Kamarya maisah, wannan wacce irin tambaya ce?

Uwarmu daya ubanmu daya

Kuma kinsan de yanada ikon yin komai akaina

Maisah ta girgiza Kai alamar gamsuwa tace shikkenan, kice da Yaya sham din za'a yi, nace qwarai kuwa Amal ta shamsuddin ce

*** *** **

After 3 months

3:00 am daidai

Taji bayanta yasara, mata, dama tunda Watan haihuwar ta yakama takejin gabanta yana faduwa

Ahankali tasauko daga kan gadon saboda bataso ta Tadashi daga bacci, tana saukowa qasa, marar ta tayi wata iriyar murdawa, da karfi tasaki ihun wahala

Hakan ne ya farkar dashi daga baccin dayake

Dasauri yasauko daga gadon, yanufeta, salma sannu

Meyake damunki?

Inane yake miki ciwo?

Daddy bayana, marata

Gaba daya ya diririce yarasa mai zaiyi, jallabiyarsa yadauka fara qal da ita yasaka, yadauketa, baijira komai ba yana sakata amota yafigi motar Sai hospital

Kafin suje hospital din, Tafita ahayyacinta, suna Zuwa aka karbeta Sai labour room, anan yasamu damar Kiran iyayansa yasanar dasu

Afijajan momy juwairah tazo itada Abba

Daddy banda Santiri babu abinda yake yi, idanunsa sun kada sunyi jajir

Yarasa me yake masa dadi

Suna nan a tsaye har akayi Kiran sallar farko

Gab da asuba, likitan yafuto, atare suka miqe suna tambayrsa doctor tasauka lafiya?

Abba yace me aka samu doctor?

Shiru yayi yana kallansu, momy tace doctor Yaya Dai, kayi magana mana

Hajia saide kuyi hakuri, munyi iya kokarin mu domin muga mun ceto rayuwar ta, but hakan bai iyuba

Allah yayi Mata rasuwa, tare da abinda yake cikinta

Abba yace innalillahi wa inna ilaihir raju'un

Yayinda momy juwairah tayi jagwab ta zauna aqasa

Qarar faduwa sukaji, suna dubawa sukaga daddy yayanke jiki yafadi qasa asume

(please Dan Allah fans kuyi hakuri, nayi tafiya ne wlhy, shiyasa bansamu dama nayi posting da wuri ba, Amma insha Allah zaku dinga jina da wuri kamar Koda yaushe)

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

7

Yana zaune a harabar school din, littafi ne ahannunsa yana dubawa

Hankalinsa kacokam yana kan karatunsa

Daga nesa kadan dashi nazy ne okasha, suna fira kadan kadan da lemuka agefensu

Tun daga nesa ta qwara masa ido tana kallansa, tarasa Yaya zatayi da soyaiyar wannan gayen

Ahankali take tafiya tayi kyau sosai cikin Riga da wando pink color tayi rolling da farin mayafi

Sallama tayi masa tare da zama, dago idanunsa yayi yazuba mata Su, a'ina yasan wannan face dinne?

Oh wadda yayarwa da waya, yafadi haka aransa

Amsa mata sallamar yayi, ya maida hankalin sa Akan littafi

Shiru ne yabiyo baya,shi yana karatunsa ita kuwa bil haqqi ta zuba masa ido tana kallan sa

Gaye duba can

Okasha yakai kallansa inda nazy yake nuna masa

Yace to Anya lafiya kuwa irin wannan kallo datake masa?

Daria nazy yasa yace kuma da alama mutumin baima saniba

Okasha yace inaga ta harbu fa, taga Dan buzaye ta rikice

Rufe littafin nasa yayi yatashi yabar wajan ko kallan ta baiyi ba

Yana tashi Wayarta tadau qara

Tana dagawa tace hello momy nah

Kafin ta amsa taci gaba da cewa momy wallahi Naga wani baki ganshi ba mai kyau inasan sa sosai momy

Maganar da momy tafada mata ne yasa ta sakin wayar hannun ta qasa nan take ta watse

*** *** ***

Ahankali yabude Zara zaran gashin idonsa, kallansa yakai ga Dakin dayake kwance, kansa ne yayi muguwar sarawa, momy dake gefensa cikin dashashiyar murya saboda tsabar kuka tace sannu daddy

Salma!

Salma!!

Why salma? Meyasa zaki tafi ki barni salma

Hawaye ne yake zarya a idonsa, abinda iyayensa basu taba gani yayi ba da girmansa de, kayi hakuri katashi muje kayi mata addu'ah za'a kaita makwancin ta

Tsam yatashi baice musu komai ba kawai tafiya yake idanunsa sun kada sunyi jajir

Direct gidansa suka wuce, yan 'uwan ta sun zo ancika gidan danqam, kowa Sai koke koke yake, har Dakin da gawar take Abba yakaishi

Tsugunna wa yayi daidai kanta, ahankali ya yaye Fuskarta, tamkar zai kirata ta amsa, Babu alamar bacin rai afuskar, asalima tamkar murmushi take, hawaye ne suka tsiyayo daga idanunsa

"karaam kayimin alqawarin zakaci gaba da sona har abada, idan namutu zaka riqe mana babynmu dakyau "

Maganganun ta ne suka Fado masa arai, ashe tafiya zakiyi kibarni salma

Yafadi haka abaiyane, salma, meyasa salma, meyasa baki zaunaba ni natafi, salma kece mai sona mai kaunata, kece kadai zaki iya zama Dani da halaiyata

Salma yau gashi babu ke babu babynmu

Gashin kansa ya hargitsa

Idanunsa jajir, Abba dayake tsaye shi kansa hawaye yake sharewa

Mahaifinta ne yayi karfin halin matsowa yaja hannun Abba, wasu daga cikin danginta suka matso zasu dauki makarar, Abba ne yasunkuya yadafa kafadar daddy

Alamar rarrashi, domin kuwa babu bakin magana

Suka dauki makarar domin amsa Kiran mahalicci

Riqe makarar yayi, yana kuka haiqam tamkar ba gwarzon namiji jarumi karaam ba

Ganin baya hayyacinsa ne yasa Abba yahadashi da maqocinsa, kamashi yayi, suka tafi, Amma daddy banda kuka yana Kiran salma babu abinda yake yi

Direct asbiti aka mayar dashi, doctor bai Bata lokaci ba wajan yimasa allurar bacci

*** *** ***

Suna zaune adakin da aka kwantar dashi, momy da Abba da anty mufy, da junior, sai shahida data biyo jirgi tadawo gida tun washe Garin rasuwar

Tunda yafarka yayi shiru, baya um bare um um, baisan awanni nawa yadaukaba a kwance, idanunsa sun kumbura

Ashe salma tafiya zatayi ta barshi, shiyasa take masa maganar mutuwa, rayuwa kenan

Idanunsa ya maida ya lumshe, Abba ne yayi karfin halin cewa yakamata katashi kayi sallah, Kasa wani Abu acikin ka, Kai musulmi ne, dole ka yarda da qaddara mai

kyau ko marar kyau, junior ne ya matsa kusa dashi, yace uncle yanzu kuma yaushe anty salma zata dawo ta haifamin qanina

Anty mufy batasan lokaci data dokeshi ba

Yaron yacika surutu dayawa, karaam ne yajanyoshi, yace yi shiru, zata dawo ka ka kajiii..... Yaqarasa maganar yana hawaye

Momy ta goge qwallar idonta tace tashi kayi sallah daddy, shahida hada masa tea

Ahankali yatashi yashiga toilet

Saida suka zo tafiya gida ne yaji Abba yana magana da likitan Akan cewa yau akayi mata sadakar uku data bakwai gaba daya

Hakuri yaqara basu, sannan sukai sallama dashi sukayi gida

Gidansa suka fara shiga zai debo kayansa, fir yaqi shiga, da Abba ya matsa ma kawai saiya sa kuka

Shi wallahi bazai shiga ba

Dole Sai anty mufy ce ta Dabo masa kayan

Suka juya gida

Tunda suka koma gida, yadena magana dakowa, Koda yaushe yana cikin dakinsa yana aikin tunani

Bashida aiki Sai kallan pictures dinsa dana salma acikin wayarsa

Koda yaushe cikin tunani yake, har hakan yafara damun iyayensa, suna ganima kamar ba'a hayyacinsa yakeba, idan cin abinci akazo saide yayi shiru ya zubawa abinci ido, sai iyayen sunyi masa magana sannan zaisha Dan shayi, yarame gaba daya ya lalace, Koda yaushe cikin rashin lafiya yake, kullum suna zarya a asbiti Amma Babu wani cigaba

*** *** ***

One month later

Office din dasuke meeting din aqawace yake da kujeru na alfarma, duk wanda kagani awajan babban Dan siyasa ne, wakilin jam'iyar aka bawa dama yabude taro da addu'ah, Bayan komai yalafa, yan majalissun dasauran jiga jigan jam'iyar suka fara bayani Akan abinda yakamata ace sunyi

Daya daga ciki ne yafara fadin, ni aaganina Yaron zai iya, sannan mahaifinsa qwararran Dan siyasa ne, dole zai samu gogewa ta wajan sa, Awannan zamanin fa wannan jihar tana buqatar matasa su shigo ciki suma ayi dasu, Dan haka ni de nagoya Bayan hakan Dari bisa Dari, daya Bayan daya jama'ar wajan kowa yayi mubaya'ah, Abdallah karaam ne yatashi yayi godia Sannan yaqara dacewa insha Allah Awannan jam'iyar tasu yanda suka yanke wannan hukunci, zai tsaya da kafafunsa wajan ganin anyi komai cikin kwanciyar hankali

Sannan Kuma cikin nasara, dahaka taron yatashi

*** *** ***

Murmushi ne kwance asaman Fuskarta tace gaskya alhaji hakan yayi, naji dadi sosai, kuma wannan yana nuna sunyima Kara ne shiyasa suke so wani naka yashigo cikin harkar Shima ayi dashi

Hakane, ai hajiya yau ansha fafatawa awajan meeting dinnan to daga baya de kowa yabada goyon baya

Tace hakane Allah yayi jagora yasa adace

Amin hajiya, ina wannan yarinyar ne? Tana ciki tana shirya wa alhaji, kasan gobe takesan komawa school, yace kirata kice taje takiramin daddy

Kira ta qwalawa shahida tana futo tace jeki kira yayanki

Bayan tatafi ne, yace hajiya inaga gobe zamuyi tafiyar nan nida daddy tace to alhaji Allah yakaiku lafiya

Zaune yake Akan danqareren gadon dakinsa, computer ce agabansa qirar Apple me Launin fari

Wando ne ajikinsa three quarter milk color, sai Riga marar hannu, ga green tea nan agabansa yana shan ahankali, fuskar nan atamke, Babu alamar rahma

Ahankali tatura kofar Dakin tashiga tare da sallama, har qasa ta tsugunna tace Yaya daddy Abba yana kiranka

Alama yayi Mata da kansa, bai qara kallanta ba, ta tashi ta futo tare da rufe masa kofar

Futowa yayi yaje falon har gaban iyayansa ya zauna aqasa yace Abba gani

Daddy dama magana nakeso muyi dakai, zuwa wannan lokacin yakamata ace kayi hakuri kamanta da komai kadawo kamar da, daddy BURINAH a rayuwa bai wuce ace naganka kadawo da walwalarka ba, kayi hakuri salma tariga da tatafi, addu'armu take buqata ayanxu

Kaikuma saide ka rungumi sabuwar qaddarar datake shirin shigo Maka ayanxu, Dasauri yadago da kansa ya kalli mahaifinsa

Abba yace qwarai kuwa domin kuwa munyi meeting dazu Kuma wannan meeting din anyi shine saboda Kai, mun tashi Akan zaka futo takarar gwamnan wannan jihar insha Allah

Amma Abba salma.... Dakata karaam, Dan Allah banasan Jin komai daga gareka

Sannan magana ta biyu ka shirya gobe da wuri tafiya ta kamamu zuwa jihar jigawa

Tashi kabani waje

Idanunsa jajir yatashi yayi dakinsa, yana zuwa yafara wulli da fululluka Dakin tamkar sune suke da laifi

*** *** ***

Karfe goma na safe a jihar jigawa tayi musu, ko government house basujeba, kawai waya mahaifinsa yayi aka turo musu da Mota guda biyu suka dau hanyar qauyan maigatari

Tunda suka dau hanya babu abinda yake cewa, saide idan yagaji da kallan hanyar ne zai dau wayarsa yayi karatun alqur'ani, daga karshe ma ajiye wayar yayi ya zubawa sarautar Allah ido

Tafiyar awa hudu ce takawo su Garin, daddy banda haushi babu abinda yakeji aransa, yarasa me Abba yake nufi dashi

Iso yasa ayi musu wajan Malam hamani, Babu Bata lokaci yace su shigo

Su kadai suka shiga falon ko'ina kalau dashi fes fes, security kuwa wasu sun tsare motocin wasu Kuma sun tsaya abakin kofa

Baba hamani yana ganinsu yagane Abba, nan da nan yamiqawa Abba hannu suka gaisa

,daddy ne yaqura masa ido, daka ganshi kaga cikakken buzu, saboda rawanin dayayi akansa na buzaye, fuskarsa babu yabo babu fallasa ya tsugunna har qasa ya gaidashi

Sosai baba hamani yaji dadin hakan

Bayan sun zauna ne yace alhaji bari akawo muku ruwa

Yana shiga gida yace wa umma Samia, takawo musu ruwa

Ruwan pure water ta dauko masu Dan karan sanyi, tazuba aflate mai kyau

Tadoshi Dakin da Amal take tace tashi kikaiwa baban ki yayi baqi

Babu Bata lokaci tasaka zumbulelen hijabinta tadaura niqab dinta tadau ruwan tatafi

Cikin zazzaqar muryar ta tayi sallama adakin, kansa asunkuye yake bai dagoba bare yaga mamallakiyar wannan zazzaqar muryar

Saida tace Ina wuninku sannan yakai dubansa gareta, Abba ne ya amsa, shikuwa gogan idanu yazuba mata

Ikon Allah ga murya har murya Amma Kuma fuska a nakashe, ita kuma Tata kaddarar kenan, inajin matsalar a idonta take kokuma abakinta

Shi kadai yake zancan zucinsa

Tana basu ruwan tajuya tayi cikin gida

Abba ne ya karantawa baba hamani matsalar daddy, Babu Bata lokaci baba hamani yatashi dakansa yahada shayi, yazuba wani Garin magani aciki

Yamiqawa daddy yace gashi kasha

Kwarjini tsohon yayi masa Dan haka babu musu yakarba yashanye shayin duka

Baba hamani yadubi Abba yace alhaji karka damu insha Allah za'a samu waraka

Abba yace mungode Malam, Jim yayi yana wani tunani aransa Dan haka yadubi daddy yace jeka Mota kajirani, Babu musu yatashi yatafi

Abba yadubi baba hamani yace wato Malam wata buqata ce Dani danake nema awajanka babba

Baba hamani yace alhaji ku fadi buqatunku

Wato Malam wannan Yaron shine da awajena Nabiyu, kwanaki matarsa Allah yayi Mata cikawa a dalilin haihuwa, wanda in baka manta ba anan mu kazo nakarbi magani awajanka

Baba hamani yadauka girgiza kansa alamar gamsuwa

Abba yaci gaba da cewa to a halin yanzu an tsaidashi takarar gwamnan jihar damuke, to bashida aure babu wani mutum nagari dazai zabi shugaba marar iyali, da dattako

Shiyasa nakeso idan babu damuwa kuma baka yiwa yar wajanka Amal miji ba inaso kabawa dana aurenta

Baba hamani yace Allah yaji qanta da rahma, alhaji na tausaya wa danku mutuqa

Kuma Amal banyi mata miji ba

Dan haka nabashi ita duniya da lahira

(Allah yaji qanki salma, wallah karaam yasani qwallah lokacin typing din nan😭😭😭)

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

8

Murmushi ne abaiyane asaman fuskarsa, yamiqawa baba hamani hannu suka sake gaisawa

Yace nagode Malam nagode sosai

Insha Allah idan naje gida, magabatansa zasu zo ayi komai agama alokacin banasan kada aja lokacin

Baba hamani yace babu komai alhaji ai temako ne

Kudi ya ajiye masa dami guda, sannan yatashi ya fita

Yana shiga motar ya kalli gefensa daddy ne a zaune ya lumshe idonsa

Murmushi yasaki cikin ransa yace wannan halin de yakusa qarewa da iznin Allah

*** *** ***

Samia kinji abinda na yanke, Amma Malam kasan de halin yaran zamani Shiba Santa yakeba, itama haka, sannan Malam yaran nan bataba haduwa sukai sukaga junaba

Hakane Samia, Amma abinda zaki duba Samia ceto mukayi, shi wannan Yaron abin atausayawa ne, matarsa ta rasu Samia, mutumin daya saba da iyali ace yau babu su dole zai shiga damuwa, sannan Yaron yakusa shekara bakwai yanasan haihuwa Amma Kuma Allah Bai bashi ba

, tunda Allah ya hore mana abinda zamu iya temakon sa ai abin yazo da sauqi, ita kuma Amal mune muke da ikon zaba mata miji ba ita ba

Abinda bazan dauka ba daya ne Samia, wulakanta Amal, muddin akai auren nan tacemin yana mata ba dadi takalmina zansa inje har gida inci ubansa nasako yata agaba mutaho

Umma tayi shiru, tasan Sarai zai aikata, fatanta daya Allah yasa abinda take tunani bashi bane tsakaninta da Shahid

Tace to Malam, yanzu kasanar wa yayanta ne?

A a Samia ban fada masaba, zande sanar dashi idan ansa lokacin bikin insha Allah

Umma tace to Malam Allah yakaimu

*** *** ***

Amma alhaji wannan wacce irin magana ce ka nema masa aure batare daka sanar dako daya daga cikinmu ba

Kuma ma yarinyar yar Malam, haba alhaji, yanzu fisabilillahi azo ace za'a yiwa daddy aure ma atambayemu yar waye kawai saimu Bude baki muce yar Malam ce

Haba ai da kunya, kamarsa yarasa wa zai aura Sai wata yar Malam

Wato hajia Naga alama kina yawan mantawa da bayanmu, Toni muddin Naga talaka Naga me kudi, to Abu daya nake daukar su

Da talaka Dame kudi duk Allah ne yayisu, Kai kanajina ko?

Daddy da idonsa yakada yayi jajir yadago yazubawa mahaifin nasa ido, yace nariga nayi magana da mahaifin yarinyar

Sai ince ma ai kamar kaganta ko? Yarinyar data kawo mana ruwa mukasha jiya?

Kansa ya girgiza alamar eh

Yaci gaba da cewa to alhmdlh, anbaka ita, Dan haka kaje kafara shiri, kafin afara shirin Zabe za'a daura auren, da fatan babu matsala?

Matsala? Yanzu shi Abba yake tambaya matsala? Arasa wa za'a aura masa Sai wata yarinya da in yayi hasashe ma yasan ya haifeta, yarinyar ma nakasashshiya, inba nakasa ba meyasa zata dinga boye Fuskarta, Abba bazai ganeba Amma irin wannan yaran munafukai ne wallahi

Kayi shiru, kokuma kaima maganganun mahaifiyarka ne yashiga kunnanka yayi ma huduba?

A a Abba nagode, Allah yasaka da alkhairi, banda BURIN daya wuce inbi umarnin ku

To dade yafima, zaka iya tashi katafi

Tashi yayi yatafi, jikinsa sanyi kalau

Yana zuwa dakinsa yafada kan gadonsa gamida rufe idonsa

Allah Sarki salma, meyasa kika tafi, yau gashi za'a aura min yarinyar da ahaifema mun haifeta

Bade auren bane, to suyi, zata gaji da zama tatafi gidansu, toda yaushe ma Salman tatafi dahar za'a mata kishiya

*** *** ***

Hi

Dago Kai yayi ya kalleta, tace magana nakeso muyi idan bazaka damuba

Okasha yace ok inajinki, wancan abokin naku

Tayi masa nuni da Shahid dayake nesa dasu, yace inajinki

Wallahi Sansa nake, meze Hana kahadani dashi, ok Tome kikeso daga gareni?

Number sa, yace ok, gashi, tana rubutawa ta tashi tace nagode sosai dan'uwa

Yace no karki damu

Next day

Da sassafe ta kirashi, kamar wasa yaji muryar mace, tace bawan Allah magana nakeso muyi, yace inajinki

Wallahi tun lokacin dana fara ganinka, naji ka kwanta min, idan bazaka damuba zanso mu qulla soyaiya atsakanin mu

Um duniya kenan, Lalle duniya tazo karshe, yanzu matane suke neman maza

Yace cigaba inajinki

Tace Dan Allah ka temaka kasoni, wallahi ban taba son wani da namiji ba kamar ka, idan bazaka damuba zanso muhadu gobe kaganni

Yace babu damuwa Allah yakaimu, daga haka yakashe wayarsa

Nikam shahida kina bani mamaki wallahi, kamar ki kina bibiyar wannan gayen

Jamcy bazaki gane bane wallahi Ina Sansa da gaske

Kafada jamcy ta daga alamar ko oho

*** *** ***

To Malam kaji abinda yake tafe damu, Malam yace eh gaskya ne munyi magana dashi, kuma yakirani awaya yafadamin Kuna tafe

Sake sabuwar gaisuwa sukayi, yatashi yafara gabatar musu da abinci da Sha, sai Bayan komai ya lafa ne, suka gabatar masa da kudin gaisuwa dana Saka Rana, Babu Bata lokaci aka sa sati biyu masu zuwa

Sai Bayan sun tafi ne, yadauki goro da komai aka rarrabawa maqota da abokan zama lafiya, suna zaune da kudin ahannunsa yana yiwa umma maganar abinda yakamata aqara siyowa kafin lokacin

Bayan yagama komai ne yabawa umma umarnin takira masa Amal

Tana zuwa baba hamani yace Amal

Na'am baba

Amal

Na'am baba

Sau nawa nakiraki? Sau biyu baba

To magana zamuyi dake ta fahimta

Akwai baki da sukazo wajena kwanaki, har kika kawo musu ruwa, kin tuna?

Eh baba

To wannan Yaron da sukazo dashi an nema masa auren ki, kuma nabasu, kinga wannan kudin?

Gabanta ne yake muguwar faduwa tadago ta kalli kudin yace to kudin sa ranar auren ki ne nanda sati biyu

Gabanta ya bada Damm!

Dasauri tace Amma baba ni wallahi Bana sansa

Ni Yaya sham nakeso

Kuma baba ni ko ba hakaba Yaya Shahid yahanani kula kowa yace saiya dawo

Waye sham?

Tambayar da baba hamani yayi Mata kenan, Dan shide a iya saninsa Bata kula kowa, tunda baiyi Mata wannan tarbiya ba

Tun farkoma da yasan akwai Yaron dayake hurewa yarsa kunne daga gefe, toda haduwarsu bazatai kyau ba

Zuba mata ido yayi, yace nace miki wayene sham??

Please kuyi hakuri da wannan

Mrs Usman ce□BURINAH □

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

9

Ba tambayrki akeba? Inji umma da mamaki yakashe ta a zaune

Cikin in Ina tace baba shi.. Shin.. Shine Wanda nakeso ni

Cikin tsawa wadda ita kanta Samia saida tayi mamaki saboda tasan yanda yakeson Amal

Yace karna sake Jin wannan maganar daga bakinki, nide nasan ban baki damar kula kowa ba, kuma ko waye wannan Yaron ki fada masa zanzo in sameshi

Tunda shine yake hure miki kunne

Nariga nagama magana, yaro de nabashi, Rana kuma ansa, kiyi abinda zaki iya, tashi kibani waje marar kunya kawai

Da gudu tayi daki tana kuka, nashiga uku na

Ni wallahi banasan kowa, arasa wanne irin aure za'a min saina dole, ni wallahi banasan sa, yawani zo yaqame awaje daya saikace gunki

Wallahi Bana sansa, hijabin ta take nema zata tafi gidansu maisah

Acan wajan su umma kuwa, Malam ne ya kalli umma yace Samia kinji wata sabuwa kuma ko?

Samia da Allah zai hadani da wannan Yaron datake magana akansa toda haduwarmu bazatai kyau ba Samia

Toni Wai yaushe ma Amal din har tasan kanta dazata fara kula wani bamu saniba

Amma may be yayanta ai shi yasani, tunda tare suke abinsu

Wayarsa yadauko daga aljihun sa, Babu Bata lokaci yadannawa Shahid kira

Bayan sun gaisa baba hamani yace dama inaso zan tambayeki ne, Shahid yace to baba inaji, Wai kasan yarinyar nan tana sauraran wani sham?

Shahid yace wacce yarinya? Domin kuwa shide yasan cewa Amal bai Santa da kowa ba

Baba yace wakuwa nake nufi banda Amal

Yace gaskya baba bansanshiba, itace tafadama hakan da Bakinta?

Yace qwarai kuwa yanzu nan muka zaunar da ita nace ga yaro nan nayi Mata miji harma mun tsaida ranar auren nanda sati biyu shine takemin wani zancen banza

Gabansa ne yafadi Wai wacce Amal din? Me baba yake nufi?

Shahid yace baba Wai Amal Amal de?

Baba yace ita mana to menene?

Kansa yadafe da hannun sa daya dayake barazanar rabewa gida biyu, idanunsa suka kada sukai jajir

Yace Amma baba Ina Santa

Wallahi Ina kaunar Amal baba

Kai Shahid me kake fada haka? Wacce irin magana ce wannan?

Baba wallahi nabari ne in dawo in sanar daku komai Amma baba Ina kaunar Amal tun batada wayo baba

Baba Dan Allah Kar ayi auren nan

Baba hamani kashe waya yayi batare dayace komai ba, ya rafka uban tagumi

Umma tace meyafaru Malam

Baba yace Samia mun shiga uku

Karaf akunnan Amal datake kuka zata tafi gidansu rumaisa, innalillahi meyafaru baba yake maganar shiga uku?

Kasa kunne tayi domin tajiyo karshan maganar

Baba yaci gaba da cewa ashe Yaron nan yadade yana San yarinyar nan Amma yaqi fada mana, Wai jira yake saiya dawo daga makaranta yasanar damu

Umma tace Wai Shahid?

Aini Malam nadade da gane take taken sa, kawai de shiru nayi Inga ko shaquwarsu Tasa hakan

Nashiga uku Samia, idan nahana Shahid auren Amal banyiwa IBRAHIMA adalci ba

Ibrahima ahannu na yadanqamin amanar Shahid Samia

Wannan wacce irin masifa ce ne?

Jiri ne yadebi Amal, batasan ya akai ba Sai ganinta tayi aqasa jagwab ta zauna

Yaya Shahid

Tayaya?

Tayaya za'ai ace akwai aure atsakanin su

Yaya Shahid fa

Inaaaa bazai iyuba, Dasauri ta tashi tun kafin iyayen su ganta tayi waje, Bata zarce ko Inaba Sai gidansu maisah

*** *** ***

Da hannu biyu yadafe kansa dayake masa mugun ciwo, innalillahi wa inna ilaihir raju'un

Why Amal?

taku yaji akansa, yana dago Kai yayi tozali da ita, dama ita yake jira, saboda sunyi waya tace tanaso su hadu dashi awajan domin yaganta

Kamar kullum de Riga da wando ne ajikinta

Tayi bala'in kyau

Ido ta zuba masa takasa janye idanunta akansa, meyasa me shi idonshi yayi jajir haka?

Zama tayi akusa dashi

Shide yakafeta da ido, yana kallan ta, ransa amutuqar bace, da bayanin da baba hamani yayi masa

Zama tayi dab dashi

Tace barka da hutawa

Ataqaice yace yawwa barka

Dafatan ka ganeni nice mukai waya jiya

Dan Allah inaso kafadamin sunan ka

Still agajarce yace Mata "shahid"

Fara'ah ce ta wanzu afuskar ta, ashe ma sunansu daya

Cikin murmushi tace ashe ma sunanmu daya

Ni sunana shahida

Dafatan ka amince da soyaiya ta

Wallahi tun ranar farko dana fara ganinka naji ka kwanta min

Wallahi Shahid idan bansameka ba ko zan iya....

Dakata Dan Allah baiwar Allah

Kawai shikkenan daga ganina kin zauna Sai zubamin surutu kike

Dan Allah ki kalleki

Da ido tabi jikinta da kallo tanaso tagano aibun daya gani agareta

Kinga ni banda ra'ayin aure mace haka, ban tsane Kiba, kawai Bana ra'ayin ki ne, bakiminba

Hannayensa yahada waje biyu

Yace Dan Allah naroqeki kifita daga rayuwa ta

Yana gama fadar haka, yajuya yabarta awajan, me shahida zatai banda kuka

Wallahi idan Bata sameshi ba mutuwa zatai

*** *** ***

Maisah nashiga uku na, auren dole baba zaimin

Bangane ba, mekike nufi ne Amal?

Cikin kuka tace wallahi da gaske nake maisah, nanda sati biyu za'a daura min aure

To dawa?

Waida wani, nifa sau daya nataba ganinsa, kawai shine baba ya karbi kayan saka ranar su

Ashe Yaya Shahid sona yake maisah

Ashe ba cikinmu daya ba

Ta qarasa maganar cikin kuka

Yaya Shahid de Amal, Yaya akai kika sani?

Wallahi da kunne na naji su baba suna maganar

Kuma ni wallahi babu Wanda nakeso inba Yaya sham ba

Amma Kuma Da'a auramin wannan mutumin gara sau dubu in auri Yaya Shahid dina

Ajiyar zuciya maisah tasaki, tace Amal, shiyasafa kwanaki nake tambayrki cewa Anya kuwa Yaya Shahid iyayen ku daya?

Kikacemin eh

Amal abinda zan fada Miki shine kiyiwa iyayenki biyaiya, bakida kamarsu aduniyar nan

Amal baba yayi miki komai, ke kanki kinsan cewa yana sanki, bayasan bacin ranki, meyasa ba zakiyi masa biyaiya ba?

Amal baba bazai ba dake inda za'a cutar dakeba, kiyi hakuri

Rungume rumaisa tayi tana ci gaba da kuka, maisah tana bubbuga bayanta alamar rarrashi

*** *** ***

Da daddare tasha maganin ciwon Kai, ta kwanta, idonta biyu, tayi shiru tana tunanin rayuwar ta yanda take neman juyewa

Umma ce tashigo ta miqo mata waya, tace gashi zakiyi magana da yayanki

Tana Bata wayar tajuya ta fita

Da sallama ta daga wayar, Yayanah

Kawai saita da kuka, Shahid da zuciyarsa ta kusa karyewa yace menene kuma abin kuka?

Ko Dan baki samu sham dinki ba?

Nifa Yaya bahak.....

A a Amal, bakiji magana ta ba, inda kinji bazakimin hakaba, cikin kuka tace Dan Allah yayanah kayafemin

Kamar wasa taji, alamar yana kuka

Dasauri tace Yaya kuka kake?

Cikin shashshekar kuka yace Amal Yaya zanyi da soyaiyarki?

Innalillahi karde zancan su umma da gasken ne

Cikin kuka nace nashiga uku yaya

Yace Amal, Babu yanda zanyi, dole in hakura dake

Tunda baba yariga yayanke hukunci

baba yayimin komai Amal, BURINAH inso abinda yake so Koda kuwa ba shine ra'ayina ba

Yaya kayafemin kula Yaya sham danayi

Insha Allah bazan sakeba Yaya nayi laifi

Amma Yaya wallahi banasan wannan mutumin

Banasan sa Yaya

Please Yaya kadawo baba yayi mana aure

Hawayen idonsa yagoge yace bazai iyuba Amal, bazai iyuba, karmu maida mahaifinmu mutumin banza

Wayar sa yakashe yana goge hawaye

Kamar wasa okasha yaji kuka, yana juyawa yaga Shahid yana goge hawaye

Subhanallah, Shahid meyake faruwa?

Kamar jira yake a tambayeshi nan yaci gaba da kuka haiqan, yana cewa shikkenan narasata okasha

Okasha narasa Amal, yarinyar nan da soyaiyarta na rayu acikin zuciya ta

Jikin okasha yayi sanyi,ya janyo shi jikinsa yana rarrashinsa

*** *** ***

Ungo wannan karbi Kisha, umma menene wannan din? Bansaniba yarme tsinannan surutu

Bata qara maganaba takarbi maganin ta shanye

Umma zanje gidansu rumaisa, bazaki ba, kije nan gidan hauwa'u tana neman ki

Babu yanda ta iya haka zura hijabin ta tatafi, tunda bikin nan ya matso ake dirka mata wannan magungunan, tarasa na menene

Ko duk Dan wannan gunkin sukeyi oho

Tana zuwa gidan anty hauwan ma, magani tahada mata tasha, wani kuma tabata su aleda Wai tanasha kullum idan ankaita bauchin

Koba bauchi ba

Zasuga bauchi

*** *** ***

Alhaji kaide kadage Akan auren nan, wallahi kuwa hajia, aure kamar anyi angama insha Allah

Yatsina fuska tayi, tayi shiru batare data qara cewa komai ba

Ina agogon nan nawa?

Wai agogon daka siyo a Qatar kaida president?

Eh shi bani shi,

Tana kawo masa yasaka, yagyara Zaman babbar rigar sa, ya kalleta yace Toni ke kin zauna ko yau bazan samu afesa min turaren ba?

Batace komai ba ta tashi tana cika tana batsewa, tafesa masa, yace yauwa kokefa

Angama saka akwatunan acikin motar?

Eh angama alhaji

Tosh mu muntafi saimun dawo, shi daddy yacemin yana jiran

Jabir, jirgin su zai sauka nanda 20 minutes

So zasu biyo mu daga baya

To alhaji Allah yakaiku lafiya, Allah yatsare Amin hajia

Yana fita suka shiga motoci shida tawagar yan daurin aure, basu zarce ko Inaba Sai jigawa state

*** *** ***

Jb, Babu inda zani, Akan wannan qanqanuwar yarinyar zanje indebowa kaina gajia, wallahi bazaniba

Jirgin ku yasauka da niyya nace masa Kai nake jira

Haba daddy, Abba nefa, meyasa zakai masa qarya? To Jb ya zanyi? Wai kasan yarinyar dayake shirin aura min ne? Yaushe ma Salman ta rasu?

Yarinyar fa batafi shahida ba, haba me zan tsinta ajikin ta?

Daria Jb yasaka

Yace a a fa daddy karka zo kana qaramar murya daga baya

Kai yarinyar fa nakasashiya ce, wallahi batada lafiya, liqamin ita ake so ayi

Kafin Jabir yayi magana wayar daddy tadau qara

Gabansa ne yafadi dayaga sunan Abba baro baro ajikin screen din wayar

Ahankali ya amsa, acan kuwa Abba yanata Fama da jama'ah Ana jiran ango yazo a daura aure tunda yace zasuzo daga baya

Abba yace Ina kuka tsaya ne, har yanzu shiru babu ku

Sumar kansa yashafa yace Abba Mota ce ta lalace mana ahanya

A a Mota ta lalace muku bazaku tsaida wata ku taho ba, yanzu Yaya kukeso ayi?

Abba kawai a daura

Abba yanajin haka yashaidawa mutane ango Mota ta lalace musu

Dan haka a daura aure

Babu Bata lokaci aka daura auren

Amal da karaam, Akan sadaki nera dubu Dari biyu, lakadan ba ajalan ba

Comments

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

10

Agida kuwa anata hidimar biki, yan'uwa daga Niger sunzo, sai kuma maqota da yan'unguwa dasuka yiwa umma Kara suka zazzo

Nikuwa muna daki nida rumaisa Sai qawaynmu yan islamiya dasuka zo mana

Ajima kadan in goge hawaye, naqiyin wata kwalliya, mutane kowa Sai magana yake in tashi in shirya, na zauna Ina kuka kamar Wanda akamin dole, maisah ce mai kareni da cewa kukan rabuwa da umma ne, dahaka take rufe musu bakinsu

Da mutane suka ragu maisah tace Amal banga angon namu ba, ai yakamata ace yazo kun gaisa ko

Idanuna jajir nace maisah basai yanaso ba zaki ganshi

Shimafa bayaso, ninarasa dalilin baba nayin wannan aure, tunda babu Wanda Yake so kawai a rabu damu,

A a Amal duk abinda babba yahango yaro bazai hangoba, kede kiyi biyayya da hakuri Dan Allah Amal

Nace to maisah ta

A kofar gida kuwa, Ana gama daurin aure aka shigo da kayan lefen akwatuna dozin biyu

Baba yace ai alhaji ku koma da wasu kawai, kayan sunyi yawa, Abba yace haba Malam Muda muke cewa sunyi kadan, Dan Allah kadena wannan maganar adauki kayanta abata, haka aka shiga dasu gida, jama'ah kowa yagani, yana tofa albarkacin bakinsa

Abinci kuwa Sai kawo shi ake baqi kowa yaci yakoshi babu laifi anyi musu karba ta mutunci

Bayan azahar aka fara shirin tafiya bauchi tare da amarya, baba hamani yace shi bazai jeba, tunda akwai yan'uwa dazasuje su Gano inda take, hannun ta yakama da kansa yace alhaji ga amanar Amal nan, batada kowa ku kadai tasani, alhaji bazamu lamunci aciwa Amal mutunci ba, ko waye tsaf zan hawo Mota inzo in dauki yata mu tafi

Abba yace haba Malam, ai Amal kamar ya take awajena, batada banbanci itada daddy, insha Allah baza'a samu ko wacce irin matsala ba

Haka iyayenta sukai mata fada, aka daukesu Sai bauchi, hannun ta yana cikin na rumaisa

*** *** ***

Shahid Ana Kiran wayarka fa

Yana daga kwance yace inaji okasha, wannan Yarinyar ce, kabarta idan tagaji zata dena ai

Haka wayar taita ringing, karshe ma Sai ya kashe wayarsa baki daya

Shahid wannan tunanin fa babu inda zai kaika, ni a ganina tunda yarinyar nan anriga anyi auren ta, kawai ka hakura, ga wata anan yarinyar nan tana Mutuwar sanka, meyasa bazaka amince ba

Kallan okasha yayi da kyau, okasha? Kalau kake kuwa? Ni in auri wa? Yarinyar da batada aiki Sai tallar jikinta a titi

Tana ganin hakan shine wayewa, tayaya zan auri sauran kallan wasu

Hmm ajiyar zuciya nazy yasauke, daya gama Jin duk kalaman su, yace Lalle Shahid kana da aiki agabanka, to yanzu a Ina kake tunanin zaka samu irin yarinyar dakake so?

Kullum cikin hijab

Bafa zaka samu ba

Zan samu nazy, Amal, Amal dina haka take, dahaka nayi Mata tarbiya tun tana qarama

Amal Amal Amal, kaide komai Amal, to yanzu de matar wani ce, tunda tariga da Tafita daga hannunku

Lover boy kadau qaddararka kawai

*** *** ***

Kema de shahida da tsinannan naci kike, kin kira yaqi yayi picking, kinsake kira yakashe wayarsa, Amma ahakan zaki debi jiki kibishi gidansu, wallahi ni DANA SANI ma daban fada miki inda gidan yakeba

Sunkuyo wa tayi daidai fuskar jamcy, tace inde naci yana bada soyaiya, to naci na zai bani soyaiyar sa

Tamiqe ta dauki jambaki ta shafa, Dan qaramin mayafi ta dauka tayi rolling, sosai tayi kyau, doguwar face dinta ta tsaru

Jakarta ta dauka, tace Shahid na shahida ne, Babu me shiga tsakanin mu

Jamcy batasan lokacin datasa daria ba, ta kwanta, tace Allah yadawo dake lafiya, ban fara shirya karbar dizgi awajan da namiji ba

Tana fita Bata zarce ko Inaba, sai gidansu Shahid

Nocking tayi, suka Bata damar shiga

Dukansu suna falo

Shahid yana ganinta ya lumshe idonsa, shikam yagamu data kansa, matar datake bin namiji har gida Wai ita ake kira ya aura

Nazy yace a a shahida sannu da zuwa, bari akawo miki lemo, tace no nazy aida ka barshi ma, yace a a ai baqonka annabinka inji bahaushe, yafadi haka yana kallan Shahid, saiyaga shi idonsa arufe yake ma, aransa yace Lalle wannan gayen da gaske yake

Okasha ma yace aida kin fada mana zuwan naki da mun Dan gyagygyara gidan namu, Amma haka kin samemu.... Be qarasa ba yana murmushi tace Ayya babu komai okesh

Hmm Wai okesh, ni batasan wannan qyale qyalen na yanmata baya gabana ba, inji Shahid aransa

Nazy yana kawo Mata lemo yayi daki, Shima okasha haka

Tashi tayi ahankali tadawo kusa dashi ta zauna

Tasan ba bacci yakeba, kawai yayi hakane saboda bayasan ganinta, Dan haka tace kayi hakuri Ina takurama, dama nazo inyima sallama ne zanje nigeria yayanah yana aure

Bai Bude idonsa ba yace Allah ya kiyaye

Kallansa tayi tasaki murmushi, ita komai yayi wallahi birgeta yake, Dan haka dubu sajen fuskarsa, kamar tasashi a gaba taita kallo

Jakarta ta ajiye, ta miqe tafara gyara falon, tas takwashe abinda yake ciki, su gwangwanin lemukan dasukasha, tagyara kujerun, ta Kade su sosai, zuwa tayi dede inda yake, tarasa me zata ce masa. Dan haka tabude jakarta da sauri ta dauko wayarta, tafara tashinsa dede hannun sa tadan daka da wayar, Bude idonsa yayi bece mata komai ba, tace ko zaka Dan matsa zan gyara wajan ne

Waye yasaki?

Jikinta ne yayi sanyi

Tace kayi hakuri

Tashi yayi bece mata komai ba, yakoma kan kujera saida ta gama tsaf, sannan tadau jakarta tace to Sai Allah yadawo Dani lafiya

Kawai daga mata hannu yayi, tana kallansa harda Wai waye sannan tafi ce daga gidan

Tana fita su nazy suka dawo, hada ido sukai da okasha, okasha yace ah ashe har soyaiya tayi Nisa kenan, Kuna aiki tare, kaga muma munci albarkaci kunyi mana gyaran falo yau

Kallansu yayi yace ni? Dani zatai aiki?

Tab

Daga haka basu sake cewa komai ba Dan sun lura akusa yake

*** *** ***

Jama'ah duk sun jigata, muna isa directly gidan momy aka kaimu, part dinta aka nufa Dani, qannan baba ne na Niger suka bani umarni in shiga da addu'ah haka akayi kuwa

Gidan cike yake da baki maqil, muna zuwa aka saukemu awani daki, maisah tana tare Dani, abinci aka kawo mana kowa yaci, nikam bawani na kirki naci ba, mukai wanka, wani less suka sake bani na saka light green sosai nayi bala'in yin kyau

Babu Bata lokaci Abba yaturo inje, nida yan'uwan mahaifina da maqotanmu muka tafi, kaina a lullube, Bayan ansake gaisawa ne

Suka bada amanata, sosai Abba ya karbemu hannu bibbiyu, momy ma babu yabo babu fallasa

Nan suka fada masa da safe suke San wuce, yace babu damuwa Allah yakaimu

Dakin da aka bamu muka dawo, sosai Dakin ya birgeni, kuma Wai ahakan ma na saukarmu ne, banawaba

Abba ne yadubi hajiya yace kiramin daddy awaya mana

Tana kiransa babu Bata lokaci yazo, yana cikin yadi fari mai mutuqar tsada, yayi kyau sosai

. Yana zama Abba yace Ina jabir?

Yana daki yana jirana Abba

OK kiramin shi

Wayarsa yadauka yakira jabeer

Kansu Akasa dukansu Abba yace jabeer sannu da zuwa ya hanya? Saikuma Mota ta lalace muku ahanya ko? Gashi babu yanda za'ai saikuka dawo gida bakuje wajan daurin auren ba

Jabir yakasa dago kansa, yace Abba kayi hakuri munyi laifi

Babu komai ai rayuwa ce, abinda zan fada muku kenan

Iyayen yarinyar sunzo kwana iya zuwa ku gaisa, inkuma hakanma kafin ku qarasa kafafunku zasu fara ciwo, zaku iya zama basai kunje ba

Wai yanzu alhaji saboda Allah Akan wannan yarinyar da aka dauko daga wani kango zaka dinga musu wannan fadan, haba alhaji

Wato juwairah Naga alama kece kike daure wa Yaron nan gindi yake abinda yaga dama

Auren nan de anriga da andaura, matarsa ce, bamu sa iko akanta saide muyi musu fatan zuri'ah ta Gari

Saida taji zance zuri'ah, sannan tayi ajiyar zuciya tace to Allah yabada Zaman lafiya

Abba yace dade yafi muku, yatashi yayi ciki ko sake kallan su daddy beyi ba Wanda kansu yake sunkuye

Aisai kuje ku gaisa, itama ta tashi tatafi

Jb yace kaga abinda nake fada Maka ko? Kaga abinda kajawo mana ko?

Abba yana ganin mutunci na Kasa yana yimana fada da girman mu da hankalin mu

Katashi muje

Kansa yariqe da hannun sa, shi tunda yake da iyayensa basu taba yimasa irin wannan fadan ba, bayasan damuwa ko kadan

Amma yanzu Akan wannan yarinyar har ran Abba yabaci yatashi yatafi yana yi musu fada

Jb kaje ku gaisa, gobe kafin su tafi zanje mu gaisa insha Allah

Yana fadar haka Shima yayi part dinsa

Girgiza Kai Jb yayi, yatashi yanufi part din su Amal

Lokacin dayaje harta tashi zata cire kayan jikinta ta kwanta, aka fada musu ga abokin ango yazo, har qasa ya tsugunna yagaidasu, sunata tambayar sa Ina ango Ina ango, yace bayajin dadi ne, Amma yace kuyi hakuri gobe yana Nan tafe insha Allah

A a babu komai wallahi

Tashi yayi zai tafi, aransa yace shi bemaga amaryar ba

Aikuwa Kamar sun San me yake cikin ransa, yana fita suka tura Amal taje tayi masa godia, kuma tace tana yiwa angon Allah yasawaqe

Yana tafiya yaji taku abayansa, yana juyawa sukai ido biyu dashi

Tsarki ya tabbata ga ubangijin daya tsara wannan halitta

Amal ce ta katse masa tunanin sa da fadin

Mungode abokin ango

Jb ya zuba mata ido, wannan zazzaqar murya haka

Yace a a babu komai

Kece amaryar Tamu ne?

Karkada idonta tayi, tace nice, shidin meya hanashi zuwa?

Jb cikin ransa yace tofa, da alama wannan bazata ragawa daddy ba, wannan wanne irin zama za'a yi?

Cikin sauri yace bayajin dadi amarya Amma gobe ai dole yazo

Tabe baki tayi tana juyawa tace to Allah yasawaqe, mungode saida safe

Bayanta ya kalla, cikin ransa yace gaskya Allah yayi halitta anan, aikuwa dole inje infesawa abokina

Yana fadar haka cikin ransa, yayi part din daddy

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

11

Ina dawowa daki nakwanta, maisah tace gobe iyanzu kuma muna gida, ke maisah yanzu har murna kike zaki tafi ki barni

Zan tafi may be ba Lalle bane Inga mijin ki

Ni Ina miki maganar tafiya Amma kinamin zan can wancan me kamar gunkin

Amal mijin ki nefa, be dace kidinga fada masa hakaba

Ajiyar zuciya nasauke nakwanta tare da juya mata baya, bacci nayi me dadi cike da mafarkin Yaya Shahid

*** *** ***

Kai abokina gaskya kayi babban kamu

Kaga matarka kuwa? Gaskya ta hadu ba qarya

Jb Dan Allah kayimin shiru, kazo Sai zuba kake kamar aku, daga ganin yarinya, bafa ita bace, ita wannan yarinyar batada lafiya larura gareta

Sannan koba hakaba, yanzu jb har yaushe zan iya mantawa da salma har inso wata Bayan ta? impossible jb

Shiru jabir yayi, shide yasan wannan yarinyar daya gani itace amarya, to Amma besan wacce larura daddy din yake nufi ba, may be ta aljanu ce

Dan haka kawai sai yayi shiru

*** *** ***

Washe gari da wuri baqi suka shirya, saboda nisan hanya, Babu Bata lokaci aka kawo musu abinci, da abinsha, kowa Sosai yayaba, dazasu tafi Abba yabada motoci a mayar dasu, Amal ta riqe maisah banda kuka babu abinda take

Maisah karki tafi Dan Allah, Amal dole zan tafi, insha Allah nayi miki alqawarin watarana zanzo mu wuni, saina koma Amma banyi miki alqawarin kwana ba, Toshiknn maisah ki kula min da iyayena, ga wannan wasiqar Dan Allah ki kaiwa Yaya sham

Kiyi masa bayanin komai kice masa ya yafemin, sosai suka rungume junansu suna kuka, manyan ne suka qara yi Mata fada, sannan suka fita, zama tayi agefen gado ta dinga aikin kuka

Suna fita harabar gidan, Amma yabada umarni akaisu gidan daddy suga gidan da Amal din zata koma da zama, haka akayi kuwa sunje gida kuma sun yaba, gida kamar ba'a qasar Nigerian kakeba

Daddy! Daddy!!

Wallahi katashi baqin nanfa zasu tafi, miqa yayi tare da addu'ar tashi daga bacci, dagashi sai jallabiya yafuto harabar gidan

Abba banda harararsa babu abinda yake

Yana qarasowa maisah cikin ranta tace tab wannan daga ganima may be shine angon, aikuwa har qasa ya tsugunna ya gaidasu

Yana basu hakuri Akan rashin zuwan sa jiya, sosai suka fahinceshi, sukace ai dama abokinka yace bakajin dadi

Baice komai ba, yasa hannu a aljihu ya ajiye musu damin kudi, yajuya yakoma

Maisah cikin ranta tace Allah Sarki Amal, kowanne irin zama za'a yi anan? Sam baya magana, ai dole ma ta dinga cewa gunki

*** *** ***

Kuka na nake ni kadai adaki, Danaga babu inda kukan zai kaini, tashi nayi nashiga toilet nayi sabon wanka, Riga da sket nadauka acikin atamfofina mai launin purple na saka, dinkin yahau jikina kamar Danni akayi, ban daura dankwalin ba na futo falo na zauna nazuba uban tagumi, Babu waya bare inkira yan'uwana inji Yaya suke, Amma ai nariqe number kowa akaina, ko wayar ma'aikatan gidan nasamu zan kirasu umma da Yaya Shahid dina

Ina wannan Zaman bansan lokacin da bacci yafara daukana ba a kwance Akan kujera

Sosai ya hade cikin suit ruwan toka, yayi masifar yin kyau, yana fesa turare jb yace Toni zan wuce

Amma daka cire wannan kayan Kasa manya saboda kasancewarka ango yau

Kallansa yayi bece komai ba qarshe ma sai yace ka gaida gida

Tare suka futo, jb yafita shikuma yayi part din iyayensa

Yana zuwa yaga momy afalo, Bayan ya gaida tane, yamatsa jikinta, yadora kansa Akan fadarta yayi shiru

Sumar kansa dataji mayuka ta shafa, tace muje nabaka abinci ko

No momy banjin yunwa saide ko anjima

Kallansa tayi, tasan Sarai yanajin yunwa Amma saboda wannan auren yasa shi a damuwa har yaro bayasan cin abinci, Dan haka tayi shiru, tana shafa masa kansa

Abba ne yasauko daga daki,

Daddy na ganinsa tunma kafin ya gaidashi, yace kai tashi kaje kakiramin matarka zanyi magana daku

Mata?

Shi wallahi Yama manta da wannan yarinyar

Tashi yayi yatafi, iyayen suka bishi da kallo

Yana zuwa falon, yabi ko'Ina da kallo, har zai shiga daki yaga mutum Akan kujera, yasan de kowa yatafi Dan haka wannan itace

Tana kwance tana bacci, kyakkyawar Fuskarta ta bayyana, gashin idonta ya kalla Zara Zara dasu, sannan yabi Dan qaramin Bakinta mai launin pink color da kallo, goshinta ya kalla duk suma, alamar tana da gashi

Tsayawa yayi ya zuba mata ido yana kallo

Yana tsaye baisan lokacin daya tsugunna ba, yakafa mata ido, kawai yana kallan ta, meyasa komai nata yake da kyau haka?

Ba lefi gaskiyar jb ne, tanada Dan kyau, to Amma meyasa take sa wannan baqin abin aface dinta?

Wayarsa ce tayi qara, Dasauri ya miqe tsaye, yana picking Abba yace Bata nan ne?

Gamu nan zuwa Abba

Memakon ya tasheta a a saiya nufi fridge yadauko ruwa, yabude murfin ruwan, yafara tsiyaya mata ajikin ta

Azabure ta miqe tana salati

Sanadin haka ne yasa Dan kwalin kanta da bata daura ba yafadi

Zubawa gashin kanta ido yayi, yanzu wannan yar mitsitsiyar yarinyar har tasan tasaka attached Akan ta?

Lalle duniya tazo karshe

Kallansa tayi, da alama kallan cike yake da Jin haushi

Aranta tace azzalumi kawai

"ki tashi Abba yana kira "

Yana fadar haka ya wullar da robar ruwan

Yayi hanyar waje, har yaje bakin qofa yajuyo, ya kalleta, alokacin ta kama gashin kanta tana nadeshi akanta kamar ribbon

Tana gamawa tasaka hijab dinta, sai tayi kamar Tasa ribbon acuci maza

Abaya ta biyoshi ,yana gaba tana binsa abaya, sai hararsa take daga baya

Dahaka sukaje har folon

Momy da kallo ta bita, aranta tace kidahuma kawai, ji wani uban hijabi, Wai ita yar Malam

Yanda taga yayi, haka tayi itama, ta zauna aqasa, tana gaidasu ba yabo ba fallasa momy ta amsa

Abba kuwa tuni yafara fara'ah, yace Amal ki saki jikinki kinji, ki dauka kamar gida ne, muma kamar amatsayin iyayenki muke, da nan dacan duk daya ne kinji, kanta asunkuye tace to Abba Allah yaqara girma

Momyyyy nah, dahaka tafara tafado falon cikin murna tana rungume mahaifiyar ta

Anty mufy tace yar renin wayo, kizo kidau jakar ki, Babu bawanki anan, haba mufeeda, yanzu daga dawowar taku daga airport kike mata fada?

Yanzu fa ta duro qasar

To yanzu momy haka za'a bar yarinyar nan baza'a yi Mata fada ba, haba momy

Qarasowa falon tayi, daddy dasuke zaune qasa shida Amal, takaiwa rankwashi akansa

Dafe wajan yayi yace auuuch, kamar zaiyi kuka yace Haba anty mufy

Tace ohh bakai baka iya gaisuwa ba

Yana shafa wajan yace Mata morning

Tana daria ta zauna a kujera kusa da Abba

Amal ta dago kanta tace mata Ina kwana?

Cikin fara'ah tace lafiya kanwata ya kwanan baqunta

Alhmdlh kawai Amal tace

Abba ne ya kalli Shahida yace baki iya gaisuwa bane? Kallan daddy tayi tace Yaya daddy good morning, Ala Sanya alkhairi

Ko 'a' baice mataba

Sake kallan ta Abba yayi, tuni tagane manufarsa, kallan Amal tayi tana yatsina tace yakike?

Lafiya, Amal tabata amsa ataqaice

Cikin ranta tace dubeta Dan Allah, gashi de tanada kyau Amma ta boyeshi, tawani saka hijab, ita abinma abin qyanqyami

Kallanta tasake yi afakaice, ita kamar tana mata kama ma da wanda tasani

Abba ne yamiqowa, Amal kwalin waya qirar tecno yace gashi Amal, kidinga amfani da ita, ki bayar data hannunki

Cikin ranta tace Abba kenan nikam dama Ina Naga wata waya

Karba tayi tana godia

Ga wannan kuma, mukullin motar dana Sai miki ne, daddy zai koya miki da kansa

Kaikuma ga wannan

Mukullin ya kalla yagane Sarai na gidansa ne, Dan haka yaqi karba yazubawa Abba ido

Cikin fada Abba yace karbi mana

Amma Abba key din wancan gidan nefa

Abba yace sosai

Kansa ya sunkuyar yace Abba kayi hakuri bazan iya rayuwa agidan nanba, bazan iya shigaba, zai sani a damuwa

Zaka karba ko bazaka karba ba?

Ganin abban ya hade rai ne yasa yakarbi key din

Abba yace tashi kadau matarka ku tafi, za'a biyoku da kayaiyakin ku, basai kun dawo ba

Tashi yayi fuskar nan babu alamun wasa yafuto

Nima sallama nayi musu natashi, nafita

Abba yadubi mufy yace mufeeda kije keda shahida ku sa ma'aika ta sudau kayan kuje ku tayaasu gyaran gidan

To Abbanah inji mufy

Tashi yayi yakoma daki, mufeeda ma tayi part din daddy zata sa afara futo da kayaiyakin sa

Shahida ta kalli momy tace momy yaushe za'a fara dinner ne, na matsu in fadawa friends dina, suzo mu cashe

Babu abinda za'a yi shahida, abban ku yahana, bansan menene dalili ba, Koda yake garama ai Kar ayi komai din, Dan idan muka gayyaci mutane dayawa, aka tambayemu yar waye aka bawa daddy, bansan me zamu ceba

Gara Kar ayi taron dade muce yar Malam ce datake wani kango aka dauko

Ni momy meyasa ma Abba yake yiwa Yaya daddy hakane, Amma to momy shi yayan yana Santa ne?

Tabe baki momy juwairah tayi, tace oho masa, shi Ana gane alqiblarsa ne

Ai shikkenan, yauwa momy namanta ban baki labarin Shahid dinaba

Kallan mamaki tayi mata, shahida da soyaiya

Tace waye kuma shahid? Cikin shagwaba tace kaiii momy

Boyfriend dinanefa

Murmushi tasaki murmushi tace tofa, zamani Ina zaka damu?

*** *** ***

Muna fita harabar gidan, Naga Sai huci yake kamar wani zaki, kallan motor sa yayi yakaiwa tayar motar duka da qafa, sannan yabude yashiga, yayi reverse

Nayi tunanin tafiya zaiyi yabarni, sainaga ya tsaya, Dasauri nabude Bayan motar nashiga tare da rufewa

"ni direban ki? "

Kamar wasa ta tsinci maganar sa, Dan haka ta futo Takoma gaban motar suka dau hanyar gidansa

Aranta tana tambyar kanta to meyasa bayasan shiga gidan?

Nashiga uku kode aljanu ne agidan?

Kokuma wani Abu aka masa yace gidan zai sashi a damuwa?

Meyake nufi da hakan?

(nikuwa nace tambayeshi)

Suna Zuwa kofar gate din dayake gidan ba Nisa, iliya mai gadi yazo ya wangale musu gate

Harabar gidan ta kalla da swimming pool tafara tozali, gashi an qawata shi da flowers

Yana ajiye motar ya shige gidan ransa abace

Dasauri ta futo tabi bayansa, Saman beni taga yahau Dan haka ta nemi kujera a falon ta zauna

Daga kan dazatai idonta yayi tozali da tamgamemen photonsa shida salma, tana rungume ajikinsa suna murmushi

Gabanta ne yafadi bade aure ne da mutumin nan ba

Dama yana murmushi?

To Amma wacece wannan,? Kode Shima ta addabeshi ne shiyasa yaqi Zaman gidan Amma shine ita aka yayimota aka kawo ta

Photon ta zubawa ido tana kallo

Ahankali taji taku akanta, tana daga Kai, ta ganshi yasauko da key ahannunsa

Yabude wani Dakin aqasa yashiga tare da banko kofar

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

12

Tagumi na rafka, saikace Wanda nayi masa wani Abu zai dokomin kofa , da abayansa nakema saide injita afuska ta

Hijabin jikina nakama nacire, nadaure kaina da dankwali

Naci gaba da Tagumi Ina tunanin wannan sabuwar rayuwa dazan fuskanta

Yarinyar dazu natuna, daga gani zatai rashin kunya, kuma wallahi bazan daukaba, kodan mema yahadani da ita, dazan kulata Ina asarar mutunci na dana iyayena

Ina wannan tunanin Naga anfara shigowa da akwatuna

Nawa aka fara shigowa dasu Ana ajiyewa a falon

Sannan na daddy

Anty mufy ce tashigo da murmushi afuskar ta, kusa Dani ta zauna, tana cire mayafin jikinta

Tace qanwata ki saki jikinki kinji, nan gidan mijin ki ne

Kinji? Tafadi haka tana murmushi

Ban iya cemata komai ba Sai gyada Kai

Am raliya Dan Allah Kai mana wadannan akwatunan wannan Dakin ta nuna wani daki kusa da wanda daddy yashiga

Nan da nan suka Kai akwatunan Amma na wajena

Kallo na tasake yi da murmushi tace Ina mijin ki yake?

Diriricewa nayi, Wai mijina

Ina in Ina nace mata yana Nan

Na nuna mata Dakin daya shiga

Kallo na tayi da murmushi ta tashi tashige Dakin

Gani nayi ta futo, yabiyota abaya

Hannayensa suna cikin aljihun wandon suit dinsa

Zama tayi kusa Dani ta dafa kafada ta, tace Amal

Kinga wannan? Ta nunamin daddy

Ku biyu zaku zauna agidan nan, bayasan ma'aika ta, saboda haka ki ware ki saki Jikin ki

Idan aiki yatashi kiyi masa magana yazo kuyi tare

Karki yarda yabarki da aiki ke kadai, ta dubeni tana murmushi tare da fadin kin gane?

Kallan Wanda ake maganar akansa nayi, Naga shi ko ajikinsa, yana tsaye yana zagaya wa acikin falon, juyowar dazaiyi idonmu yahadu

Dasauri na sunkuyar da kaina

Duk atakure nake jina, ni ban saba cire hijabi naba inba agaban Yaya Shahid ba

Kamar tasan abinda nake tunani tace muje dakin mu shirya kayan ko

Nace to

Muka shige Dakin dayake amatsayin nawa, tajuyo ta wurgawa daddy harara

Wai ita datace yazo yazauna a falon yabarni ni kadai shine yazo yatsaya mana aka kamar wani soja

Muna shiga Dakin ta jeramin akwatunan waje daya

Ta shirya min gaban mirror na

Ta Bude jakata ta shirya min wasu kayan, sauran tace idan nagama insaka su awani wajan daban

Gaskya Dakin ya birgeni sosai, komai pink color ne adakin,

Toilet din babba dashi

Muna gamawa takama hannu na muka futo falon, yana zaune adaya daga cikin kujerun falon

Kitchen muka shiga, da ita, haka ta ware tana fira tana Jana da surutu, nadan fara sakewa da ita, pride rice mukayi Sai farfesun kaza, dayaji kayan qamshi

Duk abinda Naga bansaniba a kitchen din, warewa nayi nake tambayarta, sosai na fahimci komai cikin qanqanin lokaci

A dining muka ajiye komai, tace Amal zuba mana abinci Ina zuwa

Wajan daddy ta nufa, tana zuwa takama kunnansa taja, da karfi yace wayyo anty mufy

Tace wuce muje Kaci abinci, tana riqe da kunnansa takawo shi har dining din, nikuwa Ina kallan su, sai suka bani sha'awa, nan take na tuna da Yaya Shahid dina

Cikin shagwaba yace anty mufy nifa na qoshi

Ban yardaba qanina,maza Bude bakinka

Haka ta dinga bashi abinci da kanta, Babu abinda suke tunamin irin lokacin da yayanah yake bani abinci agida, wani Abu na baqin ciki ya tokare min baqoshina

banda juya spoon din babu abinda nake

Juyowa tayi tace saura ke Amal

Dasauri nace anty na qoshi

No ban yarda ba, haka tabani abinci da dakanta, naci, gaskya matar nan tana da kirki sosai, nafadi hakan cikin Raina

Muna gamawa tace Toni zan wuce qanina, sai wani lokacin kariqe Amal sosai

Tace qanwata zomuje ki rakani zan tafi

Kamar zanyi kuka nace Dan Allah karki tafi

Juyowa yayi ya kalleni,fuskar nan atamke wato za'a barta da dodo ko aljani ko

Murmushi anty mufy tayi tace karki damu, duk lokacin da kikesan ganina ki fadawa daddy zai kawoki har Abujan kinji

Cikin sanyin jiki na girgiza kaina

Hannu na takama muka shige dakina, Shima daddy tashi yayi yahaura sama

Muna shiga Dakin muka zauna abakin gado, takama hannayena duka biyun tace

Amal, Dan Allah ki kula min da qanina, daddy yana buqatar kulawarki, karki damu da rashin maganar sa, haka yake, zaku zauna dashi maganar minti biyu bazata shiga tsakaninku ba

Sai Bayan zuwan salma cikin rayuwar sa ne muka Dan samu canjin halayensa

Bansan lokacin da bakina ya furta wacece salma?

Kai tsaye tacemin matarsa ce

Cikin Raina nace ai dama nafada

Anty mufy taci gaba da fadin matarsa ce Amal, Amma Allah yayi Mata rasuwa

Yana tsananin kaunar ta, itama haka, iyayenmu basuda wani Jin dadi da kwanciyar hankali, kasancewar mu yan kadan

Bamuda kowa

Kuma Allah Bai bamu haihuwar Akan lokaci ba, na dade da aure Amal, Amma har yanzu Yarona daya, salma ta samu ciki, wanda muka dauki son duniya muka dorawa cikin

A qarshe datazo haihuwa ta rasu itada abin dayake cikin ta

Daddy ya fuskanci qunci, kuma har yanzu shine yasa bai dawo normal ba kamar yanda yake da

Kinsan Abba Dan siyasa ne gaba da baya, sau biyu yanayin govnor Awannan jihar, daddy kuma ya riqe muqamin sanata sau daya

Hakan ne yasa ayanxu haka suka tsaida shi Dan takarar govnor na wannan jihar, wanda za'ai zaben nan da wata daya insha Allah

Salma ta rasu Awannan gabar, hakan ne yasa Abba yahadaku aure keda daddy, saboda cancantarki, saboda yasan zaki iya kula dashi,

Ki tayashi da addu'ah, Allah yasa adace a zaben dazamu fuskanta

Addu'ar mata Akan mijinta Bata hijabi awajan ubangiji, naroqeki kidinga sa daddy acikin addu'ah Bayan kinyi sallah

Kati ta dauko ta miqamin, dakyar na karba saboda yanda jikina yayi sanyi dajin kalaman ta

Tace Number na ce, idan da matsala, kokuma akwai abinda yake miki Wanda bakya so, saikiyimin magana ta waya

Nizan tafi, daqyar na iya cemata to anty nagode, saboda yanda jikina yayi sanyi, kenan auren rufin asiri akamin, saboda anaso yaci Zabe, Kar ya zauna baida mata

Muje na rakaki anty, a a Amal kiyi Zaman ki ki huta, driver na jirana awaje, ki kula da kanki da mijin ki, sai anjima

Tana fita, bansan lokacin danaji hawaye ba, ni anrabani da Yaya sham, anrabani da yayanah mai sona Yaya Shahid

Anzo an liqawa Wanda bai damu daniba, hakan yana nufin dazaran yaci zabensa banda wani amfani kenan

Ke garama hakan, gara yaci zabensa yasakeni naje na auri dan'uwana

Wayar da Abba yabani na kunna aikuwa naganta da cajin ta, da Sim card aciki Ina duba balance dinma Naga ten thousand aciki, ido na zaro, towama zan kira da wannan uban katin

Wayar umma nafara kira cikin zumudi

*** *** ***

Yanzu kenan tafiya zakiyi shahida,?

Tafiya zanyi nusy, tunda baza'a yi wani bidiri awajan bikin ba

Gobe zan koma school insha Allah

Nusy tayi fari da idonta, tace to ai kya kaimu gidan yayan naki muga new antyn naki ko

Dena ba tamin rai nusy, kidena min zance yar qauyen nan please

Shikkenan kiyi hakuri qawata yanzu de muje

Motar shahida suka nufa, suka shiga su biyar, da nusy babbar qawar shahida a Nigeria, sai sauran mutum uku, suka nufi gidan daddy

*** *** ***

Ina gama waya da umma nakira baba, haka yayita tambayata babu abinda akemin de ko?

Nace babu, yace idan akwai abinda mijin yakemin in kirashi infada masa, tare da turo masa da address din gidan, in bashi awa hudu zuwa biyar

Daria ce takamani nace baba babu komai, yace to Allah yayi miki albarka

Muna sallama dashi, nakira yayana, shikuwa alokacin yaga sabon layi, daga nigeria, jiyake shahida ce Dan haka yaqi picking

Saida nazy yace masa, Ana kiranka fa Shahid, cikin sanyin murya yace share ta nazy nasan wannan yar wahalar ce, Amma Shahid yakamata ka kirata kaji me zata fadama

Nikuwa awajena Danaga bai dagaba saina sake kira

Ina kira cikin fada yace, Wai miye ne?

Nace yayanah, kaida waye?

Yana daga kwance baisan lokacin daya tashiba, yace Amal? Dan Allah kece?

Daria nasa nace nice yayanah, I miss you so so so much

Amal miss you too, ina mijin ki kika kirani? To yayanah dole Sai yana Nan zan kiraka?

Yaya banasan auren nan

Tokiyi hakuri qanwata, muyiwa baba biyaiya insha Allah zamu ga ribar hakan

Yaya ba wannan maganar ba, bani labari

Yace wai waye yabaki waya ne? Kafin ta bashi amsa aka qwanqwasa Dakin

Dan haka tace yayanah Ina zuwa zan kiraka, tana kashe wayar itama tana turo Dakin tana shigowa

Ajiye wayar tayi, ta miqe tsaye, ta zuba mata ido, Riga da wando ne de ajikinta kamar kullum

Tana yatsina tace sannu ko

Amal data gama gane yarinyar batada mutunci Kai tsaye tace yauwa

Zaki futo ki gaisa da qwayena suna falo, tana gama fadar haka tafi ce,

Afili Amal tace yarinyar nan yar renin wayo ce

Dan kwalin ta ta yafa akanta tafice zuwa falon

Tana fita su nusy suka kwashe da dariya harda nunata da hannu

Kallan jikinta Amal tayi, tana neman makusa ajikinta

Sukuwa suka miqe suna cigaba da daria, shahida tace jiwata shiga Dan Allah yar qauyen qauyawa, kidahuma dake waike kinzo amatsayin matar yayanah ko

Nunata tayi da hannu tace Dan Allah kiduba kuga wadda takesan zama new first lady in bauchi state

Taqarasa maganar tare da dungure mata Kai, har Dan kwalinta yafadi

Hakan ne yayi Sanadin baiyanar dogon gashin kanta

Gaba dayansu suka hada wajan fadin attached?

Shahida tace au kina nufin da wannan abin zaki yaudari yayanah?

Nusy bani Reza

Aikuwa tana Bata ta nufi gashin Amal gadan gadan, ta riqe shi zata yanke, bige mata hannunta Amal din tayi

Amma ko gizau shahida batayiba

Ganin haka yasa Amal dukan hannun shahida, suma su nusy suna ganin haka suka rirriqe Amal

Shahida zata dora rezar akanta, Amal tafara ihun kuka, saboda sarkin yawa yafi sarkin qarfi

Ku qyaleni!

ku rabu Dani nace!

da karfinta take fadar haka

Shahida takama gashi ta riqe, Amal tana qoqarin qwatar kanta har suka yanketa a hannunta

kamar wasa yaji ihu aqasa

Kuma kamar fada ake

Tashi yayi, dagashi sai wando ajikinsa three quarter, baqi Sai Riga yar qarama data kama jikinsa, dantsan hannun sa sun futo sosai

Saboda yana hutawa ne

Dasauri yasakko qasa, cikin tsawa yace ke shahida!!!!

Dasauri suka saki Amal, tana kuka tana yarfe hannunta inda suka yanketa

Wani mugun kallo yamusu baice musu uffan ba, suka fice cikin sauri

Kallan sa yakai kanta, ahankali ya tsugunna dede inda take zaune tana kuka, yazubawa gashin kanta daya barbaje ido, dama wannan yarinyar gashin tane haka?

To Amma de duk yanda akai sudin ba Yan nigeria bane

Hannunta ta rufe da dankwalinta dede inda yake jinin

Cikin kuka tace masa Dan Allah na roqeka, idan Kaci zaben kasauwaqe min, inje in auri Yaya Shahid

Ni bazan iyaba

Kallanta yake shi har yanzu mamakin gashin kanta bai sake Shiba

Cikin ransa yace SHAHID

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

Yanzu wannan yarinyar har tasan soyaiya?

Dududu ma nawa take? Yar qarama da ita har tasan asaketa ta auri wani? Waye wannan Yaron? Waye shi?

Hake yake fada cikin ransa, yayinda azahiri ya kafeta da idanunsa

Tashi yayi yabar ta awajan, yahaura sama

Tana ganin tashin sa tabishi da harara, tashige dakinta da gudu tafada kan gado tasaki wani malalacin kuka

Itada ko malami ne yadaketa a makaranta yayanta da mahaifinta basa zama Sai sun rama mata itace wata yarinya da aqalla Bata wuce sa'arta ba ta yanka da Reza

Yana shiga dakinsa yafada kan gado tareda hargitsa sumar kansa, shifa bayasan damuwa, gashi tun ba'a je ko'Inaba yarinyar nan tafara haddasa masa husuma

Tana daki tana bawa kanta hakuri tare da goge hawayen idonta, taji anbude kofa

Qin dagowa tayi bare ta kalleshi

Tsayawa yayi akanta, yana Kallanta, tayi rub da ciki, gashin kanta yabazu Akan gadon kamar wata aljana

Matsawa yayi dede inda take, yakai hannu zai tabata saiya fasa

Yasake Kai hannu akaro Nabiyu, Shima yafasa

Sai akaro na ukun ne yafizgi hannun nata da karfi

Batasan lokacin datasa qara ba wayyo baba wayyo Yaya Shahid

Ko kulata baiyi ba, ya tsugunna yafara treatment din hannun nata

Kanta ta sunkuyar saboda azabar datake ji, hakan datayi ne yabawa gashin kanta damar rufewa daddy fuska

Dago kansa yayi yana Kallanta, gashin ya zubawa ido, kamar bazai taba ba, saikuma yasa hannun yakawar dashi, yaci gaba da wanke mata wajan

Hannun ya kalla fari tas dashi, farcen ta gwanin sha'awa

Ahankali itama ta Dago da kanta, tana kallan yanda yake aikin

Ta shagala a kallansa, Sarai yasan kallansa take shiyasa yaqara tamke fuskar sa

Yana gamawa yasaki hannun, yafice yabar Dakin

Ita kuwa da idanu ta bishi, mayar da gashin ta baya tayi, ta kalli Dan yatsanta inda yaduba, ta kwanta awajan bacci me nauyi yadauketa

*** *** ***

Amma Lalle yarinyar nan, jibafa yar qarama da ita har tasan duniya, shahida tace shiyasa nace muku bansan zuwa gidan, Dan zuciya ta zafi take, zatasa inyi abinda banyi niyyaba

Nusy tace to kiyi hakuri Kawai ai akwai wani lokacin saimun nuna mata ita yar qaramin matsiyaci ce

Dahaka sukai sallama, tatafi gida

*** *** ***

Sai magrib na farka daga baccin danake, ahankali natashi nacire kayana, har banasan dungurar wajan da aka yanka ni, towel na daura nashiga toilet

Nayi wanka, sai dangale hannun nake, da hannu daya nashafa mai na janyo doguwar rigar material acikin kayana mai launin blue, tayi kyau sosai, nasaka, da hannu na mai ciwon nadanne Bayan rigar, marar ciwon kuma Naja zif narufe bayana

Ko falon ban komaba, Naja wayata nakira maisah, nabata labarin abinda qanwar daddy tayimin

Rumaisa tace subhanallah, Amma wannan yarinyar batada mutunci, kiyi hakuri Amal, komai lokaci ne

Maisah wallahi baba zan fadawa yazo yadaukeni ni bazan iyaba maisah, wannan jaraba har Ina,

A a Amal, kinsan halin baba, abinda zaiyi kowa ba zaiji dadi ba, kiyi hakuri, kiyiwa mijin ki biyaiya, ayanxu aljannarki kike nema awajansa, ita qanwar sa ba aurenta kikeba, shi kike aure

Nace hakane, nan nabata labarin anty mufy, maisah tace kinji ba, tunda kikaji yar'uwarsa tace haka yake, to kiyi masa uzuri, idan abin maganar yakamaki ke kiyi masa kece aqasan sa

Nace to maisah nagode

Nabawa Yaya sham latter ki Amal, yayi ta kuka, kamar ba namiji ba, ni har yabani kunya ma, nace Allah Sarki Yaya sham, yasoni maisah, tace hakane, Allah yasa hakane yafi alkhairi nace amin

*** *** ***

Momy cikina ciwo, subhanallah Wai shahida har yanzu baki dena wannan ciwon marar ba?

Kai ta daga mata alamar eh

To sannu bari Akira likita, Bayan takira doctor yazo yadubata yabata magani tasha, yace hajiya idan bataji Dan sauqi ba atafi da ita hospital

Godia momy juwairah tayi masa yajuya yatafi

Kamar wasa taji sauqi, harma tafara hada kayanta, saboda gobe takesan komawa, momy tace haba shahida kibari kiji sauqi mana, saiki koma ko zuwa next week ne

Lalle momy Ina zan iya zama banje Naga shahid ba,

Afili kuwa saitace momy karki damu, ai naji sauqi

Momy tace Toshiknn

Kalau suka kwanta, tanata murna gobe zataje taga Shahid

1:00am ciwon nata yadawo, marar ta ta riqe har batasan tayi motsi

Haka tahanasu bacci Babu yanda momy ta'iya dole Sai asbiti suka tafi

Kamar wasa yana kwance yana bacci momy ta kirashi tafada masa halin dasuke ciki

Dasauri yasa jallabiyarsa, yahau Mota yafita, yana zuwa asbitin alokacin harta Samu bacci Bayan alluran datasha

Momy yajikin nata?

Da sauqi daddy, Abba ku yafita dazu shiyasa nakiraka, bari in shiga toilet zanyi sallah

Yace to momy

Gadon ya qarasa yana Kallanta, aransa yace marar ji kawai

Yana kallan Dakin dasuke kamar wasa yaji tana cewa Shahid...

Shahid...

Idanunta arufe da alama nafarki take, Kallanta yasake yi

Aransa yace SHAHID again?

*** *** ***

After 2 week's

Haka Zaman su Amal yakasan ce, daddy baya nemanta, itama haka

Babu wanda yake shiga sabgar dan'uwansa

Shi kullum babu fara'ah fuska a daure

Bata kula shi, ko taji motsinsa banza take dashi, saide abinda takasa ganewa shine, kullum saiya shiga Dakin dayake kusa danata

Tarasa me yake yi adakin tunda shide dakinsa asama yake

A bangaren daddy kuwa shi shaf ma yamanta da ita

Siyasar datake qara matsowa itace aransa

*** *** ***

Kwalliya akeci tagani tafada, jamcy tace qawata Sai Ina haka?

Fari tayi da idonta tace Sai wajan Shahid na shahida

Zanje mufita ko shan ice cream ne

Kallan agogo tayi tace Amma shahida yanzu karfe tara fa, kina ganin zaki iya Jan hankalin sa har kuje tare?

Karki damu jamcy, tana fadar haka tadau Jakarta tafi ce

Bata zarce ko Inaba Sai gidansu Shahid

Suna falo suna kallo dukansu, tayi sallama tare da shiga falon, Nazy da okasha suka tashi suka bar musu wajan

Cikin ransa yace wannan yarinyar badai naci ba

Akusa dashi ta zauna tace um Shahid nace Dan Allah ko zaka shirya muje musha ice cream?

Kallanta yayi da mamaki baisan lokacin dayace

"shahida yaushe nafara magana dake mai tsawo dahar zan debi kafa nafita tare dake? "

Maimakon tayi fishi saitayi murmushi tace Shahid yau wacce Rana kakira sunana?

Tafe kansa yayi da hannun sa, yace Dan Allah kifita daga gidan nan, bazaki gane yanda zuciyata take zafi ba idan naganki, banasanki shahida

Akwai wadda nakeso

Hawaye ne suka wanke mata fuska, cikin kuka ta tsugunna qasa tace Shahid Ina sanka

Cikin zafi yace nikuma Bana sanki

Kafafunsa takama ta riqe, yafizge kafarsa, tareda Kai hannu zai dauketa da mari

Okasha ne yafuto Dasauri, wanda yaji suna rikici cikin daga murya, hakanne yasashi futowa

Yace haba Shahid?

Dukan mace?

Yadubi shahida yace shahida tashi ki tafi, insha Allah komai zaiyi normal kinji?

Kai ta daga masa tana goge hawayen idonta

Tana fita okasha yace abokina meyayi zafi haka?

Yarinyar nan tana sanka, koyayane kadinga kulata zataji dadi, be kamata irin haka yadinga shiga tsakanin Kuba

Okasha nafada mata banasanta, Bana Santa okasha, Yaya take so namata?

Har wannan yarinyar ce zatasa hannu tace zata riqeni?

Nawa ma take, Amma har tasan tana taba Jikin maza

Ahakan zan sota in aure ta?

Okasha ya kalleshi yace Amma na tabbatar ayanda kake bamu labarin Amal, abinda yafi riqewa ma kayi mata, shin ita Amal din muharramarka ce?

Amal da shahida duk daya suke awajanka, zaka iya auren kowa acikinsu

Amma Okasha...

Dan Allah kayi shiru Shahid, kadena kokarin dukan mace ko Yaya take Dan Allah

Shahid yana huci yashige daki, okasha bai taba yima sa fadaba Sai Akan wannan jarababbiyar yarinyar, tayaya zai sota?

*** *** ***

After ten day's

Zabe yarage saura kwana biyu, kullum daddy baya gida, dagani Sai mai gadi, haka nayi ta zagaye gidan yau ni kadai, naci abinci nakaiwa iliya mai gadi, acan nayi zamana mukasha firar mu

Hannu na ya dade da warkewa

Da yamma nayi wanka nasa Riga da sket dinkin Jan less sosai nayi kyau acikin less din, yakarbi fatar jikina, hips dina sun futo sosai, haka rigar ma Ana iya hango albarkatun qirjina

Kawai nishadi nakeji yau, kuma nakira Yaya Shahid bansameshiba, na zauna afalo na kunna kallo, kamar wasa nace ke bari de yau inga menene adakin nan da daddy yake shiga

Dakin natura nashiga, da photunan ta nafara tozali, tsayawa nayi Ina kallan Dakin, ko Ina photunan salma, kan gadon na kallah Naga Rigar baccinta akai, kenan nan yake zuwa yayita kallan pictures dinta, ya rungume rigar baccinta

To tayaya ma zai kulani,? Nan take naji wani qullulun baqin ciki araina

Aigara ni rayaiye nakeso, shikuwa Akan matacciya yakasa dubani, bai damu da cina da shana ba, kamar an ajiye masa gunki

Hararar photon nayi, afili nace Allah yaji qanki de

Computer nagani agefen gadon nasan tasace, Dan haka nadauka Nakai falo, nacire dankwali na, naci damara dashi, nakwashe pictures din duka Nakai dakina, naduba ko Ina, banbar komai nataba

Tas nakwashe komai nakaishi dakina, inata fada, ni za'a renawa hankali, nan gaba Naga inda zaka dinga shiga

Computer nadauka nahau sama, Nakai masa ita dakinsa, wannan ne Karo nafarko dana shiga Dakin, komai na Dakin red ne, Dakin yayi mugun tsaruwa kamar ba Dakin namiji ba

Akan bedside drawer na ajiye computer

Kallan Dakin naci gaba dayi, anan Naga pic dinsa babba, yasaka suit, yana daria, sosai photon yayi mugun kyau

Agefen gadonsa Naga wani Dan qarami, shikuma na salma ne, afili nace, afili nace, bacci salma, Rana kana Dakin salma, tayaya za'a kalli Amal?

Photon nadauke nasauko qasa dashi, ina Tafe Ina sababi, nasan tunda nace masa idan yaci Zabe yasakeni nasan zai sakeni, tunda naji yayi shiru, Amma Kuma mutum ma ai rahma ce, duk da zai sakeni Bayan zaben ai ko gaisawa yaci ace munayi

Amma muna zaune zama kamar Zaman gaba, inata magana ta afili Shima pic din nasake kaishi dakina

Dirin motarsa naji, Dan haka nacire dankwali na daga da marar danaci, nariqeshi ahannu na

Ribbon din kaina nacire gashin kaina yabazu har Saman kafaduna

Yarfe hannu na nafarayi me ciwon inajin Bude kofar falon, Nakai kallo na gareshi

Shima din niyake kallah, shi wallahi Yama manta da yarinyar saboda harkar Zabe dayazo kusa, mekuma yasamu hannun nata?

Kallansa tayi yayi kyau sosai cikin manyan kaya farare

Ahankali tataka taje kusa dashi tana Yarfe hannun, ta miqa masa ribbon din Hannunta red color, kalar kayan jikinta

Tace Dan dauremin gashi na, hannu na ciwo yakemin

Idanunsa masu fizgar yanmata yazuba mata, Lalle ma wannan yarinyar

Yasan cewa da Allah yabashi haihuwa da wuri shida salma da tuni sun haifeta

Amma saboda yarinta shi zata renawa hankali tace masa ciwon ta kusan 1 month har yanzu bai warkeba

Kode jitake Shima Yaron ne kamar ta?

Comments dinku yana qaramin qwarin gwiwa

Please share

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

14

Alama yayi Mata da kansa alamun ta matsa, zuba masa ido tayi ga ribbon ahannun ta, qara kawar da Kansa yayi alamun ta bashi waje, fuskar nan babu alamun wasa, tuni yayi Mata kwarjini, taja gefe guda tabashi waje

Da kallo tabishi harya haura sama,ko juyowa baiyi yasake Kallanta ba, haushi yasa tayi jifa da ribbon din Hannunta

Idanu ta zaro afili tace photunan matarsa

Ai aguje tayi dakinta, tare da kulle wa

Tafada kan gadon tana maida munfashi

Yana shiga dakinsa, yacire babbar rigarsa ya kwanta kan gadon yayi shiru yana kallan sama, daga baya yashiga toilet yayi wanka, jallabiya yasaka yasauko qasa

Dining ya kalla wayam Babu komai, wannan yarinyar Bata iya komai ba Sai shirme, antashi an aura masa wadda ko girki Bata iyaba

Juyawa yayi yashiga Dakin salma, tsayawa yayi yana kallan Dakin ganin komai yasauya

Acan Dakin Amal kuwa ta labe ajikin kofar Dakin, tana jiran sammaci, taji ya bude Dakin salma

Cikin bacin rai afili yace wannan yarinyar!!

Futowa yayi yazo Dakin ta, yatura yaji kofa gam arufe, qwanqwasawa yayi, tana jinsa tafara matsawa dabaya ahankali, sake qwanqwasawa yayi, tadaga murya tace Yaya daddy wasa nake saida safe

Kallan kofar Dakin yayi kamar ita yake kalla, tasan meta aikata ai dole ta rufe daki

Dakinsa yakoma, Idanunsa suka sauka Akan computer sa, kenan harnan tashigo, Lalle zai gamu da yarinyar nan

Computer yadauka yafara dube dube, wayarsa tadau qara dauka yayi tare da fadin jb ya akayi

Kai kuma shikkenan daga aure shiru ake jinka, wato kasamu sweet 18 ko

Girgiza kansa yayi ransa abace kamar jabeer din yana ganinsa, yace idan kasamu time kazo, katahomin da abinci a restaurant, yakashe wayar

Jb ya kalli wayar da mamaki

Shima anasa bangaren rufe computer yayi ya kwanta yafada duniyar tunani

Nikuwa kan gado nafada nasaki daria, afili nace hauka nake zan bude ka dakeni

Wayata na dauka nakira maisah, Bayan mun gaisa tacemin Ina oga, da fatan de komai lafiya?

Nace wacce lafiya maisah, nifa kinga Bama magana har yanzu, maisah zan iya cemiki tunda nazo gidan nan maganar arziqi Bata taba hadani dashiba,

Ajiyar zuciya maisah tayi, tace Anya Amal kina yiwa mijinki biyaiya kuwa?

Maisah wacce biyaiya sakinafa zaiyi

Subhanallah me kike fada haka Amal?

Shidinne da bakinsa yace zai sakeki?

To ai nafada masa idan yaci Zabe yasakeni na auri Yaya Shahid

Yasalam, Amal kanki daya kuwa? Mijinki kike cewa yasake ki Amal? Shin idan yasakeki kina tunanin baba zaiyi farin ciki da hakan ne?

Ke kanki idan yasakeki yamayar dake qaramar bazawara, ba Shahid kadai ba, a'idon kowama ke bazawara ce ba budurwa ba

Amal ki dawo hankalin ki, ki riqe aurenki dakyau, kede kifita haqqinsa, shi idan yasauke haqqinsa kansa, idan bai sauke ba yayiwa kansa

Nasan yanzu irin Dan Jan hankalin nan ma namata bakya yi Amal

Jikinane yayi sanyi dajin kalaman maisah, cikin sanyi jiki nace maisah wallahi inayi

Dazu ma haka nabashi ribbon nace masa hannu na yanamin ciwo ya daure min kaina, Amma shine ko arziqin magana bansamu ba, qarshe ma alama yayimin dakansa inmatsa tun kafin ya gabjeni

Maisah batasan lokacin datasa daria ba, tace Lalle Amal, to ai haushin dakika bashi ma kadai zaisa yakasa kulaki bare yayi miki magana, koni nan nasan ciwonki ya warke Amal, bare shi

Haka ake Jan hankalin?

Ki tashi tsaye ki gyara rayuwar aurenki Amal

Kidinga yimasa abinci, ya siyo abinci yakawo Amma saide kiyi kuci keda mai gadi

Shi ko oho

nace maisah idan nayi ma bazai ciba, tace kintaba yi ne yaqi ci?

Nayi shiru, tace yakamata de ki gyara, Dan gyaran Dakin nan, dayi masa magana ko bayaso, nide BURINAH shine inganki keda daddy Kuna shimfida soyaiya, kunyi bala'in dacewa da junanku Amal

Ina daria nace maisah soyaiya... Nide nagode Sai anjima

Ina kashe wayar, nafada duniyar tunani, maganganun maisah gaskiya ne, saide wannan mutumin kome nayi Bana tunanin zai Kalle ni, amatsayin mace, tunda tunanin matarsa bazai barshi ba, Amma Kuma aita mutu, yanzu nice matarsa, gaskya de dole insake taku

Yana kwance adakinsa, jb yashigo, ya ajiye masa take away yace na shigo inata sallama babu kowa agidan ne?

"tana nan"

Abinda yace kenan

Jb yace to meke faruwa yau din, baka samu abinda zaka ci agidan ba?

Ajiyar zuciya yasauke, yatashi daga kwanciyar dayayi, yace jb idan nakama yarinyar nan Sai jikinta yagaya mata

Subhanallah daddy meke faruwa ne?

Tashiga Dakin salma takwashe min pictures dinta gaba daya, tashigo dakina tadaukemin Wanda suke nan

Yaushe nafara wasa yarinyar nan jb?

Ajiyar zuciya jb yasaki, cikin ransa yace alhmdlh Zaman lafiya yakusa fara wanzuwa

Afili kuwa yace haba daddy kayi mana kasan fa yarinya ce

Nikuwa nasan yarinya ce jb

Dazu fa....

Saikuma yayi shiru, yaci gaba da fadin ni ban iya ko dafa shayi ba, kullum Bata bani abinci, narasa aure akamin kokuma Reno aka bani, kawai jb Bayan Zabe zan saki yarinyar nan

Dasauri jb yace Lalle daddy bakada hankali, karma kafara

Nagaji da Zaman Dakin Dan haka na futo falo domin infara gyarawa kamar yanda maisah tabani shawara, nagama shara Ina mopping naji takunsu, ina daga Kai mukai ido hudu dashi, ai aguje nayar da moper nayi daki jikake garam narufo kofar

Me jb zaiyi inba daria ba, wannan gida akwai drama

*** *** ***

Washe gari Ina zaune afalo iliya mai gadi yazo yace Ana sallama Dani awaje, Dan qaramin hijabi na saka iyakarsa qirjina, ina futowa harabar gidan Naga wasu

mutane su biyu, har rissinawa sukayi suka gaidani, nide nacika da mamaki, sukace ranki yadade anbamu umarni ne azo ayi Miki voters card

Araina nace ikon Allah

Nace to bissmillah, kujera iliya yadauko akayimin abuna, Babu Bata lokaci aka yi aka ciromin abina, dazasu tafi nace ku tsaya, nashiga ciki Dasauri nadauko musu ruwa da lemuka nace gashi kwasha ahanya banbaku ruwaba har zaku tafi, fuskar su dauke da fara'ah sukamin godia suka tafi

Suna fita daya yadubi dayan yace gaskya maigida yayi sa'ah, kaduba kaga yar qarama da ita Amma Babu girman Kai babu komai harda bamu abinsha, dayan yace eh gaskya wannan dole yaboyeta, kwanaki naji wasu samari suna cewa ba'a taba ganin matar daya sake aura ba

Kaikuwa me wannan dalleliyar matar Ina zai bari aganta? Dayan yace hakane Kam

Ina komawa ciki, na ajiye katin zaben Akan kujera nafada kitchen saida nasake gyara kitchen din sannan nafara girki, qamshi yacika ko ina, jallof din couscous nakeyi dayaji kayan lambu da nama, ina gamawa najera komai yanda yadace nadawo daki nayi wanka nakwanta

Wayata nadauka Ina game, in shiga nan induba nan har bacci ya daukeni

Cikin dare kamar Wanda aka tsikara natashi, naduba wayata Naga karfe uku daidai

Maganar anty mufy ce tafadomin, tsam natashi nayi toilet nadauro alwala nazo nafara gabatar da sallah, bansan ya akayi ba nide nasan na tsinci kaina dayiwa daddy addu'ah akan Allah yabashi nasara Akan zaben da zasuyi

Ban kwanta ba Sai da akayi sallar asuba, bacci na nake hani'an, har karfe goma da rabi, ina farkawa natashi Dasauri nashiga toilet domin wanka

*** *** ***

Yana shiryawa cikin manyan kaya yadi mai kyau da tsada launin light blue, wayarsa tadau qara, yana picking Abba yafara fada yana cewa Ina kuka tsayane har yanzu banga an nuna agidan TV kaje kayi zaben ba?

Kaida yakamata ace tunda wuri kunje kun dawo, tomude munje, kadau matarka kukama hanya kutafi, inkuma yanzun ma nunamin zakai bakasan siyasar ka watsamin qasa a ido Toshiknn

Saura kuma Kasa wannan qananun kayan naka kaji

Yana gama fadansa yakashe wayar

Kallan wayar daddy yayi, Wai Abba ya yakeson yayi ne? Shi wallahi baisan hayaniya, kallan kansa yayi, yace danma nasa manyan kayan de

Fita yayi daga Dakin cikin sauri, har yaje zai fita saikuma yadawo, yatura kansa cikin Dakin Amal

Alokacin tana gaban mirror tana kwalliya, kanta ko Dan kwali babu, tsayawa yayi daga bakin kofar Dakin yana Kallanta, Gaba daya tagama diriricewa, jambaki ta dauka tasaka launin ja adan qaramin bakinta, cikakken gashin girarta ta taje, tadauki mascara tana taje Zara zaran gashin idonta

Yakafeta da ido yana Kallanta, Gaba daya jikinta yayi sanyi, takasa kuzari, shigowa Dakin yayi yana zagayawa, addu'ah take aranta Allah yasa karyaga pictures din salma

Yana zagayawa har yazo saitin inda take tsaye, kallansu tayi amadubi taga yazuba mata ido, Babu um bare um um

Dasauri ta dauki ribbon dinta zata daure gashin kanta, taga ya kalli agogon dake daure a tsintsiyar hannun sa qirar Gucci

Yaga tana neman Bata masa lokaci Dan haka yasa hannu zai karbi ribbon din, hannunsa ta kalla duk gashi ya kwanta ajikinsa, Dasauri tasaki ribbon din

Karba yayi yadawo Bayanta har tana jiyo hucin numfashinsa, ahankali yakana gashin kanta yafara daurewa

Ido tazuba masa ta mirror tana kallan yanda yake daure gashin, fuskar sa atamke kamar tayi masa dole

Yana gamawa yayi hanyar fita

"zomu tafi"

Kamar amafarki taji maganr sa, karfin Hali tayi wajan fadin Ina zamu je?

"nace kizo muje "

Daga kafadunta tayi tace to

Mayafin doguwar rigar jikinta tayi sauri ta dauka tayi rolling, tayi mugun kyau

Tana futowa falo taga baya nan, kayanta ta kalla tasaki daria, tace yaude munyi iri daya da daddy kamar hadin baki

Tana fita harabar gidan taga yashiga Mota, Dasauri tabude gaban motar tashiga

Tashin motar yayi suka fara tafiya, sunyi Nisa kadan suna shiga jama'ah

Ya kalleta, yakawar da kansa, tissue din gaban motar yadauka ya miqa mata

Kallan tissue din tayi, Babu alamun wasa afuskar sa

Dan haka takasa tambayar sa, Tasa hannu takarba, kamar bazaiyi maganaba Sai can yace

" goge abin bakinki "

Sake kallansa tayi, ahankali ta yagi tissue din ta goge jambakin datasa

Motarsu tana dosar wajan mutane suka cika wajan danqam, yanayin parking yafuto 'yan jarida da gidan TV suka fara daukarsa, yafara tafiya kenan, wayarsa tadau qara yana dagawa Abba yace katafi kabar yarinya abaya, daddy banasan shirme fa

Kallan sa yakai kanta, yazuba mata ido, wato daga zuwan sa har andauka Ana nuna shi agidan TV su Abba suna kallansu dayake live ne

Hannunsa yakai kan nata, ya riqe ta suka fara ratsa jama'ar wajan suna shiga, tako'ina jinake qyas qyas qaran camera

Basu bi layiba aka tantance su, sukaje aka basu ballot paper suka dangwala, idanunta Akan takardar hannunsa, duk abinda taga yayi itama shi tayi, yana gamawa jama'ah suka fara yimasa tambayoyi yana amsawa

Dakyar yasamu yafuto still hannunsu yana sarqe dana juna

Saida suka zo gab da motar sannan ya fizge nasa hannun, kallansa tayi tasakar masa harara afakaice, suka shiga Mota suka tafi

*** *** ***

After one week

Sakamakon Zabe ya bayyana inda daddy yayi nasarar lashe zaben jihar, saboda jama'ah masu taya murna gidan Abba muka koma

Kasancewar momy tana cikin farin ciki ko kulani ma batayiba, saide duk inda ka duba social media pictures dinane yake yawo New first lady,, new first lady

Su baba sunkira Abba sun tayashi murna sosai shida umma

Saida komai yalafa su Momy juwairah suka koma government house, yayinda daddy yace baya buqatar Zaman gidan, saide lokaci zuwa lokaci muna zuwa

Wani lokacin kuma zai barni agida ni kadai shikuma yaje can Sai wajan dare yadawo gida saboda ayyukan dasuke gabansa

Bayan an rantsar dasu ne yafara gabatar da aiki gadan gadan tareda temakon mahaifinsa, inda yake qara dorashi Akan hanyar data dace

Doka ta farko daya fara kafawa itace duk wani Wanda zai hau machine to doka ce yasaka hular kwano akansa, saboda matsalar qwaqwalwa da ake yawan samu idan hatsarin machine yafaru

Amma idan da ita abin zaizo da sauqi

Tunda yafara gabatar da mulkinsa baya zama yau shine can gobe can, yau meeting gobe zuwa ziyara asbiti saboda ganin marasa lafiya

Yau shine Bude wannan taro gobe shine barin qasar, Gaba daya ya hauka ta jihar da ayyuka

Nikaina saina dade ban ganshi ba, haka ce taci gaba da faruwa har zuwa tsawon wani lokaci mai tsawo, saide inkira su umma ko maisah musha firar duniya kokuma Yaya Shahid yayita sakani daria hakan ne yahanani Zaman kadaici

*** *** ***

Yanzu shahida menene abin damuwa Dan zaki rabu da wannan gayen?

Bazaki ganeba jamcy wallahi Ina sansa Amma yakasa fahimta ta, to tunda yakasa basai ki rabu dashiba

Toshiknn jamcy insha Allah zan gwada hakan

tunda ga lokacin shahida tadena kula Shahid, ko hakan zaisa ta manta shi, saide hakan bai samu ba asalima qara kaunar sa take

Bayan wasu watanni suka kammala karatunsu lafiya, suna karbar results dinsu alhaji sidi yaturo musu kudin jirgi

Shahid ko neman shahida baiyi ba, haka suka hau shirin tahowa nigeria shida okasha da nazy

Ko yan gida bai fadawa zaizo ba yafison yayi musu surprised

Yau suka sauka a Nigerian saida suka huta dukansu a gidansu okasha sannan Shahid yayi hanyar jigawa, nazy kuma yayi hanyar bauchi

Shahida kuka Tasa lokacin dataji labarin su Shahid sun tafi, ta kuma tabbatar Bata gaban Shahid,kuma batasan inda zata sake ganinsaba,

hakan ne ya kwantar da ita jinya, inda sukaje asbiti aka tabbatar musu dacewa tana dauke da hawan jini

Babu yanda ta iya, itama tana karbar result dinta, ta tashi hankalin jamcy Akan su hada kayansu su dawo nigeria

Daga ranar suma suka fara shirin dawowa gida

(gaskya babu abinda zance da masoyan wannan littafin nawa sai godia, Facebook fan's da wahtsp dakowa dakowa Ina godia harda masu Bina ta privet chat, duk Ina godia tare da miqa saqon gaisuwa ta agareku)

Karku manta da

Comments

Share

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

15

Befi 2 hours ba yayi ahanya, yasauka agarin maigatari, kallan yanayin Garin yayi, an Dan same canji ba kamar bayaba, har kofar gida mai motar daya kawo shi yakai shi, kafin yashiga saida yaqarewa gidan kallo, yana Nan yanda yake komai kalau, harma sabunta fanti da akayi

Baba hamani akwai riqon alqawari bai lalata wannan gidan ba, yasan hakanne ma yahana mai gidan tashin su

Mai motar yasallama yakwashi jakunkunansa, yayi cikin gidan, da umma yafara tozali

Tana harhada kayan abincin dazata dora

Yana ganinta yazubar da jakar yatafi da gudu ya rungume ta

Umma tace Shahid? Kaine? Kaine Shahid?

Shikuwa daria ma tahanashi magana, umma ta qwalawa baba kira

Malam! Malam!! Futo ga Shahid

Baba hamani yana futowa Shahid yahadasu duka ya rungume su, Gaba daya suka rasa inda zasu saka shi Dan murna

Umma barin dora abincin tayi, suka dawo falo, aka Bude babin fira, baba yace meyasa baka fadamana zaka zoba, aida na shirya da kaina naje nadauko Amal munje har filin jirgin mun dauko ka

Cikin ransa yace baba kenan, har yanzu de yana Nan yanda yake, inba hakaba yarinya agidan mijinta kaje ka dauko ta, saboda zan dawo

Afili yace baba ai so nake nayi muku bazata, umma tace ai Kam munga bazata, bari inje in dorama dana abinci,mekakesan ci Shahid din umma? baba ne yace dakata samiya, bar abincin nan

Yanzu zan fita naje nasiyo kaji ayi masa farfesu

Tashi kaje kayi wanka kahuta Shahid

Yana murmushi yace to baba, yatashi yayi ciki

Bayan yayi wanka yana kwance a dakinsa umma tace yataso farfesu yahadu, yace to umma ganinan, yafuto kenan zai wuce Dakin Amal kawai saiya tura yashiga, Dakin ya kalla yana Nan yanda yake, duk tarkacanta suna nan aciki, Murmushi yasaki yace Amal din baba da Yaya Shahid Ina Nan tafe inzo inganki

Yana fadar haka ya wuce falo, yaci abinci, suna zaune dukansu baba yace shahid meyasa tun farko baka fadamin gaskiyar abinda kakeji game da yar'uwarka ba?

Sosa kansa yayi yace baba ai Amal yarinya ce, nabari ne in gama karatu tukunna

Jinjina Kai baba yayi yace hakane, Amma ni banji dadin wannan shirun nakaba, Naso ka auri Amal, BURINAH inganku Koda yaushe cikin farin ciki kaida yar'uwarka

Shahid yace baba ai babu komai haka Allah yatsara ikonsa, ubangiji Allah yasa hakane yafi alkhairi

Baba da umma suka hada baki wajan fadin amin

Baba yace ai mijin nata ma kwanaki yaci Zabe, shine gwamnan Garin nasu, Shahid yace da gaske baba?

Yace wallahi kuwa, suna can bauchi suna Fama da jama'ah . shekaran jiyama mijin nata ya aiko mana da takardar fili babba acan Bayan Gari, yace zai turo afara ginawa mu koma sabon gida, baisan wannan din dama na aro neba

Cikin murna yace kai Amma ya kyauta, Allah yasaka musu da alkhairi

Allah yatayasu riqo baba, Nima idan nahuta insha Allah zansa time inje in ganta

Umma tace eh gaskya yakamata Kam

Yanzu ma bari nakira ta awaya inyi mata albishir

*** *** ***

Ina zaune afalo ni kadai duk kewa ta dameni, yau kwanana biyu rabon danasa daddy a'idona, kafin yadawo nayi bacci, shikuma idan yadawo baya nemana

Abinci idan nayi wataran yaci wataran kuma yanda na ajiye haka zanje na dauke

Yanzu ma nagama jera komai a dining table, jira nake yadawo inde beci ba to wallahi nadena wahalar da kaina Akan yi masa abinci

Wayata ce ta dauki qara, cikin shagwaba nace umma Dan Allah kizo naganki, kokuma ni nataho

Ke rufemin baki shashasha kawai, ga yayanki

Daskarewa nayi a zaune wanne yayan nawa? Mamaki nane yakatse da naji muryar Yaya Shahid adodon kunne na

Ihun murna nasa nace Yaya Shahid Dan Allah Kaine?

Wayyo Yaya yaushe kadawo? Shine Koka fadamin ko?

Shigowarsa kenan daga waje, yayi kyau sosai cikin suit me launin blue, sosai ta karbi fatar jikinsa, ya tsaya yana kallan yanda take hauka awaya

Amal kuwa waya take zuciyar ta daya, yanzu yayanah me Dame kakawomin? Daga bangaren Shahid yace zanzo da kaina inkawo miki tsarabarki, cikin zumudin murna tace

Allah yaya Shahid? Amma naji dadi sosai wallahi, I miss you muahh, tasakar masa kiss ta wayar

Gabansa ne yafadi, yayinda qirjinsa yake masa wani mugun zafi, azuciye yaje zai karbe wayar saikuma yafasa, ya haura sama

Amal tana ganin giftawar sa tace tooo yau kuma dawuri aka dawo kenan

Taci gaba da wayar ta, baba ne yakarbi wayar yace Amal din baba, tace na'am baba

Yace bawa mijin ki waya zanyi masa godia, tace godia kuma baba?

Baba yace nace kikai masa ko, ahankali ta tashi tace to baba

Saman tahau, ta tura Dakin ahankali kamar marar gaskya, yana qoqarin cire suit dinsa tashigo

Juyawa yayi, yazuba mata ido, cikin in Ina tace am, dama waya ce baba yace nabaka

Tafadi haka tare da miqa masa wayar

Sallama yayi ahankali, cikin ladabi yagaida baba, Amal ta zuba masa ido tana kallan yanda yake motsa bakinsa yana magana kamar bayaso

Godia sosai baba yayi masa, daddy aransa yace yasan aikin Abba ne wannan Dan shide beyi musu komai ba

Yana kashe wayar yajuyo yamiqa mata, takawa tayi taje gabansa zata karba ya fuzgota har saida ta tsorata tayi yar qara

Dab da fuskar ta ya matso da tashi fuskar, cikin bacin rai da daga murya yace Ina kikaimin photon matata?

Tsorata tayi da yanayin sa nan da nan jikinta yahau rawa, tace ai.. Ai de zan dauko Maka abinka ko?

Cikin ransa yace dade yafi, Dan bazaki kwashe min photunan matata ke kije kina waya da wani qato ba

Sakinta yayi tayi hanyar fita aguje, taji yace zoki dauke wannan wayar daga kusa Dani tun kafin nafasa ta

Cikin tsoro tace toka ajiye mana saina dauka

Bazaki zo ki dauka ba?

Yafadi hakan cikin fishi

Itama cikin rashin kunya tace nace Maka ma ajiye ha'a

Batai tsammani ba taga yayi Mata jifa da wayar, yashige toilet cikin qunan rai

Amal ta dubi yanda wayar tayi daidai asaman tayils din Dakin, Dasauri ta tsugunna ta kashe, ta harari kofar toilet din, aranta tace mugu kawai azzalumi

Tayi waje

*** *** ***

Tana shigowa falon, security suka fara shigo mata da kayanta

Dasauri ta rungume mahaifiyar ta, momy tace oyoyo my daughter

Shahida tace momy driver yana daukoni Naga yakawo ni nan gidan ashe hardamu aka dawo

Momy tace eh anan muke shahida ta, momy Ina Yaya daddy?

Yana gidansa, ba Koda yaushe yake zama anan ba

Meyasameki Naga wannan zuwan kin rame haka? Momy babu komai fa kawai missing dinku ne, Abba ne yashigo shahida tace abbanah

Da murnar sa yace a a kaga auta andawo gida ko,? Yaya karatun to da fatan de angama lafiya? Lafiya Abba, to Allah yabada sa'ah tace amin

Momy ta kalla tace momy zanje inyi wanka nahuta, tashi momy tayi da kanta takaita har sabon dakinta sannan ta futo

Shahida na kwanciya zazzafan zazzabi yarufeta, har dare momy taji shahida shiru taje ta tarar da ita ba lafiya, dama tasan yarinyar nan batajin dadi Amma tace Wai missing dinsu ne yasa

Babu Bata lokaci momy Tasa Abba yakira musu doctor, yana gama duba ta Abba yace doctor meyake damun tane?

Doctor yace wato alhaji gaskya yarinyar nan tana akwai abinda yake damunta, Tasa damuwa aranta har hakan ya haifar mata da hawan jini

Momy tace hawan jini doctor? Innalillahi

Abba yace subhanallah wato doctor dama yarinyar tana yawan jinya kawai Ina ganin za'a fitar da ita ko zuwa India ne Sai muga doctor acan

Doctor yace karka damu alhaji insha Allah muma nan zamuyi bakin qoqarin mu muga ta samu lafiya

Abba yace Toshiknn doctor Allah yasa

Momy ce tadau waya takira domin fadawa daddy halin da ake ciki

*** *** ***

Abinci nakeci afalo, Naga yafuto Dasauri yana waya, dagaji kasan ba lafiya ba, yace yanzu Yaya Jikin shahidan? Ok to to momy ganinan zuwa

Hannu na natsame daga cikin abincin Dasauri natashi tsaye jikina Sai rawa yake kamar Wanda akace qanwar uwatace babu lafiya nace

Yaya daddy Nima zan bika Inga Jikin nata

Har cikin ransa yaji dadi, duk da wulaqancin da yamin dazu hakan bai hanani duba yar'uwar saba

Shirun Danaga yayi ne yabani damar surar hijabi na, nabishi abaya, bamu zarce ko Inaba Sai daya gidan

Muna shiga nayi saurin shiga Dakin dayake na shahida, har bangaje daddy nake, kamar yar'uwata nafara tambayar ta shahida yajikin naki?

Ganin su Abba da daddy yasa ahankali tace da sauqi, Abba ne suka fita shida daddy da doctor, Nakai kallo na wajan momy nace momy yajikin nata?

Tace keee karna sakeji Kin kirani da wannan sunan ubanki ya radamin sunan ko wa?

Idanuna ne suka ciko da qwallah, Babu Bata lokaci hawaye suka sakko asaman fuskata, shahida ce ta motsa da qyar tace Dalla malama fice kibar mana daki, Dasauri nadago kaina na kalleta, kafin nayi magana momy tace bazaki tashi ki fice ba?

Adaidai lokacin daddy yashigo, harara ya zabgawa shahida, ya tsugunna dede inda nake zaune Ina kuka, hannun sa ya dora Akan kafaduna yatasheni tsaye, tare da riqo hannu na muka fice daga Dakin

Inda momy tatasa shahida agaba Akan tafada mata damuwar ta, ba tayi kokarin karya ba Nan ta shaida mata Akan Shahid ne

*** *** ***

Muna tafiya amota banda kuka babu abinda nake, wannan wanne irin cin mutunci ne? Ubana?

Yanajin kukanta Amma yakasa rarrashin ta, dazata gane data dena kukan nan saboda yanda yake taba masa zuciya

Yanayin parking na futo dagudu nayi cikin dakina Ina kuka

Futowa yayi Shima yakaiwa motar duka, meyasa momy take hakane? Whay?

Nikuwa tunda nashiga daki nakwanta nake kuka, qarshema kulle kofata nayi, ko abinci ban qara waiwaitarsa ba nayi kwanciya ta

*** *** ***

Next day

Da sassafe yashirya cikin manyan kaya, sai zuba qamshi yake yadin fari ya karbi fatar jikinsa, cikin takun qasaita yafuto already motoci sun zama ready Bude masa akayi, yashiga suka fita

Saida sukai Nisa sannan yafada musu inda zasuje, Dasauri suka qarasa babban shagon kayan wasa, yana futowa cikin sauri yashiga tun kafin mutane su taru

Mutum biyu ne suka take masa baya har ciki, cikin ladabi me shagon ya rissina yace yallabai me ake buqata?

Saida yayi Dan jimm sannan cikin sakin fuska yace kayan wasa zaka hadamin

To wanne iri kenan yallabai?

Haka teddy's da babyn roba, kagane kawai kayan wasa de na mata yarinya ce zatayi amfani dasu Bata wuce 18 year's ba haka

Me shagon yasake kallansa da mamaki gashi babu damar tambaya, cikin ransa yace ikon Allah 18 years fa

Hada musu kayan yayi me mugun yawa Dan teddy's kadai ma kusan guda hudu Akasa manya

Daya daga cikin masu take masa bayane yabada ATM aka cire kudin suka futo daga shagon

Ina zaune afalo Naga anfara shigowa da kayan wasa, da mamaki Nakai dubana kansu, cikin Raina yace to wannan kuma kosu junior ne suka zo?

Bangama mamaki naba, Naga yashigo, kallansa nake Shima niyake kallo, rabona dashi tun jiya

Kusa Dani yazo ya tsaya ya nunamin kayan wasan yace

"gashinan kidinga wasa nasan zasu debe miki kewa idan Bana nan "

Amal batasan lokacin datasa daria ba, Lalle ma daddy yarasa wazai siyowa wannan kayan saini? Shekara goma Sha tara? Daria taci gaba dayi sosai, tana daga teddy's din

Ya shagala a kallan ta, ashe tana daria haka? Ikon Allah, yasan wannan dariyar duk saboda an siyo mata kayan wasa ne, Allah Sarki andade ba'a hadu ba

Taga kayan wasa, shida yasan tana San kayan wasan aida tuni yabada order akawo mata, kodan ta dena damunsa

Koda yake ai kwanaki ma Tataba fada masa tana wasa

Cikin daria tace nagode, tafara jidarsu tanayin dakinta dasu, gaskya wannan mutumin ya mugun Rena mata hankali

Saida tashiga daki sannan yajuya yakoma dakinsa

*** *** ***

After one week

Shahid kakaiwa Amal kayan miyar nan nasan zata dinga amfani dasu, wannan kuma umma ta nuna masa wata jarka, da tsumi aciki na maganin mata

Tace kafada mata ta dinga Sha kullum kafin ta kwanta da daddare

Kallan jarkar yayi, yace umma menene aciki?

Tace banasan tambaya Shahid, tashi katafi Allah ya kiyaye hanya, Murmushi yayi yace to umma na bye bye

Yana sauka a bauchi, directly gidansu nazy yatafi, saida yahuta, sannan yakira Amal Yace tayi masa kwatancen gidan nata gashi yazo

Murna acikin Amal tace Yayanah kawai kace akawo ka government house munzo tun jiya muna nan, ok kawai yace yakashe wayar

Shida nazy suka tafi, Akan machine din nazy roba roba mai kyau, dayake nazy Dan Garin ne basu Sha wahala ba Kai tsaye suka nufi gidan

Bayin Allah basu San ansa dokar saka hular kwano ba, kasancewar suna Indonesia lokacin dayahau

Suna Zuwa gate din gidan, security suka musu kallan banza suka watsar

Shahid ne yasauko yayi masifar kyau cikin qananun kaya wandon blue jeans, da rigar ciki fara, sai yar sama ya dora kalar jeans din

Hannu yamiqawa daya daga cikin su yayi masa bayani yazo wajan qanwar sane, security din yadubeshi yace Dan samari ka matsa daga kusa Dani tun kafin bindigar hannu na tafara aiki

Shahid yace subhanallah me yayi zafi haka?

In banda renin wayo ansa doka agari kun karya, sannan kazo Wai abarka kashiga ciki

Nazy ne ya taso yace dalla malamai idan bazaku barmu mushiga ba miye na fadar magana?

Aikuwa nan hayaniya ta kaure tsakanin su

Su sukace saisun shiga security kuma suka hanasu

Yana daga dakinsa yaji hayaniya ta window yaleqa, yaga abinda yake faruwa nan yatashi yafuto da kansa, Amal ma takira Shahid yace Mata yana gate anhanashi shiga, Dan haka tafuto domin tayi musu magana

Shahida kuwa da aka tasheta a bacci cikin masifa tafuto falon

Alokacin har daddy yabada umarni abarsu su shigo gidan yaga su waye, kuma me suke nema?

Shahid kuwa yana shiga, aka nuna musu hanyar falon, iya tsaruwa gaskya gidan ya tsaru, Tako'ina sojoji ne atsaye

Yana shiga falon Amal tataso da gudu ta rungume shi tana cewa yeeee ga Yaya Shahid

Daskarewa daddy yayi atsaye, cikin ransa ya maimaita SHAHID

Janyeta yayi daga jikinsa yadago ta kenan Idanunsa yasauka Akan na shahida, yayinda nazy yacika da mamaki meya kawo shahida nan?

Dagudu Takoma daki tana kuka tana fasa kayan Dakin, komai ta Zara jifa take dashi, tana kuka

wayyo momy nashiga uku na lalace

Momy tafuto Dasauri tayi Dakin shahida tana tambayar ta menene?

Cikin kuka tace momy nashiga uku na kashe kaina!!!

Kar amanta da:

Comments

Share

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

16

Subhanallah me kike fada hakane shahida? Kiyimin bayani yanda zan gane

Momy Shahid... Shahid..

Me Shahid din yayi?

Momy Shahid yayan Amal ne, wallahi yayanta ne, gasucan afalo

Innalillahi, cikin sanyin jiki momy tace yi hakuri yi shiru, ina zuwa, goge hawayenki

Tashi ki gyara fuskarki, shahida na shiga toilet momy ta rafka tagumi da wanne ido zata kalli yarinyar nan?

Acan falo kuwa Amal ta rirriqe Shahid ahankali yace Mata bari mana, hannu ya miqawa daddy dayake tsaye yana kallansu fuskar sa babu fara'ah, Ba yabo ba fallasa yabashi hannun suka gaisa, kujera ya nuna musu yadan saki fuskar Tasa, yace Bismillah ku zauna mana

Suna zama yayi ciki,domin yafadawa momy, nazy ya kalli Shahid fuskar sa fal tambayoyi

Yana kokarin tura kofar Dakin yaji momy nacewa yauwa goge fuskar ki dakyau, kuma karki sake kuka bare yarenaki, cikin shagwaba tace to momy kome nayi Shahid bazai Soni ba, momy inaga San Shahid shine ajalina

Dasauri daddy yayi baya, dama... Kenan wannan Yaron shine yar'uwarsa take mafarki? To'ina tasanshi?

Iska me zafi ya furzar, matarsa Nason Shahid

Qanwarsa Nason Shahid, shikuwa me zaiyiwa wannan Yaron?

Abinma be tsaya iya shahida ba, harda aurensa? Bawai yanajin son yarinyar bane, Gaba dayama gani yake ya haifeta, to Amma bazai bari aci mutunci aurensa ba, yanayin komai ne saboda yakare darajar aurensa

Tsaki yasaki, aransa yace to mene ma zai dameni?

Alamun Bude kofa yaji Dasauri ya kalli wajan, Murmushi yasaki ganin momy tafuto

Da mamaki ta kalleshi, tace daddy nah, me kakeyi anan?

Cikin murmushi yace momy wannan yarinyar tayi Baqi ne shine zan fada Miki

Da fara'ah momy tace aaa to muje, muje mana, tayi gaba ta barshi abaya

Momy tana zuwa falon su Shahid suka gaida ta da fara'ah har qasa

Idanu ta zubawa Shahid, Yaron yanada kyau, dole ya haukatar mata da yarinya

Shikuwa yana futowa, kujerar da Amal ta zauna yaje Bayan kujerar ya tsaya, hannayensa cikin aljihun wandonsa

Yana kallansu, yarasa meyasa yakeji aransa yaran nan suyi suyi sutafi

Amal cikin dar dar tace momy ga yayanah Yaya Shahid, momy tace Allah Sarki, aikuwa ga kama nan, ta dubi Shahid din tace yasu umman naku?

Amal tacika da tsananin mamaki

Shahid yace suna nan lafiya, sunce agaida ku

Daddy kuwa kallansa yake, cikin ransa yace babu laifi Yaron yahadu ba qarya

Ganin yanda gaba daya hankalin Shahid yana kan Amal ne yasa ahankali yadawo kujerar da Amal take zaune yazauna dab da ita, cinyarsu na gogar tajuna, ta Bayanta yakai hannun sa ya rungumota kadan zuwa jikinsa

Gabanta ne yake faduwa, me Yaya daddy yake shirin yi ne haka?

Kallansa take yayinda Shima yazuba mata ido kamar yau ne Karo na farko dasuka taba ganin juna

Cikin murmushin daya mutuqar saka Amal mamaki yadubeta yace

"kinata surutu baki kawo musu ruwa ba? "

Kallansa tasake yi sosai, takasa magana, yau daddy ne yariqeta haka Kamar wani masoyin da za'a qwace masa budurwa?

Tashi zanyi momy cikin sauri tace a a Amal yi zamanki, nan tafara qwalawa me aikinsu kira

Raliya!

Raliya!!

Dasauri Raliya ta futo tare da rissinawa,

momy tace Raliya me kike haka kika bar baqi babu ruwa babu drinks?

Yi hakuri hajiya, bari akawo

Tana juyawa shahida tafuto, fuskar ta babu yabo babu fallasa, ta zauna kusa da momy

Kallan su Shahida tayi kamar ba itace tashiga da kuka ba, sannun ku da zuwa, Shahid kamar bai santaba agajarce yace yauwa

Cikin ransa yace

Meyasa meta duk ta rame haka?

Nazy kuwa daya Kasa boye mamakinsa yace shahida ashe anan kike?

Da murmushi afuskar ta tace nazy anan nake

Amal da aka yiwa dabaibayi cikin mamaki ta dubi Shahid tace yayanah? Dama kunsan juna ne?

Murmushi yasaki yace nasanta a school dinmu

Amal tace ok,Allah Sarki ai ban taba saniba

Shahid qara kallan daddy yayi yanda yawani qanqame Amal, kana kallan qwayar idonsa zaka hango kishi qarara, baisan cewa shi yariga yadau qaddarar saba tarashin Amal, kawai de qanwar tasace bayaso, kuma shi soyaiyar nan de ba ayi dole

Raliya ce tafara jera kayan motsa baki, Babu Bata lokaci gabansu Shahid yacika da sinadarin sanyaya maqoshi

Zata fara zuba musu shahida tace barshi Raliya

Ahankali tataka har inda suke ta miqawa nazy, yace thanks shahida

Shahid ta zubawa ta miqa masa, yazuba mata ido, kamar bazai karba ba saikuma ya basar ya karba baice mata uffan ba

Suna Sha momy tace Shahid Amma ai anan zaku kwana ko?

Gaban daddy ne yafadi, kwana? Kuma anan gidan? Ko dayake aiba damuwa tunda su sunada wani gidan

Shahid yace a a hajiya yau nakesan komawa jigawa insha Allah, tace Toshiknn Amma kashirya next time idan kadawo anan zaka kwana, Shahid baice komai ba Sai murmushi

Amal tace yayanah, Ya baba yake? Dafatan de yanzu Yadena rigimarsa ko?

Shahid yace a a yana Nan ai saide in ba'a taba Kiba

Gaba daya sukasa daria,shida ita

shahida kuwa wani irin dadi takeji yau Shahid a gidansu

Saqonta yabata yace gashi mu zamu wuce, Dasauri ta tashi, Dan dama amatse take da wannan Zaman na daddy agefenta

Momy ce tayi ciki Dasauri, shahida ma tabita

Amal tace Yaya muje na rakaka,hannu suka miqawa daddy dukansu sannan suka fita

suna fita daga falon yatashi yakoma Jikin labulen window yanda zai dinga kallansu

Momy tabawa ma'aikatan kaya masu yawa tace abawa su Shahid, kayaiyaki ne su atamfa da less masu tsadar gaske, na umma Sai kuma turare na baba

Sai nashi agogo mai shegen tsada da shadda

Da farko Qin karba yayi, saida Amal tace ya karba, tace yayanah Dan Allah ka gaida su ummatah, Kallanta yake da murmushi yace zasu ji, but Bama Lalle na samesu ba Dan sunce zasuje kano gidansu okasha su yiwa mahaifinsu godia, Amal ta eh gaskya Kam yakamata, Nima ai nakusa zuwa Yaya

Daria yasa yace ke kina cikin wannan sojojin inake Ina fita, yauwa namanta acikin saqon ki umma tace akwai wani magani kidinga Sha da daddare kafin ki kwanta, bansan kona mene ba na tambayeta taqi fadamin, but inaga de na tsari ne baba yayi miki

Dan Naga alama wannan gidan naku saida neman tsari, idan aka sako mutum a gaba da naci

Kallan rashin fahimta tayi masa, tace Yayanah, me kake nufi?

Da murmushi afuskar sa yace nida masu gadin can nake

Sakin Fuskarta tayi tace ok, juyowar dazatayi tayi ido biyu da daddy dayake tsaye ajikin window, da kansa yayi Mata alama data dawo ciki

Allah yaso Shahid bai lura ba, Dan haka sukai sallama cikin sanyin jiki tadawo ciki

Tana zuwa falon anan taganshi yana aikin zageye falon, Kallansa tayi fuskar sa tadawo kamar da atamke

Tashare shi tashige dakinta

Saida yaga shigarta daki sannan Shima yakoma dakinsa

Da daddare Amal tafuto zataje kitchen tasamawa kanta abinda zataji, tafuto da flate din ahannun ta, saiga shahida, cikin ranta tace shahida ganinki ba alkhairi ba, Shahid ta zauna dab da Amal, Amal kuwa ta dauke abincin ta zata tafi daki,

Riqeta tayi tace Amal, magana zamuyi

Cikin dakiya Amal tace inajinki

Amal Dan girman Allah kiyafemin, haqiqa nasan nabata miki abaya, Amma kuskure ne da aikin shedan Dan Allah kiyi hakuri ki yafemin

Amal inasan yayanki tun muna school, Amma baya kulani, baya sona, kuma baya qaunar ganina Amal, Amma Naga tsantsar soyaiyar ki acikin Idanunsa, idan kikai masa magana nasan zai Soni

Amal kokin San a dalilin qaunar yayanki nashiga wannan halin? Nakamu da ciwon hawan jini

Riqo hannun Amal din tasakeyi cikin kuka tace Dan Allah Amal

Amal da mamaki yacika ta cikin haushi da takaici ta Fizge hannun ta, har hakan yayi Sanadin faduwar flate din Hannunta tace shahida me kike ce?

Yana dakinsa yaji qara Dan haka Dasauri yafuto, yanayin daya gansu aciki ne yasan cewa babu lafiya Dan haka yaja yatsaya yana kallansu daga nesa

Amal tace kin manta cin mutuncin da kikamin shahida? Har gida kika debo kawayanki kukazo kuka tozartani

Shahida cikin kuka tace Amal.....

Itama Amal din kukan Tasa tace Dan Allah kimin shiru shahida bakida abinda zaki fadamin, tajuya dakinta da gudu tana kuka, yayinda shahida ta tsugunna awajan tana wani malalacin kuka

Yana gama kallansu yaja kofar dakinsa yarufe, yafada duniyar tunani

*** *** ***

Suna zaune adakin Abba momy tace alhaji yaufa baqi mukai bakanan yayan Amal yazo tareda abokinsa, Amma Kuma hajiya kukasa sanar Dani?

Kama hannayensa tayi tace alhaji kayi hakuri aikasan baka Gari, sannan banasan katse Maka ayyukan dasuke gabanka, Abba yace eto hakane kuma, to dafatan de babu damuwa sun koma kalau ko?

Tace alhmdlh sun koma lafiya, Amma Kuma saide akwai matsaloli guda biyu , cikin tashin hankali Abba yace subhanallah hajiya meyake faruwa kuma ?

Alhaji jinyar shahida fa wani yaro ne take so shikuma baya Santa, sannan yau yayan Amal yana zuwa shahida tana ganinsa tace shine Yaron da take so, Abba yace tofa

Shine nace alhaji meze Hana kayiwa mahaifinsa magana inyaso ayi tuwona maina?

Abba yace hajiya idan muka bashi ita, Bayan kuma bayasanta to bamu siya mata yanci awajansa ba, ta dage da kanta da dabarar ku ta mata tashawo kansa ya amince, inyaso saina yiwa mahaifinsa magana

Cikin sanyin jiki momy tace Toshiknn alhaji, Amma wlhy ni har yanzu nama Kasa yiwa yarinyar magana, Gaba daya kunyar ta nakeji

Abba yace hakane, to kinga abinda nake nusar dake akai tunba yauba, insha Allah komai zaiyi normal, BURINAH Inga kowa de acikinsu yana cikin kwanciyar hankali

Momy tace hakane, saikuma magana ta biyu, alhaji, nifa nafara damuwa da yaran nan, Amal da daddy, har yanzu babu wani labari, shiru

Abba yasa dariyar su ta manya, yace to hajiya ya za'a musu, shi yanzu daka tabashi Akan batun haihuwa zai sunkuyar dakai yace yana bakin qoqarinsa

Momy tace a a alhaji ayi musu wani Abu de, ko Yaya ne, Abba yace Toshiknn hajiyata zansan abinyi

Dukansu sukasa daria

*** *** ***

Yana zaune ya hakimce a office dinsa, office din yatsaru mutuqa, manyan kaya ne ajikinsa, kalar milk, agogon dake daure a tsintsiyar hannun sa qirar Rolex sosai yayi kyau, daga bayansa tutar nigeria ce guda biyu manya,

Saikuma guda biyu qanana akafe agaban tebir din dake gabansa,

Deputy n sane yake masa jawabi Akan wasu takardu, ranka ya dade wannan takardar dazaka saka hannu ne Akan kudin daka ware domin akaiwa dukkanin copper's din jihar bauchi da aka turasu camp domin atallafa musu

Sai wannan kuma signing suke buqata naka saboda suna so zasu Bude gidan mai a qauyen DASS

Gasucan guda uku, wannan agarin SHIRA wannan kuma JAMA'ARE

Dauka yayi dukansu yasa hannu, yaware guda daya aciki, yace wannan ta jama'aren nags dede wajan kamar za'a shiga cikin gonakin talakawa so bazamu saka masa hannu ba

Rissinawa yayi yace ranka ya dade Allah yatemakeka

Kallansa yasakeyi yace motoci sun zama ready ne?

Sun zama ready sir

Yace to Ina ganin yau zamu kaiwa Garin GAMAWA da GIADE dakuma KIRFI ziyara

OK sir

Babu Bata lokaci suka shiga motoci suka tafi, domin Jin korafe korafen talakawan dake qarqashin mulkinsa

*** *** ***

After one week

Suna zaune a dining dukansu suna break fast, Amal, Abba, daddy, shahida, momy

Bakajin maganar kowa Sai qaran spoon dayake tashi

Shahida tace anty Amal, yaude yakamata mufita dake Garin nan kema ki duba talakawan dasuke qarqashin ku

Amal Jin maganar tayi banbara Kwai, Wai anty Amal,

Murmushin yaqe kawai tayi

Momy tace rabu da ita yata Amal, kici abinci kinji?

Daddy yazuba mata ido yanaso yaga yanayin ta

Abba ne yatashi yana goge bakinsa da tissue yadubi daddy yace to Kai idan kun gama Ina jiranku amota kaida Amal, akwai inda zamuje

Atare suka kalli juna, saikuma suka kalli abban, tsam yatashi yabi Bayan Abba, itama Dasauri ta tashi tadau mayafinta suka fita

Basu zarce ko'inaba Sai asbiti, suna Zuwa doctor ya karbesu dayake yasan da zuwansu, Amal tarasa dalilin zuwansu hakama daddy

Abba yadubi doctor, yace gasunan likita, adubamin su koba kalau suke ba, aure kusan wata shida Amma Babu ko batan wata basu taba yiba

Ba Amal kadai ba, hatta daddy saida gabansa yafadi, cikin sauri ta sunkuyar da kanta, shi kansa doctor din mamaki ne daria suka kamashi

Kai iyaye Sai hakuri,sude Koda yaushe ganin yayansu suke yara awajansu

Amma inba hakaba govnor guda asakoshi agaba haka Kamar qanqanin yaro

Dan haka yatashi yace yadubi Amal Yace ranki yadade zaki kwanta anan muyi scanning muga menene matsalar

Dago kansa yayi yacewa doctor din "am Ina ganin kawai kahadata da mace"

Abba ne ya kalleshi cikin ransa yace shegen kishi

Doctor din yace to ranka yadade, Babu dadewa yahadata da mace ta dubata, Shima aka dubashi aka tabbatar musu dacewa kalau suke kawai lokaci ne baiyi ba, anan yamai godia suka juya Mota, suna shiga Mota Amal tahada ido da daddy, atare suka kawar da kansu daga kallan juna

Suna komawa gida daddy yafada duniyar tunani waida mulkin da aka liqa masa zaiji Koda mace?

Amma zaiyi amfani da wannan damar wajan ganin ya zauna agida yahuta kamar da batare dayafita ko'inaba

*** *** ***

After 2 week's

Su daddy sun koma gidansu, yashirya yazo gida, yasamu Abba afalo, suna zaune da momy

Ya tsugunna har qasa ya gaida su, saikuma yayi shiru, Abba yace daddy nah meyake faruwa ne?

Naga alama bakin ka akwai magana, daddy yace Abba dama... Am dama Abba inasan bada riqon qwarya ne

Abba ya kalleshi da mamaki yace but why?

Daddy yace Abba ni dama wannan mulkin baya barina insake da iyali na ne

Abba dayaji haka Sai yayi tunanin ko a nasan samar musu da jika ne

Dan haka Kai tsaye cikin murmushi yace to alhmdlh ai Ina ganin saiku tafi ko Germany ne kuhuta ko, ai yafi ace za'a bada mulki riqon qwarya ko Malam karaam, saikuje kuhuta nadan lokaci ku dawo

Innalillahi... Shifa yafadi hakane Dan a barshi yahuta kamar yanda yake Ada

Abba yace tashi kaje, saika shirya kadauki matarka zuwa jibi ku wuce, Allah ya kiyaye hanya yatsare

Acan qasan muryar sa yace "Amin"

Yana fita directly office ya wuce yagama rubuce rubucensa inda yadauki hutun taqaicaccan lokaci na Tsawon wata daya, zaije qasar Germany domin aduba lafiyar sa

Babu Bata lokaci labari ya watsu zuwa dare har anfara sanarwa akafafen Yada labarai cewa maigirma governor zaije ganin likita zuwa qasar Germany

*** *** ***

Tana zaune afalo tatasa TV agaba tana kallo, gajiya tayi da kallan harzata kashe taje ta kwanta, saitaga Ana sanarwa maigirma governor zuwa jibi zaije qasar Germany domin duba lafiyar sa

Inda zai dauki tsawon wata daya kafin yadawo, al'amarin daya daga hankalin masoyan sa, inda suke masa fatan samun lafiya

Tana gama Jin labaran ta kwashe da daria, afili tace maqaryatan banza, Wai Germany

Ko waye ba lafiyar oho

Daria tasake saki tace wallahi suzo wajena su samu labari, bawani Germany dazaije, yana Nan agida rass yake

Motsin dataji abayanta ne yasa cikin sauri tajuya, gabanta ne yafadi lokacin datai ido biyu da daddy atsaye

(masoyana masoyan wannan novel, ina mai Baku hakurin rashin typing din dabanyiba Daren jiya, hakan yafaru ne Sanadin rashin charge da banda shi, Amma inaso kusani yanda kukai ta tunanin BURINAH jiya haka Nima naita tunanin ku, nagode)

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

17

Cikin ranta tace shikkenan namutu

Miqewa tayi tana karkade jikinta kamar Wanda ta zauna acikin qasa,tana tafiya da baya da baya

Takowa yakeyi yana kusantota, tanayin baya yana sake matso ta, har sukaje Jikin bangon falon

Yasa hannu yadafa bangon yazuba mata ido fuskar sa babu alamar wasa

Itama zuba masa ido tayi, ganin fuskar su dab data juna kamar Wanda zaiyi kissing dinta

Nan da nan tafara zare ido

"me kikace? "

" naji kamar kina magana "

Girgiza kanta tayi, yayinda idanunta suka Raina fata, cikin tsoro tace a a badakai nakeba, wallahi wani film na kalla

Kallan kin renamin wayo yayi Mata ya nunata da hannun sa yace idan kika sake qaryatani saina tsinka miki mari

Ayanda taga qwayar idonsa tsaf zai iya Marin nata Dan haka tayi sauri ta tsugunna ta qasansa tayi wuf tashige dakinta ta datse kofar

Kan gado tafada tana maida numfashi, yayinda murmushi ya wanzu asaman Fuskarta

Murmushin sa ta tuna na jiya, yanayin Zaman su, yanda yake magana cikin aji da soyaiya

"kinata surutu baki kawo musu ruwaba?

Juya manyan idanunta tayi, data tuna abinda yafaru tsakanin su yanzu

" me kikace? "

Tatuna da maganar sa, lumshe idanunta tayi, ta Bude, afili tace lips dinsa mai kyau pink dashi Dan qarami

Fuskarta ce ta sauya data gama tunanin, ganin ita kadai take haukan ta, tashi tayi tashiga toilet domin watsa ruwa, saboda zafin da akeyi agarin

Tana futowa tasaka rigar bacci acikin rigunan aurenta, baqa ce, Gaba daya tsawon rigar iyakarsa gwiwarta, gashin ta data wanke tazo takama ta taje, ta shafa mayuka masu mutuqar qamshi

Ta daure shi ta kwanta

Kamar wasa cikin baccinta taji iska me karfi natashi, Windows din Dakin Sai budewa suke suna rufewa, tashi tayi taleqa taga Gari yahadu da hadari

Tayi sauri taja windows din ta rufe, Takoma ta kwanta

Wata gigitacciyar tsawa akayi dayasa Amal sakin ihun dabata shiryaba

Ta takure awaje daya, alokacin daddy yana falo, Babu ruwa a fridge din Dakin

Yafuto zaisha ruwa yaji Qarar ta, kamar zai share ta saikuma yatunkari kofar Dakin

Ahankali yatura kofar Dakin yashiga, ya tsaya daga bakin kofar yana kallan yanda ta takure waje daya tana kuka

Rigar bacci ne ajikinsa fara qal me madauri daga cikinsa, Samanta kuma abude take, hakan ne yabaiyanar lallausan baqin gashin daya kwanta a faffadan kirjinsa

"me kike yi haka? "

Tana Jin muryar sa, tadago da kanta ta ganshi, Dasauri taje tafada jikinsa tana cigaba da kuka

Binta yayi da kallo yanda ta rirriqeshi, kallan rigar baccin dake jikinta yayi, anan yayi ido biyu da madedetan nashanunta, dasuke acike atsaye, bulbul dasu farare

Maganar tace tadawo dashi daga kallan daya Lula, cikin kuka tace ni Yaya daddy tsoro nakeji, Allah bazan iya kwana ba

Still Kallanta yake yakasa magana, haka kuma yakasa rungume ta da hannayensa

Tuno jiya yayi yanda ta rirriqe Shahid kamar wani mijinta

Wani haushi yataso masa, nan da nan yafinciketa daga jikinsa

Kan gadon ya nuna mata yace "kwanta"

Girgiza Kai tayi tace ni tsoro nakeji

"nace ki kwanta "

Ganin bayasan musu yasa taje kan gadon ta kwanta, ta maqure awaje daya

Kujerar dake gefe yanema ya zauna, yana aikin Kallanta

Ita kuwa tana runtse ido, kuma ga daddy tana gani a gefe, hakan yasa ta janyo teddy bear dinta guda daya ta rungume shi, tayi shiru ta nutsu har bacci yadauketa

Ahankali yatashi yaje kanta yatsaya yana Kallanta

Wani irin yanayi daya dade rabonsa dashi yana fizgar sa

Ganin tayi bacci yasa yakashe wutar Dakin, yarage karfin esi, sannan yaja kofar ahankali gudun kada ta tashi, yafice yayi dakinsa

Yana kwnciya yayi addu'ah, ya runtse idonsa domin bacci, saide me, yana rufe ido itan de yake gani

Yanayin su na dazu yatuna, tsoron daya gani atare da itane yafi birgeshi,murmushin dabai shirya bane ya qwace masa

Wata zuciyar tace Kai karaam shiga taitayinka, wannan yarinyar babu kowa acikin ranta banda yayanta

Fuskarsa ce Takoma yanda take Ada,Babu walwala

Yajuya ya gyara kwanciyarsa, yana tunanin to mema yakai shi Dakin?

Fillon gefensa yadauka yayi wulli dashi, yayi DANA SANI yafi aqirga

Daga baya bacci yadaushi

*** *** ***

Washe gari Amal daqyar tatashi saboda yanda baccin yayi Mata dadi, tana idar da sallar asuba, tadau alqur'ani tana karantawa, har Gari yayi haske

Window ta Bude taga yanayin Gari

Taga yana Nan baqiqqirin da hadari

Rufewa tayi, ta dauke alqur'anin data karanta, tafuto tahada musu break fast

Shayi ta zuba ta gabza Uwar madara, tayi dakinta, tana gama shan shayin tayi wanka, tasaka doguwar rigar material

Kanta babu dankwali kamar kullum tafuto falon ta zauna

Yayyafi aka fara, daga nan ruwa ya zuge ake zubashi kamar da bakin qwarya

Fita tayi harabar gidan, tafara wanka cikin ruwan Saman da ake

Kamar a mafarki yakejin daria na tashi, gashi Ana ruwan sama, tashi yayi yabude window din dakinsa, dayake asama yake, can yahango Amal tana wanka tana zuba daria acikin ruwa, sai juyawa take, gashin kanta daya jiqe yana sake dawowa yarufe mata fuska

Tana janyeshi tana cigaba da wankanta

Besan adadin lokacin daya dauka yana Kallanta ba, labulan yasaki tareda rufe window yace "kanki idan kika hadu da jinya"

Amal kuwa Bata dawo ciki ba saida tagama wanka ta tsaf, tadawo ta cire kayan jikinta, ta sauya wani ta kwanta tana game awayar ta

Dan babu komai acikin wayar banda game

*** *** ***

Washe gari karfe goma nasafe, yashirya cikin baqin yadi, kalar kayan ta karbi jikinsa, hasken fatarsa yafuto acikin yadin

Agogon hannun sa ya kalla qirar plaget, ya furzar da Iska me zafi, saura awa daya jirgin su yatashi, gashi wannan yarinyar ko futowa batayiba

Shikuma bazai shiga dakinta yagano wa kansa abinda zaizo yadameshi ba

Goma da kwata, nayi aka fara kiransa, masu jiransa ne Wanda zasu rakashi airport

Ganin zai batawa kansa lokaci yasa yasa yatura kofar Dakin ahankali, ganinta yayi tana kwance hankalinta kwance Sai sharar baccinta take

Teddy din dake gefenta yadauko ya zungureta dashi, ahankali take Bude idonta, harta budeshi gaba daya tareda wata irin miqa

Innalillahi, yafadi haka aransa yajuya mata baya, yace ki tashi ki shirya ki dauki kayanki zamuyi tafiya

Yana fada Mata haka yajuya yafita

Dakinsa ya koma ya zauna agefen gado tare da cire hularsa ya ajiye a gefe

Dama abinda yake gudu kenan, gashi kuma yafaru

Amal kuwa tana gama wanka ta duba kayan dazata saka, Murmushi tasaki ta janyo baqar abaya me adon stone ajikinta tasaka, tace yauma iri daya zamuyi Yaya daddy

Da dankwalin abayar tayi rolling, tayi farkin gashin ta, Tasa red din janbaki sosai tayi kyau, kasan farin mutum da Jan janbaki, nan da nan ta haska, shafe dinta yafuto sosai acikin rigar, kayanta tasaka Dasauri acikin trolley

Ta janyo Jakarta zuwa falo

Wayam taga bayanan, harabar gidan ta leqa still be futo ba, Dan haka tabishi dakinsa

Tana zuwa taganshi a zaune ga qaramar trolley agabansa yana kokarin rufewa Amma taqi rufuwa

Motsin ta yaji yadago kansa ya kalleta, Kasa janye Idanunsa yayi akanta, Murmushi tasakar masa, tatako ahankali har zuwa gabansa

Tsugunna wa tayi dab dashi, sai a sannan ya janye Idanunsa akanta, Gaba daya qamshin turaren data fesa yacika masa hanci, Hannunta ta miqa tace

"kozan iya temaka ma?"

Fuskarsa ahade yasakar mata jakar, ita kuwa duk ta cire kayaiyakin ciki, tayi mamaki sosai ganin gaba daya qananan kaya yadiba, aranta tace shida baya saka qananun kaya da yawa, yau shine duk ya jidesu

Daya Bayan daya take nade kayan tana maida wa cikin trolley din, aranta tana cewa ita jakar mahaukaciyar inace zata rufu Bayan an tula mata kaya ko ninkin arziqi babu

Kallanta yake sosai, harta gama, 'yar qanqanuwar yarinya da ita, Amma ta iya wannan aiki

Jakar ta janyo tace masa Toni nafita

Abaya ya biyoba, suna Zuwa falo ya karbi jakarsa itama ta janyo Tata trolley din

Sunzo fita daga falon kenan yasake dubanta, yace

"ina wannan abin naki?"

Fari tayi da idonta, tace wanne Abu?

Babu alamar wasa afuskar sa yace "ina nufin wannan baqin abun dakike sakawa a face dinki"

Da mamaki ta kalleshi tace, au Wai niqab kake nufi?

Be Bata amsaba, sai kansa daya jijjiga mata

Juyawa tayi ciki, Dasauri ta dauko shi, agabansa ta daura sannan suka fita

Baqar Mota suka shiga qirar Range Rover, driver zai fice daga gidan kenan ya dakatar dashi, ya leqa ta window yace iliya, daga yau kadena aiki anan, ka koma can daya gidan kasanar dasu cewa nace subaka aiki kowanne iri ne

Cikin ladabi yace to ranka ya dade

Sunyi Nisa ahanya ta dage niqab dinta ta fuskanceshi tace to kuma waye zaina Bude gate din?

Kallanta yayi yace "duk mutumin daya zabi nunawa masu gadi jikinsa ai dole zaizo yaci gaba da aikin masu gadi"

Tanajin wannan furucin nasa tasan cewa da'ita yake, Dan haka taja Bakinta tayi shiru, niqab dinta ta maida tadinga hararar sa

Suna sauka a Airport jama'ah suka cika wajan, Amal na gefe taji andafa ta, tana dubawa taga shahida ce

Shahida tace anty Amal zuwa nayi Inga tafiyar ku, Dan Allah idan kunje nide karki manta da tsaraba ta nida Shahid nida dina

Haushi ne yasa Amal ture hannun ta daga jikinta, duk abinda suke daddy yana kallansu

Ana sanarwa zasu iya shiga jirgi, yayi sallama da mutane, Amal ko kallan shahida batayiba taja Jakarta tayi ciki

Wajan daddy shahida ta nufa tace Yaya daddy saikun dawo, da tsadaddan murmushin sa yace Mata to a kula de banasan yawace yawace fa qawaye, tace to Yaya bye bye

Juyawa yayi wajan Amal, suka shiga cikin Sir Abubakar Tafawa Balewa International Airport Bauchi, inda sukabi jirgin Emirates zuwa Germany

*** *** ***

Saukar dare sukayi, Amal Sai Kalle Kalle take da mamaki, ashe de da gaske yake tafiyar zaiyi, Allah Sarki hartake qaryatawa

Basu zarce ko'Inaba Sai hadaddan Hotel din nan naqasar Germany wato Berlin

Tana bayansa a reception yagama musu komai, daki daya suka kama

Suna Zuwa Dakin ta zauna jagwab,Akan kujera saboda gajiya

Shikuwa banda aikin amsa waya babu abinda yake

Yana gama wayar yatashi yafice daga Dakin

Be dade ta futaba, taji Ana nocking tana budewa taga ma'aikaciya ce takawo musu abinci, karbar abincin tayi, tajuya cikin Dakin

Gasasshiyar kaza ce da chips, sai shinkafa dataji kori

Dasu Lemon tsami aciki

Zama ta gyara taci abincin tayi Nak, ta ajiye masa sauran, tashiga toilet tayi wanka

Rigar bacci Tasa yellow, daga Saman breast dinta qoqo ne da rigar, daga qasa kuma net ne, kana iya hango komai na jikinta

Tafeshe jikinta ta turare, ta kalli Dakin, afili tace to ga gado ga qasa ga kujera

Idan nabari yadawo qarshan al'amarin zai juye ne yadawo kaina, in kwanta aqasa ko a kujera, shikuma hakimin a gado

Nikuma bazan iyaba, Dan haka bari insamawa kaina mafita, tana gama magana tahaye gadon tayi daidai akansa, tacire ribbon dinta, tare da baza gashin kanta tayi addu'ah Sai bacci

Karde amanta da :

Comments

Share

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

18

Saida yayi kusan 1hour awaje, yana qara bayani Akan aiyukan daya bayar ayi kafin yadawo, sannan yadawo Dakin

Yana turo kofar da kyakkyawar Fuskarta yayi tozali, tana baccinta hankali a kwance,duk gashin kanta ya rufe mata fuska, jijjiga kansa yayi yanufi toilet ya watsa ruwa yafuto yasaka jallabiya baqa

Jikin gadon ya matsa yana Kallanta yace "tashi kikoma qasa"

Yaji shiru

"nasan Sarai kinajina nace ki tashi kikoma qasa"

Nanma yaji shiru, fillon datayi matashi dashi ya bubbuga, ahankali ta Bude idonta, saboda gajiya ga kuma bacci daya dauko dadi

Ta kalleshi, yana tsaye qiqam, tace menene?

Yace nace ki tashi kikoma qasa

Kallansa tayi da mamaki tace qasa? Qasafa kace, uhum wallahi bazan iya kwana a qasaba, saboda ban sababa, jikina ciwo zaimin

Tajuya masa baya tayi kwanciyar ta

Kallanta yake da mamaki, wato kenan de yanzu yarinyar nan tana nufin shine yasaba kwana aqasa ko

Zagayawa yayi ta daya gefenta yadauki fillon gefenta ya wullar aqasa, yadawo yasa hannun sa Akan fillon datake kwance, yajanye fillon, jikake qum

Yabugawa Amal kanta ajikin gadon

Da sauri ta tashi zaune tace Kai Kai Kai

Tana shafa inda ta bige, yau nashiga uku Daren Hana bacci yazo

Kallanta yake sosai, yakasa Hana qwayar idonsa kallan abinda take muradi

Cikin karfin Hali yace "ki iya bakinki"

Kuma still yakasa dauke ido akanta

Hararsa tayi afakaice, aranta tace wallahi gaskiyar Yaya Shahid

Miqewa tayi, tabude kayanta ta dauko jarkar maganin da umma ta aiko mata, takafa Kai tasha sosai

Duk abinda take yana Kallanta afakaice

Tana gama Sha tajuyo tana cewa irin wannan kallan haka ai saida neman tsari

Yace "me kikace?"

Tace a a magana nake da kaina, tahaye kan gadon ta kwanta tare da rufe ilahirin jikinta

Ajiyar zuciya yasauke,yace tashi ki kawomin abinci, dago kanta tayi ta nuna masa abincin tace gashi can acan ai

Shima yace nagani

Tana zunbura baki ta tashi takai masa abincin Takoma gado, yana ganin ta kwanta yasake cewa

Bani takarda acikin jakata

Kafin ta motsa saida tadafe kanta da Hannunta, tace Yaya daddy, Amma bacci nake fa

Kallanta yayi bece mata komai ba, ta tashi ta dauko masa, Takoma gadon zata kwanta tace akwai wani Abu kuma?

Girgiza mata Kai yayi yana Kallanta, tana ganin haka tajuya tasake addu'ah ta kwanta

Iska ya firzar daga bakinsa, shi kansa yarasa gane kansa, yarasa meyasa yake sakata wannan aikin

To Amma meyasa zata lullube jikinta?

Amal kuwa tana komawa gadon bacci ya dauke ta

Shima abincin yaja Dan dole yaci kadan, ko kula takardar data bashi be yiba

Tajera fillon daya dauko agadon yadauko blanket ya shimfida aqasa, yatakure ya kwanta anan

*** *** ***

Alerm ne yatashe su dede lokacin sallar asuba, atare suka farka, Amal ta tashi tana murtsike idonta, tare da hamma saboda baccin be ishetaba

Daddy yana farkawa yaji bayansa ya amsa, Dasauri yakai hannun sa wajan, yaji wajan yariqe, saboda kwana a'inda bai sababa

Dakyar yatashi yashiga toilet, yayi wanka tare da alwala, yana futowa itama tashiga tadauro alwala, tanata kallansa aranta tace wanka da wannan asubar kona menene oho

Yana sallah tana binsa abaya har suka idar, tana gama lazimi Takoma ta kwanta, shikuma yadauko alqur'ani yana karantawa, tana daga kan gadon ta zuba masa ido tana kallansa

Gashinan mutum har mutum Amma ba shida mutuncin kirki

Runtse idonta tayi, Takoma bacci

Shima yana gama karatun, yayi oder abinci yaci, yafita, be zame ko'Inaba Sai Chemist

Maganin ciwon jiki ya karba, yasha, yajefa sauran a aljihunsa, daga nan ya wuce yawon sa ko inda Amal take bai nemaba

Amal kuwa Sai wajan karfe goma ta farka, tayi wanka tashirya cikin atamfa dinkin Riga da zani, Wayarta ta dauka,zata kira su umma Amma Kuma batada Sim card din qasar

Dole Sai hakura tayi ta kwanta

Baidawoba Sai yamma, yana shigowa Dakin tayi masa barka da zuwa

Agajarce ya amsa da "yauwa"

Wanka yashiga, yafuto sanye da jallabiya ajikinsa

Tashi tayi Takoma wajan window tana kallan waje, harya gama shirya

Yadauko takardunsa yafara aiki

Ahankali tace Yaya daddy

Batare daya kalleta ba yace "inajinki"

Dama Dan Allah Dan kiramin anty mufy kaji

Kallanta yayi batare dayace mata komai ba yadau wayar yamiqa mata

Da murmushi afuskar ta, ta karba ta duba Wayarta tadau number takira

Tana shiga anty mufy ta daga, Amal tace anty Ina yini

Muryar wa nakeji kamar masu tafiya honeymoon?

Batasan lokacin datasa daria ba tace a a anty duba lafiyar Yaya daddy mukazo, mufy tace haka de kukace, kawai kuce kun tafi soyaiyarku

Amal ce ta kawar zan can da fadin anty ya junior?

Yana Nan lafiya Amal, inji de babu abinda Dan rigimar nan yake miki ko?

A a anty babu komai, Toshiknn ku kula da kanku bye bye, to anty bye

Tana kashe wayar memakon tabashi saitasa number umma suka gaisa itada baba, sannan takira maisah

Maisah tace Amal wannan layin fa, tace kede bari layin Yaya daddy ne, maisah tace inyee kice komai yazama normal anriga da anwuce wajan?

Ajiyar zuciya ta sauke tace kede bari qawata saina dawo kawai, maisah tace Toshiknn Amal, suna sallama saita kira Shahid, yana dagawa tace Yayanah yakake yagida?

Takardar hannun sa ya ajiye, tsam yatashi yanufeta, batare da yayi Mata magana ba, yamiqa mata hannun sa

Hannun nasa tabi da kallo, alama yayi da kansa ma'ana tabashi wayarsa, idanunta cikin nasa, tabashi wayar

Yana karba yakashe wayar yace "ba kudin banza gareniba dazaki dinga mutane shashakai dashi"

Lalle ma Yaya Shahid dinne shashasha? Tafadi haka aranta

Daukar Wayarta tayi afili tace yaqi taho shashashar wayata, ni Ina sanki, haka yanmata da qannan wasu suna rububinki

Kallanta yayi, yazo dab da ita yace maimaita abinda kikace

Cikin takaici da bacin rai itama tace cewa nayi qannan wasu na rububinki

Yace ita wayar Taki?

Tace nifa bada Kai nake ba, fuskar sa yakawo dab da Tata, ya nunata da yatsa yace idan kika kuskura kika sake kiramin wannan Yaron acikin wayata saina zaneki

Hannunsa takama zata janye takasa

Nikam yayanah ba yaro bane

Cikin bacin rai yace ok, to waye Yaron? Kinsan de inda salma na nan toda tuni na haifeki ko?

Haushi ne yakamata, Jin sunan daya ambata cikin faduwar gaba da bacin rai tace Dan Allah Nika matsa

"bazan matsa ba, kisanar Dani waye yaro? "

Abinda yace kenan

Kokarin matsawa tafarayi, shiko ko gizau be yiba, tana yunqurawa zata tashi ya damqi hannun ta yafizgota dab dashi har sunajin hucin numfashin juna

Idanu suka zubawa juna,nadan wani lokaci, itace tafara janye idanunta acikin nasa

Ta qwace jikinta, Shima yasake ruqota, da karbi ta fizge jikinta, Garin yaruqo hannun tane, saita zame, hannun sa bai sauka ako'inaba Sai Akan nashanunta, yanda yayi niyyar kaiwa Hannunta kyakykyawar damqa aka samu akasi haka yayi musu, wani irin laushi yaji

Atare suka zaro idanunsu

Cikin sauri yasaketa tare dayin baya

Itama Dasauri Takoma kan gadon tare da juya baya, Shima wajan takardunsa ya koma, shiru Dakin yayi, kamar ba yanzu ne suke hayaniyaba

Daddy shiru, Amal shiru

Cikin ransa yace shikkenan najawa kaina raini awajan yarinyar nan, da wanne ido zan kalleta?

Itama anata bangaren cewa take nashiga uku, abinda bai taba faruwa daniba, nida Bayan Yaya Shahid babu Wanda nake hada jiki dashi

Amma Yaya daddy.... Innalillahi

Runtse idonta tayi, kamar mai bacci, Awannan Rana har dare yayi suka kwanta basu sake yarda sun hada idoba

Hakane yayita kasancewa atsakanin su har tsawon sati daya, yau da dare yayi, cikin sauri yadauki wayarsa yahau kan gado ya kwanta

Amal tana ganinsa batace komai ba, saida tazo kwanciya, ta tsaya akansa tace Yaya daddy zan kwanta, qasan Dakin ya nuna mata, yace ga wajenan, nahanaki kwanciya ne?

Kallan qasan Dakin tayi, taja fillo tadau bargo tayi shinfida ta kwanta, Dan ita Kam tadena musu dashi, Kar abinda yafi na rannan yasake faruwa

Yana Kallanta, harta yi bacci sannan Shima yayi bacci

Da asuba Bayan sunyi sallah da Gari yayi haske yatashi zai koma gado ya kwanta, yaga Amal tana mammatsa Hannunta, alamun ciwo yake mata

Maganin daya siyo rannan yatashi yadauko ya wulla mata, yahaye gadon yamiqe

Maganin ta kalla, ta kalleshi, shi ko tausayin ta ma bazai jiba? Kodan yata iya tunda itace tafara

Maganin tasha ta kwanta, sai wajan shadaya nasafe suka farka, shine yarigata tashi, yashirya cikin qananun kaya, baqin wando baqar Riga mai adon ja agaban rigar, saikuma takalmi baqi Shima

Sumar sa tasha gyara, yayi kyau na qarshe

Amal tana ganinsa zai fice aranta tace wallahi nadena Zaman gadi, Dan haka tace, Yaya daddy Nima zani

Kallanta yayi, sannan yace ba Kiyi wanka ba, baki shirya ba tayaya zan tsaya ki batamin lokaci?

Cikin shagwabar da ita kanta tayi mamakin kanta, tace Yaya daddy yanzu fa zan shirya

Kafada yadaga, yanufi kayansa yana fesa turare

Cikin sauri ta dauki towel, ko kayan jikinta Bata cire ba ta nufi toilet

Kallanta yayi, yace minti goma

Dasauri tace to

Tashige toilet din

Zama yayi a bakin gadon Dakin yana kallan wayarsa

Ajima ya kalli agogo ajima yasake kallah

Amal naciki tana Cuda jikinta, ko rabi Bata yiba, taji yace "minti shida"

Sauri taqara Sawa, tagama Cuda jikinta kenan taji yace "minti tara"

Batayi wata wataba, ta sheqa ruwan taja towel tadaura tafuto

Gaba daya iyakar towel din Rabin cinyarta

Yanajin Bude kofar toilet ya kalli wajan

Idanunsa ne suka sauka Akan santala santalan fararen cinyoyinta, yazuba musu wani irin Mayan kallo, yakasa dauke idonsa akansu

Ita kuwa batasan ma yanayiba, tana sauri ta shirya karya tafi yabarta

Agabansa tayi komai, tashirya cikin doguwar Riga, tayi Rolling, tajuyo tace masa nagama

Dago kansa yayi ya kalleta, sannan yatashi yayi gaba

Yaya daddy

Takirashi

Yajuyo be ce mata komai ba

Tace meyasami idonka yayi ja?

Kai tsaye yace Mata ciwo yake

Da kallan mamaki tabishi, ciwon ido alokaci daya haka? Allah kenan me iko

Suna fita basu zarce ko'Inaba Sai wajan shan iska, Amal anata waige ta kalli nan ta kalli can

Wato kenan shi yawon sa yake fita yabarta a hotel a kulle

Wallahi ta dena yarda yafita, yabarta

Suna shiga wajan, sai yan tsirarun mutane awajan, kowa yana harkar gabansa

Wajan zama yanema yazauna, itama haka ta zauna agefensa, tana kallansa tana murmushi

Kallan qarin bayani yayi Mata

Babu wata alamar tsoro atare da ita, tace "kayan sunyi ma kyau Yaya daddy, idan muka koma nigeria kadinga saka qananun kaya"

Eh Lalle Sai yau yasake tabbatar da yarintar wannan yarinyar, in banda yarinta tayaya yana matsayin babban mutum a'idon jama'ah kuma governor zai dau

qananun kaya yasaka? Shiyasa fa wasu ayyukan daya kamata ace itace zatayi baya kulata yabata, Dan yasan cewa lokaci daya zata lalata komai

Ai saide yasa suit kokuma manyan kaya,Dan haka ya share ta kawai

Tasake cewa kaji?

Dan karta dameshi ne yasa yace to

Murna acikin Amal, yau itama Tasa mijinta Abu, yace zaiyi

Kallansa tayi tasake cewa Yaya daddy zansha ice cream

Wani waje yanuna mata yace ga wajan can

Hararar sa Tayi ta shareshi, yasanfa batada ko sisi Amma yake cewa ga wajan can it means taje ta siyo

Suna zaune shiru Shiba magana ita kuma taji haushi ta qyaleshi

Saiji sukai an bugo musu ball

Atare suka kalli ball din, kafin su Dago saiga wani kyakykyawan yaro yazo zai dauka

Amal tana ganin Yaron taji ya birgeta

Kamashi tayi ta riqe

Daria Yaron yasaki yace anty nadena please

Mamaki ne yakama Amal da daddy Jin hausa radau a bakin wannan farin Yaron kamar bature

Tace Toshiknn niba abinda zanyima, zoka zauna, zaka tayani fira?

Daga Kai yayi yace eh

Daddy kuwa kallansu yake da birgewa sosai suka bashi sha'awa itada Yaron

Allah yazuba masa son yara, Amma Kuma gashi Allah Bai bashi ba

Me photo ne yake yawo da camera awuyansa, yanayiwa mutane photo suna bashi kudi

Shi kansa yana zuwa wajan su yaga sun birgeshi, yaqaro so yace wow fine boy

Kafin ma yanemi izninsu yafara yiwa Yaron photo

Yadubi Amal Yace kece maman sa? Aikuwa tace eh, yace ta dauki Yaron ayi musu, aikuwa ta sakashi a cinyar ta akayi musu pic din, ya cewa daddy Shima yamatso

Ahankali ya matsa kusa dasu, me photon yace kariqesu mana, ahankali ya rungume Amal, itama ta rungume Yaron akayi musu wani

Me photo saiyi yake, yadago kansa daga kan camera yace Amal ta zauna a cinyar daddy ta riqe Yaron yadauke su

Gabanta yafadi, itafa jikinta yafara sanyi da wannan photunan tunda anyi na marmari ai shikkenan ko

Me photon yace please

Shi kuwa daddy ido yazuba mata yaga gudun ruwan ta

Dan karta bayar da kanta awajan me photo yagano halin dasuke ciki ne yasa kawai ta tashi ta Dane cinyar daddy

Innalillahi... Wannan yarinyar kanta daya kuwa,? Yake tambayar kansa

Amal de adarare ta zauna Yaron kuwa babu ruwansa Shima yahau cinyar Amal, akayi musu photon, yana gama dauka tsilak tatashi daga cinyar sa

Camera yabasu, Wai suga pictures din, suna cikin gani Yaron yataba camera yace gani, gaka, yanuna Amal Yace ga momy

Murmushi daddy yayi yace cewa zakai ga daddy, ba gani ba kaji?

Yaron yadaga kansa

Daddy yace yasunan ka? Yaron yace Sunana Hanif ahmad Muhammad marzuq

Daddy tace what?

Kafin yayi magana saiga iyayensa sunzo wajan

Daddy naganin ahmad yace haba, no wonder, nide yacemin hanif ahmad Muhammad

Cikin murmushi ahmad yace daddy, Wai Kaine anan? Gaba daya ganinku yayi wahala, siyasa ta boyeku

Daddy yace kaide bari abokina, wannan duk aikin Abba ne wallahi

Cikin daria ahmad yace wallahi nasani, kaga iyayen nan namu Sai ahankali, shiyasa nabaiwa ayyukan company na muhinmanci sosai, saboda Nima kada dady yasakani a harkar siyasar nan tasu

Gaba daya sukasa daria daddy yace eh gaskya ne, wallahi

Wai kana nufin wannan Yaron Kane? Ahmad yace emana, ai twins ne ga dayan can shida mamansu suna tahowa

Itama tana qarasowa ta miqa wa Amal hannu suka gaisa, wadda mamaki yakashe ta a zaune

Tace sunana nafeesa, Ana kirana da feenah

Amal tace sunana Amal

Abinka da mata nan suka koma gefe suma suna tasu firar

Amal nan da nan tasaki jikinta da feenah, da fira tayi tsawo nema feenah take qara wayar mata dakai Akan Zaman takewar rayuwar aure, tana qara jaddada mata cewa ta riqe mijinta dakyau

Domin kuwa sun dace mutuqa

Zan can sosai yashigi Amal, anan taita mata godia

Ahmad ne yace zasu tafi, anan daddy yake cewa yaushe zasu tafi sukace gobe, dama kawai sunzo hutawa ne nadan lokaci

Daddy yace suma suna kan hanya nanda sati uku

Amal ta riqe feenah tace anty nafeesa, Dan Allah ku daga tafiyar kizo muyita firar mu

Feenah ta dafata tace kiyi qanwata, insha Allah wataran zan kawo miki ziyara

Abinda yasa zamu tafi gobe, Ana bikin aminiyata ne Zahra da abokin karatuna kb

Amma Badan hakaba zan tsaya, rungume juna sukai

Anan sukai sallama suka tafi

Wajan shiru yasake yi kamar da, Amal ta dubeshi aranta tace kiga yanda yake zubawa abokinsa daria, Amma ni ko oho

Saida suka dade awajan sannan suka kama hanyar komawa hotel, ita kadai yace tayi gaba zaije yadawo

Batace masa komai ba tayi ciki, tana shiga daki tafada duniyar tunanin makomar aurensu

Daddy baya kulata, Amma kowa bashida bakin magana saide yace sun dace

Har tsawon wanne lokaci zasu dauka ahaka? Wanne irin miji Allah yabata ne?

Tana wannan tunanin taji yaturo kofar Dakin yashigo da Leda ahannunsa

Be tsaya ko Inaba Sai Gabanta, ya miqa mata Ledar

Karba tayi cikin sanyin jiki ta Bude, tana budewa tags ice cream ne aciki dayawa

Da murmushi a Fuskarta tadago tana kallansa

Comments and share please

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

19

Tace nagode Yaya daddy

Juyawa yayi yakoma kan kujera yana cire safar qafarsa, Kallanta yake yanda take shan ice cream din har wani lumshe ido take, ta wani kama suna ta riqe kamar a bakin ta

Yana Kallanta takai sauran cikin fridge, tadau towel zata shiga wanka yatashi yabar Dakin, Dan yadena gangancin ganowa kansa tashin hankali

Lokacin daya dawo Dakin tagama wanka, tana tsaye tana fesa turare yashigo, saudaya ya kalleta yadauke kansa

Yadau jallabiya yashiga toilet, lokacin harta kwanta, dataga yafuto ne ta tashi Takoma window danta barshi yashirya anutse duk da acikin jallabiya yake

Yanayin Garin take kalla, tako'ina yahadu, tana Nan Jikin window harya gama shirya yazo gadon Shima yaja bargo tare da kwanciya

Motsinsa taji a gado, takai Kallanta Gare shi, tace a a Yaya daddy yahaka?

Kallan rashin fahimta yayi Mata, Dan haka tace nice fa a kwance agadon

Amma Kuma Naga kazo ka kwanta, anan zaka kwanta ne?

"amsar kenan"

Abinda yafada mata kenan yajuya mata baya ya share ta

Takaici da haushi suka cika Amal, Toma da meyasa ta tashi?

Kawai daga bashi dama yashirya shine harda zuwa gadon ya harde

Fillo taja qwaya daya tayar aqasan Dakin

Taje ta dauko jarkar maganin tsuminta, muryar sa taji yana cewa "menene wannan?"

Cike da haushi ko kallan inda yake batayiba tace "maganin tsari ne"

Yana Kallanta ta kafa Kai ta diddika sannan Takoma qasan Dakin ta kwanta ko blanket Bata shinfida ba ta kwanta haka

Kallanta yake Sai cika take tana batsewa kamar zata fashe, yaruntse idonsa gamida bacci

*** *** ***

Washe gari ma haka Amal ta tashi jiki duk ciwo,tana kallan maganin daya wullo mata rannan ko kula shi batayiba bare tasha, tana tashi tayi wanka, yarigata tashi, ashirye ta ganshi Amma takardu ne agabansa

Dan haka itama ta shirya ta zauna tana jiran yagama su fita

Shiru shiru bataga alamun zai fita ba tace Yaya daddy, yau ba fita?

Yace "zan fita de wajan koyan gaisuwa"

Ajiyar zuciya ta sauka, sannan tace Ina kwana?

Yayi banza ya shareta

Har yamma suna zaune ahaka, Babu me magana, shi yana aikin gabansa, ita kuma ta kama masa ido tana kallansa

Meyasa takeji ne komai yayi birgeta yake?

Meyasa take yawan tunanin sa?

Mutumin akwai aji ba laifi

Lumshe idonta tayi aranta tace dole in nemi maisah idan nakoma in fada Mata abinda nakeji game dashi, ko zata Iya bani shawara

Haka suka zauna har dare, Babu inda suka fita, da daddare yauma yarigata wanka, Dan haka yayi kwanciyarsa a gado, saboda yagaji da aiki sosai

Yakashe wutar Dakin ya kwanta

Amal na futowa daga wanka ta kalli daki duhu, ta kalli qasan Dakin baya nan, kallan gadon tayi taganshi ya kwanta harya fara bacci

Dan haka ta shirya itama, cikin rigar bacci medan kauri kadan

Tafesa turare ako'ina na jikinta, ba tayi wata wata ba ta Haye gadon ta kwanta

Wato shi ko ajikinsa, ta mutu ko Tai rai, saide ya miqe a gado yabarta da kwanan ciwon jiki

Addu'ah tayi ta kwanta

Bacci yayi bacci, Amal Sai juyi take, batasan ta kusanto kanta dashiba, haka Shima cikin hancinsa yakejin qamshin turare da humra, natashi, baisan lokacin daya matso ba, hancinsa daidai wuyan Amal, bacci yayi dadi alarm ya buga, Babu wanda ya motsa acikinsu

Saida Gari yafara haske, Amal tafara Bude idonta ahankali, Gaba daya shaf ta manta tare take da daddy, tana gama Bude idonta taganta ajikinsa

Gaba daya kansa yana Jikin wuyanta, kamar Wanda Yake kissing wuyan nata

Da karfi tace wayyo Allah nah!

Hakan data fada ne ya farkar da daddy daga daddadan baccin dayake

Kallanta yayi, yaga yanayin da suke ciki

Cikin sauri ya tureta, yatashi yashige toilet, yasakarwa kansa shower

Meyakawo wannan yarinyar kan gado? Inaga de yarinyar nan idan baiyi da gaske ba zata sa azo ayi abin kunya

Yana futowa daga wanka yaga tagama gyara gadon

Kallanta yayi yace "meyasa kika kwanta a gado?"

Murya ciki ciki tace Yaya daddy jikina ne yake ciwo idan na kwanta aqasa, saboda ban sababa

"to waye yasaba? "

Tace ba kowa, kuma saida nacema ka kwanta Akan gado Bayan nice zan kwanta kace amsar kenan

Cikin bacin rai yace ok nagane, to Dan Allah kici gaba da kwanciya kinji, zakiga abinda zai biyo baya

Yana fada Mata haka, yatada kabbarar sallah

Itama toilet din tashige tana cewa babu abinda zan gani Sai alkhairi

Tun daga wannan Rana Amal ta tsorata da maganar daddy, tadena kwana a gado, tadawo qasa, tun jiki na tsami harta saba

Bayan fitar dasukai zuwa wajan shan iska, sau daya yasake fita da ita wajan wasanni anan taga Gari sosai, daga nan bai sake fita da ita ko'inaba

Har hutu daya dauka yaqare, yau suna tashi yace ta shirya zasu fita

Cikin zumudi ta shirya, cikin doguwar rigar atamfa launin purple

Mayafi ta Yafa basu wuce ko'inaba Sai wajan siyaiya

Tunda suka shiga wajan suke ta zagayawa, tana binshi abaya, shikuma yana gaba yana amsa waya

Sunfi minti talatin dashiga shagon, ya juyo zaice mata kingama? Saiyaga wayam Babu abinda ta dauka

Kallanta yayi dakyau yace me kike yi ne?

Cikin fara'ah tace ba yawo muka zoba? Wallahi wajan yayi mugun kyau Yaya daddy, tafadi haka tana juyawa tana kallan wajan tareda wara hannayenta

Haushi kashe daddy

Gaba dayama yarasa maganar dazai fada Mata

Yanzu fisabilillahi yarasa Ina zaije yawo Sai wajan shopping? Meyake damun tane Wai?

Fizgar Hannunta yayi, yajata qiiii Sai tafiya suke, saida yakawo ta wajan kayan kwalliya ya tsaya yace kidau abinda kike so gobe zamu wuce Nigerian

Ga mamakinsa Saiyaga ta Bata fuska, tace nagode babu abinda nakeso mu koma kawai

Matso wa yayi dab da ita, yayi qasa da murya kamar me rada yace karki min musu anan, ki dauka mu tafi

Tana zunbura baki ta daukarwa Abba turaruka, ita kuma tadau kayan kwalliya

Shiru tayi tana nazari me momy take so? Sai can tasaki murmushi ita kadai, tasan momy akwai son ado, kullum cikin kwalliya take, Dan haka tajuyo ta cewa daddy zamuje wani wajan

Shikuwa Kallanta yake, yaga tana Abu kamar me jinnu, inba hakaba kiyi shiru kina tunani kuma ki saki daria ke kadai? Wani abinma de sai yara

Zagayawa ta dinga yi awajan saida suka zo wajan saida yari, ta nuna masa wata hamshaqiyar sarqar gold tace adauko mata ita, me wajan kuwa ya miqo mata ita tare da Dan kunnan ta, sai ta kuma daukan Zabe na azurfa me kyau, sai kuma wani zoben Amma shi na gold ne, ta gwada ahannun ta, sannan ta cewa daddy tsaya anan Ina zuwa

Wajan kayan maza ta nufa ta dauko masa gajerun wanduna, da three quarters, sai best masu shegen kyau da tsada

Tazo tace masa nagama mu tafi

Kallanta yayi, Shiba Wai siyaiyar ce tayi yawa ba a a kawai Yana mamakin sarqa da dankunnan datace abata ne, mezatai dashi? Anya kuwa tasan kudinsu?

Ita kuma Amal Sarai taga kudin sarqar, dubu Dari biyar ne, tunda tasan tazo da daddy tasan cewa batada matsalar kudi

Suna komawa gida tahada musu kayansu duka, tsarabar ta kuma tasaka acikin Jakarta, zoben azurfar data siyo ta kalli aranta tace nasan wannan zoben zaiyiwa Yaya Shahid kyau

Ta daga dayan zoben gold din, tace wannan kuma nasan zaiyiwa shahida kyau, bazan Bata hannu da hannu ba, Yaya Shahid zan bawa yasaka mata da kansa, nasan shahida zatai farin ciki da haka

Washe gari suka Lula nigeria, jirgin su na sauka motoci sukazo taryansa, jama'ah kamar me, dole Sai motar datake da baqin glass suka shiga wato tinte

Government house suka tafi Kai tsaye, motocinsu na sauka shahida ta futo da gudu tahadasu ta rungume su, sai sannu dazuwa take musu

Ba yabo ba fallasa Amal ta amsa mata, saida sukaci abinci suka huta

Sannan yasamu damar ganawa dasu Abba

Amal ce tafuto Fuskarta da murmushi tace miqawa Abba tureren data siyo tace Abba gashi

Yakarba yace masha Allah nagode sosai yata

Ta dauko sarqar data siyo ta bawa momy cikin ladabi tace momy kema ga naki

Duk Akan idon daddy

Momy tace Kai Kai masha Allahu Amma Amal kince nayi kwalliya naje gidan biki kaina tsaye

Gaba dayansu sukasa daria, Abba yadubi daddy yace babana to kaga yanda akeyi

Shikam mamaki ne yahanashi magana,kawai ya sunkuyar da kansa qasa cikin kunya, kenan ita Bata siyowa nata iyayen komai ba, nasa iyayen tasiyo wa, shikuma daya kamata yayi tunanin siyo musu, Shima bai siyo ba

Haka kowa yakoma dakinsa cikin nishadi

Washe gari suka koma gidansu, inda daddy yakoma bakin aikinsa

*** *** ***

Bayan kwana biyu takira maisah zata fada Mata abinda takeji game da daddy, sai maisah tace gobe gobe ma zatazo bauchi takawo mata ziyara

Amal de kawai tajita ne, Amma Bata yarda ba, haka sukai sallama

Washe gari daddy bai kwana agida ba, misalin karfe biyu saiga Kiran maisah tace Amal nazo, na qwanqwasa gidan maigadin bai budeba, Amal cikin mamaki tace wanne gida maisah?

Cikin daria maisah tace gidanku mana, ai aguje Amal tazo tabude mata gidan suka rungume juna

Suna shiga ciki aka Bude babin fira, tare suka shiga kitchen suka hada abinci mai rai da lafiya, sannan suka koma falo sukaita firar su

Maisah tace inajinki yar damagaram, Amal tayi Ajiyar zuciya tace maisah tunanin sa nake, idan na zauna ni kadai banda aiki Sai tunanin murmushin sa, da maganar sa

Koya batamin rai Ana jimawa zan manta inyita tunanin sa

Maisah takama hannayenta tace wa kike nufi Amal?

Kai tsaye tace daddy maisah

Amma shi baya sona, Bana gabansa, maisah tunda nake dashi bantabajin yakira sunana ba, bayamin magana saide inta kama dole, nikuma a jinsa birgeni yake wallahi

Maisah tace Amal, kin kamu da mahaukacin kaunar mijinki

Zare hannayenta tayi daga cikin na maisah tace tayaya? Tayaya hakan zata kasance maisah?

Mutumin daya tsani inyi masa magana zan kamu da soyaiyarsa?

Maisah saboda nafita waje Ana ruwan sama nayi wanka, shikkenan yakori maigadin gidan, Wai nice zan dinga budewa tunda na zabi nuna wa maza jikina

Arana saina kirashi yafi sau nawa, Amma shi Koda wasa ban taba ji yakirani ba, kullum cikin Zaman hakuri muke nida shi

Maisah ce tasake riqo hannayen Amal tace, to Amal koma de menene, kina kaunar daddy, yanzu ai yarage namu, Wajan ganin mun shawo kansa yadawo kan layi, Koda wasa kada ki nuna masa kina sansa, Dan mazan yanzu sunce suna sanka ma Yaya aka qare, bare basu nuna suna soba,

Sannan kome zakiyi masa kawai kiyi abisa ke bakisan kinyi ba

Kidinga jansa da fira yanaso ko bayaso, sauran maganar kuma kawo kunnanki kiji

Rada maisah tayi mata, tace kin gane de, ke nida nake budurwa ma nice me gwada miki wadannan dabarun?

Maisah kin tabbatar idan nayi haka zai Soni Shima?

Sosai ma kuwa Amal, ki jarraba kigani

Amal tace Toshiknn, aikuwa zan aiwatar maisah

Haka suka tafi Dakin Amal, suka barbaje kayan akwatunan ta, maisah ta dinga ware mata wasu daban, tana qara wayar mata dakai

Sannan suka futo, suka Sha firar su, dazata tafi Amal tayi dibi dibi tarasa me zata Bata, tace maisah mezan baki?

Acikin gidan nanfa tunda nazo kudi nawa na kaina ban taba riqe wa ba, baya bani, maisah tace keni kin isheni da mitar mijinki, tsakanin ku, lokacin dazaku fara love bawanda yasani

Daria Amal Tasa, cikin ranta tana darurar aikata shawarar da maisah ta Bata

Saida ta raka maisah gar gate, sannan tadawo gidan ta zauna afalo, tana tunani, Wai ita keson daddy, mutumin dabawani kulata yakeba banda ganganci irin na zuciyar ta

Tashi tayi, tashige daki tafara hada kayanta tana gyarawa, afili tace daga yau zan fara kawo canji awajanka daddy

Nagaji da wannan rayuwar

Tunda kayi gangancin dana soka wallahi kaima saika Soni

Zakasan ka shigo hannun yar mutanan Niger

Tana ta magana afili tana shirya kayan acikin wardrobe

(Sharhi please)

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

20

Bayan tagama jera kayan, ta tsaya ta kalli Dakin, nan tacire Dan kwalin kanta tayi wulli dashi, tafara gyara Dakin, tashiga toilet ta wanke ko'ina

Sannan tasaka turaren wuta me shegen qamshi adakin, tadauko kayan data siyawa daddy a Germany tatafi dasu dakinsa

Cikin wardrobe dinsa ta Bude tasaka masa aciki, sannan tahau gyara Dakin

Gadon tafara gyarawa tayi shara tayi mopping, taje toilet din nanma ta wanke shi ta gyara tsaf, hatta turarukan dasuke kan mirror saida ta sauya musu tsari, sannan tasaka wani turaren wutar mai qamshi daban

Nan da nan Dakin yayi hankali, kitchen taje ta gyara ko'ina, sannan tadawo falo nanma ta gyara, Gaba daya gidan qamshi ne ke tashi, daban daban

Saida tagama gyara ko'ina sannan tashiga kitchen tahada kunun Aya dayaji kayan qamshi, tadauko kwakwa da madara tahada Lemon kwakwa, tayi shinkafa fara dataji Karas aciki, sai kuma miyar ja da naman kaji

Takai komai dining ta jerasu, sannan tashiga dakinta tayi wanka, tana futowa daga wanka Ana Kiran sallar magrib, tayi sallah, sannan taje gaban madubi tafara tsarawa kanta kwalliya

Gashin kanta ta taje tayi fakin, ta Bude kayan data gama shirya wa dazu, wanda maisah ta ware mata, ta janyo wata Riga da wando tasaka, ta kalli kanta a madubi, tace Ina Bata yiba, tacire ta, tadauko wata Riga ja, iyakarta gwiwa, taduba takalmanta ta dauko wani baqi me shegen tsini tasaka, ta bude jikinta da humra

Sannan tafuto falon ta zauna tana kallo

Aranta tace yanzu duk wannan shirin idan bai zoba Yaya zanyi?

Yatashi a banza kenan fa ko?

Wayarta ta duba gaba daya batada number sa, afili tace kinyi sakaci kinyi sakaci Amal, ya Allah Kasa yadawo gida yau

Har wajan karfe tara shiru Bai zoba

Nanfa hankalin ta yafara tashi, ta tashi tsaye tana zagaye cikin falon da Wayarta ahannunta

Tara da kwata nayi, taji alamun shigowa gidan, saurarawa tayi, saikuma taji alamun rufe gate

Ta window ta leqa, ta ganshi tare da wasu mutane, da alama magana suke, saida suka gama tattaunawa sannan taga dayan yabude musu gate din sun fice, shikuma ya juyo yanufo cikin gidan da yar qaramar jaka ahannunsa

Gabanta ne yake faduwa, me zatayi yanzu? Karfa yamata kwarjini, cikin ranta tace Amal daure daure Amal kada komai ya lalace

Matsawa tayi Dasauri tabar wajan, Takoma tsakiyar falon tana zagayawa alamun tanada damuwa

Yana turo kansa cikin falon wani irin qamshi yadaki hancinsa, baisan lokacin daya lumshe idonsa ba

Tana dago kanta ta ganshi tasaki murmushi tatafi Dagudu ta rungume shi, tana cewa Yaya daddy oyoyo, nayi missing dinka

Tana riqe dashi tadago kanta ta kalleshi tace tsoro nakeji ni kadai tun jiya bangankaba, inata jiranka

Kasa magana yayi, Gaba daya ta cika shi da mamaki, saide wata irin nannauyar Ajiyar zuciya dayake saukewa

Itama Sarai taga yanayin daya shiga, Dan haka takama hannun sa ta riqe tace muje kayi wanka Kaci abinci

Kamar dolo haka yake binta, saida takai shi har dakinsa, sannan ta karbi jakar hannun sa ta ajiye

Babbar rigar sa takama zata fara cirewa tace masa, daga hannun mana Yaya daddy

Shide kawai binta yake da kallo, me yarinyar nan take shirya wa?

Tana cire masa rigar ta nuna masa toilet tace to bissmillah ko

Tajuya tafi ce daga Dakin

Bayanta yabi da kallo yanda hips dinta yake juyawa acikin rigar

Tana rufe masa kofar ta jingina da Jikin kofar Gabanta yana faduwa, Amal Ina kika samo wannan qwarin gwiwa? Saida tatabbtar yashiga wanka sannan Takoma Dakin, Akan gadon taga ya zubar da kayan daya cire, tayi sauri ta dauka ta ajiye shi, sannan taduba cikin kayansa zata dauko masa wani kayan, taga kaya birjik aciki, wani wajan iya manyan kaya ne kawai, wani wajan suit wani wajan kuma qanana, rasa wanda zata dauka tayi aciki, sai ruwan ido take, idan tadau wannan saita maida ta dauko masa wani, daga karshe de ta dauko masa wando three quarter kalar Ja, sai rigar ta dauko masa baqa, ta ajiye Akan, jakar daya shigo da ita dauke zata saka masa Akan bedside drawer, Garin dauka mirfin jakar ya bude, daloli tagani aciki masu yawa, ta jinjina Kai, ita tunda take Bata taba ganin kudi hakaba, mayarwa tayi ta rufe, ta ajiye jakar sannan tafi ce zuwa falo

Saida yabata lokaci yana wanka sannan yafuto, da kayan data ajiye masa yayi tozali, baisan lokacin dayasa murmushi ba, wannan yarinyar? Hmm

Kayan yadauka yasaka sannan yafara feshe jikinsa ta turare, turo Dakin Amal tayi tadawo, tana addu'ah aranta Allah yasa de yasaka kayan, aikuwa saitaga yasaka din

Jingina tayi da kofar Dakin ta zuba masa ido tana murmushi

Sannan tace Amma Yaya daddy wannan kayan sunyi ma kyau sosai

Tatako ahankali zuwa gabansa takamo hannun sa, hannun yabi da kallo yakasa magana, tace muje nabaka abinci, hannun su sarqe da juna suka sauka qasa sunyi kyau kamar kasacesu ka gudu

Har dining din takaishi, memakon ta zauna akujerar datake fuskantarsa, a a saita zauna akujerar gefensa, harda qara matso da kujerar, tafara zuba masa abincin, sai Kallanta yake yanda take komai nata cikin nutsuwa, gabansa ta ajiye abincin, sannan ta tsiyaya masa kunun a yar, tazuba masa ido tana kallansa

Abincin yafara ci cikin nutsuwa, yana ci acikin ransa yana masha Allah

Yanaci dazaran yadago kansa saisu hada ido itadashi, kamar wasa taji yace "meyasa bazakici abincin ba?"

Tace no banjin yunwa yanzu saide zuwa jimawa

Bakinta yake kalla yanda take motsa shi, Dan qanqani dashi

Dayawa yaci abincin, yature sauran, dasaurin ta ta janyo flate din tace haba Yaya daddy dubafa saura Dan kadan ka cinye, please daure ka qarasa kaji?

Tafadi hakan da sigar rarrashi

Jiya yi wani Abu ya tsirgo masa tun daga kansa har zuwa tafin kafarsa

Babu musu yadauki spoon din zai qarasa abincin, tayi sauri ta dora Hannunta Akan nasa tace barshi nabaka,

Debo abincin tayi ta nufi bakinsa dashi , tanaji jikinta yana taba nasa, saida ta qara matso wa jikinsa da niyya take goga masa nashanunta ajikinsa

Ahankali yabude bakinsa tazuba masa abincin, tana cewa yauuuwa, Bakinta dab danashi kamar zatai kissing dinsa

Haka ta dinga bashi yana ci, harya qare, sannan yadauki kunun ayar ya shanye duka na cup din data zuba masa, ya kalleta da wani irin yanayi atare dashi muryar ashaqe yace to naqoshi

Cikin shagwaba tace Kai Yaya Dan Allah, ba kasha wannan dinbafa, ta nuna masa Lemon kwakwar, yace "Aina koshi"

Tace a a gaskya, tsaya kaji, sau daya kawai zakasha, ta tsiyayo Lemon kwakwar takai masa bakinsa

Kadan yadansha, ta kalleshi tace Yaya daddy da dadi ko?

Jijjiga kansa yayi, alamun eh

Aikuwa tabashi yakafa Kai saida ya shanye tass

Sannan yace naqoshi

Kallanta yayi yace kamar naji Ana buga gate Dan leqa ta window

Zuciyar ta daya tatafi wajan windon

Batasan wayo yayi Mataba

Yana ganin tashinta ya kalli wandon jikinsa, kamar zaiyi kuka yace nashiga uku, meyake shirin faruwa da nine?

Aguje yatashi yayi sama, yana tsoron karta juyo taga halin dayake ciki, yana zuwa Dakin yashige toilet

Amal kuwa tana waigowa zata fada masa babu kowa, taga bayanan, da mamaki tabishi Dakin sa, tana shiga Dakin taji Motsin ruwa a toilet

Bakinta ta rufe da hannunta saboda Kar dariyar datake ta futo fili, tace waya fada Maka barno gabas take, tajuya takai kwanukan abincin kitchen ta wuce daki ta shirya ta kwanta bacci

*** *** ***

Washe gari tunda tayi sallar asuba Bata koma bacci ba, Bayan tayi karatun alqur'ani da kazimi Tafita ta gyara gidan, gida yadau qamshi kamar ba gobe, kitchen ta nufa tahada musu breakfast, madara ta dama tayi musu kunun madara da kwakwa, sai fruit salad, da wainar semolina

Daki tashiga tayi wanka, tasaka Riga da sket qanana, sket din iyakarsa gwiwa, sai rigar yar qarama daga sama kana iya hango kirjinta, daga qasa kuma bata gama rufe mata cibiyarta ba, Ana ganin shafaffan cikinta

Gashin kanta tasaki ko daure shi batayiba taje falo tana jiran futowar daddy

Shiru shiru har goma ta wuce bai futo ba, Dan haka ta tashi taje Dakin, ganinsa tayi yana kwance yana bacci, tsayawa tayi tana kallan tsantsar kyau irin na daddy, cikin ranta tace ya Allah Kasa mutumin nan ya Soni kamar ba gobe

Gyaran Dakin tayi, sannan tashiga toilet ta wanke Tasa turaren wuta, tafuto, tana sakawa Dakin ma taga yayi juyi yaja fillon dake gefensa ya rungume shi

Shikuma mafarkin ta yake, gatanan tana kwance ajikinsa zata tashi yaqara rungume ta, Amma Kuma yakasa yimata magana

Qamshin turaren wutar dayaji ne ya farkar dashi, ahankali yabude idonsa, dede lokacin Amal tajuyo, idanunsu suka sarqe dana juna

Ido yazuba mata yakasa janyewa, meyasa nake Abu ne kamar wani wawa cikin kwanakin nan? Duk a saboda ke

Murmushi tasakar masa tace Yaya daddy Ina kwana?

Yace "lafiya"

Yatashi yashige toilet din

Tana mopping Dakin yafuto daga toilet daure da towel a'iya qugunsa, duk jikinsa awaje, kallansa tayi akaro nafarko ahaka, Dasauri ta janye idanunta daga kallansa, gashi ne dayawa a kwance akirjinsa

Gabanta yana faduwa, tadau ko masa kayansa ta ajiye Akan gadon, takasa hada ido dashi, Shima ya lura da firgicin datake ciki, Dan haka ya matso kusa da ita sosai daga Bayanta, yadan rankwafa dede tsawon ta, yakai bakinsa saitin kunnanta

Cikin aji da nutsuwa yace "kingama aikin, kokuma in temaka miki?"

Maganar ce tazo mata wani iri, shi dinne zai taimaka mata? Tab Lalle in hakane aikinta na kyau

Dasauri tace a a... Nagode, saika futo, tayi wuf tafi ce daga Dakin

Yabita da kallan murmushi

Juyawa yayi wajan mirror ya kalli kansa yanda yake murmushin

Afili yace meyake damunane? Wannan yanayin da nakeji ko Akan salma banji Shiba

Shiryawa yayi cikin sauri, yafuto qasa

Yauma tare suka ci abinci, kowa yana satar kallan dan'uwansa dasun hada ido kowa saiya kawar dakai

Suna gamawa Takoma kujera ta zauna, Shima daki yashiga yabaje takardu zai fara aiki, kawai kuma saiya fasa yadawo falon Shima, hannun sa ta kalla taga takardu da wannan jakar dayazo da ita

Zama yayi anesa da ita kadan, ita tana kallo shikuma yana aiki, yana cike takardu yana satar kallan ta, ita kuwa Bata sani Bama

Yaya daddy Dan Allah Dan aramin wayarka, dago kansa yayi ya kalleta, Babu musu ya miqa mata wayar, tana amsa number ta tasaka aciki takira, Kiran na shigowa Wayarta tayi saving number sa

Sannan ta dauki number momy, data Shahida da Abba, already tanada ta anty mufy

Bashi wayar tayi, tace gashinan nagode, ina zuwa, ta tashi tashige dakinta

Yana ganin shigarta yadauki wayar Tata, yaduba wayarsa yaga number ta tasaka aciki tayi kira

Sake Kiran wayar Tata yayi, yazubawa wayar ido ganin

"my d"

Yafuto barobaro Akan screen din wayar, me kenan? My daddy? My darling? My dear?

Motsin ta yaji yayi sauri ya ajiye wayar ya sun kunyar dakansa kamar bashiba

Akwatin daya shigo da ita jiya yatura mata Gabanta, kallan mamaki tabishi dashi tace na menene Yaya daddy? Kai tsaye yace kudinki ne

Tace kudi kuma? Girgiza kansa yayi yace haqqinki ne amatsayin ki na matar gorvnor, bakida banki shiyasa nakawo Miki duka

Mamaki ne yakamata, ita Amal itace da wannan kudin?

Dagowa tayi cikin murmushi da Jin dadi tace nagode Yaya daddy

Yace bani ne nabaki ba, wannan haqqin government ne

Tace nasani but babu abinda zanyi dashi, kayi amfani dashi wajan ciyar da yara yan primary abinci duk ranar juma'ah

Kallanta yayi da tsananin mamaki, wacce irin yarinya ce wannan?

Kafin yayi magana ta nuna masa wata takarda acikin takardun gabansa tace Yaya daddy wannan ta menene?

Cikin mamakinta yace, sunayen dalibai ne dazamu tura qasar waje domin su qaro karatu

Daria tasaki tace eh gaskya ka kyauta Allah yatemaka yatayaka riqo

Yace amin, idansa akanta

Awannan Rana haka suka wuni cikin nishadi, haka tasashi a gaba taita tambayar sa abubuwa Akan mulkin su yana fada Mata

*** *** ***

After one week

Yana zaune a office dinsa, yayi Nisa cikin tunanin ta,

"Yaya daddy oyoyo, nayi missing dinka "

Maganar tace take masa yawo acikin kunnuwansa

deputynsa yazo yakawo masa wasu takardu yace ranka ya dade!

Ranka yadade!!

Ranka yadade!!!

Yafada da Dan karfi

Firgigit yayi yadawo daga duniyar tunanin daya tafi

Yace ranka yadade wannan takardun hajiya ne, angama hada komai harma anfara rabawa yaran kamar yanda tabada umarni, sauran kudin kuma suna cikin account dinta kamar yanda kace abude asaka, inyaso duk Bayan wata saita dinga turowa

Ajiyar zuciya yasauke Yakalleshi yace yanzu na wata nawa aka dauka? Rissinawa yayi yace andau na wata shida

Na Rabin shekara kenan?

Eh ranka ya dade na Rabin shekara, daddy yace ok zaka iya tafiya

Yana fita wayar daddy tadau qara yana dubawa yaga momy ce, tace yazo gida shahida ba lafiya

Dasauri yatashi yace ganinan zuwa momy

Lokacin dayaje gidan harta samu bacci, yadubi momy yace momy Wai jikinne?

Cikin jimami tace shine daddy, shahida tacika tunani Akan Yaron nan dan'uwan Amal, nace ta rage tunani Amma taqi ji, kuma nace abbanku yayi wa mahaifinsu magana yace a a

Jinjina kansa yayi yace Allah yasawaqe insha Allah komai zaizo qarshe

Momy tace to Allah yasa

Yace bari naje gida zuwa dare zan dawo insha Allah kafin nan tafarka

Tace to daddy nah

*** *** ***

Karfe tara yashigo gidan, yana zuwa yafada kan kujerar falo yacire hularsa yayi wulli da ita, Sumar kansa ya hargitsa, Wai wannan Yaron meyake ji dashi ne zai kama yakashe masa qanwar sa?

Idanunsa suka kada sukai jajir

Amal ce tabude kofar dakinta ta futo, tace Yaya daddy sannu da zuwa

Be amsa mataba yatashi yafara dosota

Tsorata tayi da ganin yanayinsa, tafara Ja dabaya har suka je kofar dakinta

Idanunsa jajir yanuna ta da yatsa yace "ki fadawa wannan Yaron, wallahi tallahi idan ya kuskura qanwata ta rasa ranta a dalilin sa, sai nadau mummunan mataki Akan ku, dagake harshi zan hadaku in kulle

Dafe kanta tayi da Hannunta, shahidan datake tunanin yanda zata shawo kan Yaya Shahid ya kula ta, akanta ake mata wannan tozarcin

Dago kanta tayi tace, naji Yaya daddy, Amma please kadena aibata yayanah agabana, yanda kakeji da shahida haka nake jinsa acikin zuciyata

Cikin tsawa yace karki sake ambatar wannan Yaron agabana, ok wato kina jinsa azuciyarki, kenan sansa kike, kaunarsa kike

Cikin haushi da bacin rai tace, Yaya daddy sansa nake, kuma aurensa zanyi, Dan Allah kayi abinda zakayi

Tajuya cikin daki tana kuka, rufe kofar Dakin tayi tana wani irin kuka me ciwo, wato ita tana Nan tana haukan sansa shi zuciyar sa tana bashi Shahid takeso

Lalle kuka ma rahma ne, Dan dabatayi ba, inaga saita samu matsala

Shima daddy Juyawa yayi yakoma dakinsa, yafada kan gado

Da aurensa da komai Amma tana San wancan Yaron, me zai nuna masa? Meyasa shi bazata soshi ba Sai Shahid?

Binjimar jikinsa yacire yayi wulli da ita, sai huci yake shi kadai

Awannan dare haka masoyan biyu suka Kasa rintsawa kowa yana tunanin dan'uwansa

*** *** ***

Tana idar da sallar asuba, tadau Jakarta tazuba kaya kala biyu aciki, ta nayi tana share hawaye, saida Gari yayi haske wajan karfe takwas tatashi taduba ko Ina tayi batada ko sisi, Wayarta ta duba taga tanada sauran kudi aciki dubu biyar da Dari biyu

Ahankali tafuto falo taci babban hijabi, har taje harabar gidan wani tunani yafado mata, tadawo ciki tadau niqab dinta ta daura, sannan tafi ce daga gidan Bata zarce ko Inaba Sai tashar Mota

A bangaren daddy kuwa karfe goma yatashi, yayi shirin office yafuto domin ganin Yaya Amal tatashi

Yana futowa falo yaduba dining yaga wayam Babu komai

Dakinta yashiga Dasauri, saide har toilet yaduba babu ita babu alamar ta

Kamar mahaukaci yayi hanyar kitchen nanma batanan

Harabar gidan yaduba still nanma batanan

Gidan yadawo yaduba lungu da saqo batanan

Ahankali yazame yafadi jagwab aqasa, Idanunsa yacika da qwallah, gumi ya wanke masa fuska

Kirjinsa yaji yariqe, yaji numfashi yana gagararsa yi

Cikin ransa yafara maimaita kalmar

Innalillahi wa inna ilaihir raju'un

Comments and share please

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

21

duhu duhu yake gani, hakan yasa ya rufe idonsa yana maimaita hailala cikin ransa

Bade yarinyar nan guduwa tayi ta barshi da halinsaba

Daqyar yakai kansa daki, yakira jb awaya

Kan gadon ya kwanta kansa na wata irin sarawa nan da nan zazzafan zazzabi ya rufeshi, yashige cikin bargo yana karkarwar sanyi

*** *** ***

Tana zuwa tasha taga mutane kowa yana harkar gabansa, jama'ah kamar ba safiya ba, anan taga amfanin niqab, domin kuwa dabata futo dashi ba da tuni anganeta, inda a jigawa ne Babu wanda zai Santa, Amma nan, mutane dayawa sun Santa

Me adedeta ta kalla tace Dan Allah bawan Allah kaini shagon da ake saida Kati

Mai adedeta yace haba hajia, maganar gaskya to kudinki ya qaru

Tace babu matsala, nide kaini

Har gaban shagon inda ake saida katin yakaita, yace sallameni hajiya

Juyowa tayi tace Dan Allah kayi hakuri Ina zuwa

Wajan me shagon taje tace Dan Allah zakasai katin? Wayarsa ya dauko Yace Fado number's din Katin

Tace no transfer nake nufi

Yace nawane kudin? Tace dubu biyar ne

Yace to gaskya duk nera dubu Dari takwas muke siya, kinga kudinki yakama dubu hudu kenan

Tace badamuwa

Kati yabata yace ga number ta nan ki turo

Diri Diri tayi, tarasa ya zatayi, saboda Bata taba yiba, tace a a ga wayar katura da kanka

Karba yayi yasaka number yace nawane pin din transfer din?

Tace bansaniba wallahi ban taba yiba

Yace tab hajia kice aikin naki ba qarami bane, to Bari abude miki

Me adedeta ne yasaki hon

Tajuyo tace Dan Allah kayi hakuri bawan Allah, so nake yabani kudin saina baka

Me shagon ne ya kalleta yace, nawane kudin nasa hajiya?

Itama ta dubi me adedeta tace nawane kudin?

Yace Dari biyar

Me shagon yadauka yabashi, Shima yayi transfer yabata dubu hudu, tace miqa masa Dari biyar din tace gashi

Yace haba hajiya babu komai kije kawai, ainaga kina halin buqata ne, kallansa tayi sosai tace nagode bawan Allah, Dan Allah Ina zan samu motar jigawa?

Yace muje na rakaki, tana bin bayansa sukaje har wajan lodin motoci, taji Ana jigawa, jigawa, dutse, ina na dutse

Tace masa nagode bawan Allah, Allah yasaka da alkhairi, Yaya sunanka Dan Allah? Yace sunana hamza tace to ngd Malam hamza

Tana zuwa tace jigawa zata, aka Bata waje ta zauna, aranta tace gara in nemi ruwa insha Dan tafiyar ba qarama bace, futowa tayi zata fice condasta yace malama Ina zaki, saura mutum daya Mota ta tashi, tace ruwa nakeso

Hannu ya miqo mata yace kawo a siyo miki, Dan idan kikaje wajan nan za'ai tunanin wani Abu zakisa hajiya ko bomb haka, saboda kinci wannan uban hijabi ga liqabi

Itade kudin tabashi Takoma motar, yana kawo Mata ta karba tasaka a cinyar ta

Ba'a jimaba Mota ta cika aka fara hada kudin Mota tace nawane kudin?

Yace kudin ki dubu daya da dari biyar

Tadau ka tabashi

Sunyi Nisa atafiya sosai, wani yaro a cinyar maman sa yadubi Amal Yace anty budemin

Kallansa tayi taga Bobo ne ahannunsa, ta karba ta Bude masa, tana bashi yace kema ki Bude idonki irin mamana

Matar ce ta bige masa baki, tace Umar nahanaka surutu bakaji ko? Ta dubi Amal tace nagode baiwar Allah Dan Allah kiyi hakuri

Murmushi Amal tayi tace a a rabu dashi babu komai

Matar tasake cewa Lalle kin ciri tuta, wannan Bobo tun ranar juma'ah aka Raba musu shi a school Amma yaqi Sha, sai zai Bude saiya fasa, gashi yaude anbude shi

Murmushi Amal tayi tace Allah Sarki

Wani ne daga baya yace ai ance matar gwamna ce tace a dinga rabawa yara ko

Matar tace eh wlhy ai ta kyauta wallahi

Gabanta ne yafadi, kenan.. Dama Yaya daddy da gaske yake wannan uban kudin nata ne?

Kenan maganar data fada masa harya aiwatar da ita

Jingina tayi da Bayan kujerar datake zaune ta lumshe idonta

"kingama aikin, kokuma in temaka miki?"

Maganar daddy ta Fado mata arai, hawayen idonta ta share afakaice, yanzu bala'in datake ji na qaunar daddy haka shahida takeji? Harna shahida yafi nata yawa? Akan soyaiya harda su hawan jini? Amma still Yaya Shahid yaqi kulata?

Sukuwa wanne irin yayu Allah yabasu? Daddy baya sonta, Shahid bayasan shahida

Ajiyar zuciya tayi, insha Allah zan dedeta tsakanin su, shikuwa wannan yaje ya qarata da halinsa

*** *** ***

Har cikin Dakin jb yashigo, ganin mutum yayi a kwance asaman gado yana karkarwar sanyi, cikin zolaya yakama bargon yace maigirma gwamna ya akayi?

Wani irin zafi ne yabugoshi, Dasauri yace subhanallah

Daddy? Meyasameka? Me akama? Ina Amal din take ta barka haka Kai kadai?

Cikin karkarwar sanyi yace jb nashiga ukuna jb

Subhanallah daddy kana fadar min da gabafa, Dan Allah menene?

Shiru daddy ba amsa

Dagoshi jb yayi, yace daddy meyake faruwa, meyafaru da abban?

Kuka daddy yasaka

Abinda jb tunda yake dashi bai taba ganiba, yace innalillahi daddy waye ya mutu Dan Allah?

Rungume shi yayi yace jb tatafi, ta gudu ta barni, wallahi bazan iya rayuwa batare da itaba

Jikin jb ne yayi sanyi, yana kallan daddy, Amal din da ake cewa za'a saka itace yau ake kuka akanta?

Bubbuga bayansa yakeyi alamar rarrashi yace Haba daddy calm down mana menene abin kuka? Mekayi mata?

Saboda nayi fada Akan wannan Yaron shine ta rama masa

Jb yace wanne yaro kenan?

Kai tsaye yace yayanta Shahid, wanda shahidan momy take so

Jb yace to meyasa zakai mata fada akansa, ba yayanta neba?

Da sauri yadago yace yayanta ne Amma ai da aure atsakanin su, Wai harda cewa tana Sansa, kenan ni Bata sona

Daria ce takesan kwacewa jb, yace kayi hakuri, Amma tunda ka lura bataso saika dena fadan

Kamar itace agabansa cikin zafin rai yace kuma saita tafi tabarni?

Jb yakasa boye dariyar sa, dole saida ya murmusa sannan yace yanzu Ina taje? Daddy Yace bansaniba jb, nasan tsabar tsanar datamin ne yasa ta gudu

Jb yace kuma yazaka zauna haka? Muje gidan momy mu duba idan Bata nan Sai Akira commissioner of polis yasa atare ko wacce hanya aduba

Yace bazan iya tashiba jb kirjina ciwo yake

A a daddy daure muje, daure kaji, yafadi hakan yana kokarin dagashi, haka suka fice daga gidan suka nufi gidan momy, wayarsa ya dauko akaro na farko yafara Kiran number ta, Amma is switch off

Suna Zuwa gidan, jb yagaisa da momy, ta dubi daddy tace shikuma wannan me aka masa?

Cikin karyaiyar murya me kama data masu kuka daddy yace momy Bata....

Bai qarasaba jb ya tare zancan da fadin, bayajin dadi ne, Wai abinci zaici ya kwanta yahuta

Hararsa momy tayi tace kabar matarka agida kazo Nan neman abinci? Ta tashi tayi kitchen

Atare suka kalli juna shida jb kenan Bata zoba

Number commissioner daddy yanema cikin sauri yace aduba duk wata Mota dazata jigawa daga bauchi idan anga mace wata yar fara, bazata wuce shekara Sha takwas ba, to adakatar da motar

Cikin girmamawa ya amsa da angama sir, abinka da waya tuni aka dakatar da ko wacce Motar dazata shiga jigawa

*** *** ***

Suna gab da shiga cikin dutse aka dakatar da motarsu, Dan sandan ya dubi direban motar yace Dan Allah sorry fa zamu duba wata mata ne

Gabanta ne yayanke yafadi, Karde ita daddy yasa adubo

Nanta fara salatin annabi acikin ranta

Dan sandan yaduba babu ma yarinya a motar Sai mai niqab nan yace baiwar Allah Dan Allah Dan Bude fuskar ki

Gabanta yana dukan tara tara ta kama niqab din zata cire, me motar yace haba oga, yanzu kuma idan matar aure cefa?

Dan sandan yayi shiru Sai can yace hakane to shikkenan kawai ku wuce

Wata wawar Ajiyar zuciya tasauke, suna shiga dutse tahau motar dazata kaita maigatari

*** *** ***

Har dare Ana bincike babu matar da ake nema, Dan haka suka sanar da daddy daya Kasa zaune yakasa tsaye shida jb

Ana fada masa ba'a ganta ba Jiri ya debeshi Sai gashi yaraf Akan kujera, jb yace ya Salam, doctor yakira, yazo yaduba daddy, yana gama duba shi yace ranka ya dade zamu turaka zuwa India asake duba lafiyar ka, saboda jininka yahau sosai

Duban doctor din yayi yace zansa lokaci naje, thank you zaka iya tafiya

Yana fita, daddy ya lumshe idonsa, yarinyar nan zata kasheshi

Commissioner ne yasake Kiran wayar daddy, cikin sauri ya amsa yace anganta ne?

Yace yallabai gaskya babu labari abinda yafi shine ka turo number Wayarta, saimu tuntubi number muga inda me wayar take,sannan dazu anga wata yarinya ne niqab afuskar ta, but ance matar aure ce shiyasa muka barta suka wuce

Dasauri ya miqe tsaye yace kace niqab? Commissioner yace qwarai kuwa haka bincikenmu ya nuna

Kawai kashe wayar yayi yadubi jb yace tabbas itace, jb yace daddy mata fa masu niqab yawa garesu, yau da ace kaga kayan jikinta, to saimu kafa hujja dashi, hanyar kawai dayace a tura musu number aga inda take, nakega hakan shine zaifi bamu tabbacin inda take

Duban jb yayi a sheqe yace kanka daya kuwa jb? Number matar tawa zan dauka nabasu?

Daddy yanzu fa babu lokacin nuna kishi, nemanta muke, dole mubi wannan hanyar

Shiru yayi tare da tura number Amma cikin ransa ya qudurta cewa dole yasake mata Sim card

Yana tura musu suka kirashi sukace sun duba, Amma wayar a kashe, Dan haka zasuci gaba da dubawa dazaran anbude wayar zasu sanar dashi halin da ake ciki

Awannan Rana haka daddy yadinga faman kiransu awaya, suna cewa suna nan suna jiran kunna wayar

*** *** ***

Yamma lis na sauka agarinmu, cikin sauri nataka aqafa na qarasa gida, saboda some time bancika son Hawa machine ba, ina shiga gidan nafara ganin umma, haka itama tanajin sallamata tadago Kai tana kallo na cike da mamaki, ina zuwa nafada jikinta, umma tace Amal? Anya lafiya kuwa zuwa haka babu sanarwa?

Nace umma lafiya kalau, ina Yaya Shahid da baba? Tace babanki yafita Shahid kuma yana ciki

Daga murya nayi nace yayanah gani nazo futo

Da mamaki afuskar sa yafuto yana cewa wanake gani kamar Amal? Da murna ta Nace nice yayanah, umma taje takawo min ruwa, tana zama nakoma jikinta nakwanta nayi shiru, umma tunda ta ganni tasan cewa ba kalau ba, tsakanin uwa da da dama Sai Allah

Shahid yace umma karki Bata abinci zanje inkawowa qanwata abin dadi

Nace yauwa Yaya Shahid yi sauri, yana fita kuwa, umma tace Amal inji de kalau din ne kamar yanda kika fada?

Idanuna ne suka kawo ruwa, tana ganin haka cikin ranta tace dama nafada

Dan haka tace naji, kiyi hakuri, kowa dakike gani Amal hakuri yake agidan auren sa, karki sake naji kin fadawa babanku wani Abu tsakanin ki da mijin ki, Sarai kinsan halinsa saide yasake lalata komai

Kaina na girgiza nace to umma insha Allah, tadafa kaina tace yauwa Allah yayi miki albarka

Muna zaune Yaya Shahid yadawo naji shawarar umma haka nasaki jikina mukai ta fira, Yaya Sai daria yake bani, da daddare baba yadawo yaganni, muna zaune afalo dukanmu ya kalleni yace Amal, nace na'am baba, Amal na'am baba, Amal na'am baba, saunawa nakiraki?

Nace sau uku

Ya ki fadamin wannan zuwan naki babu sanarwa idan wani Abu Yaron nan yayi miki insaki agaba kikaini wajansa inci ubansa mudawo gida shikkenan anwuce wajan

Nace baba wallahi babu komai kawai kewarku nayi shiyasa nazo naganku, yace to shikkenan Allah yayi miki albarka nace amin baba

Yace ai muma angama ginan sabon gidan namu, jibi jibin nan mukasa zamuje wajan mijin naki da iyayansa muyi musu sabuwar godia, nace to Allah yakaimu baba yace amin

Saida naje kwanciya ne nafada duniyar tunanin mijina, Allah Sarki Yaya daddy ko Ina yake yanzu? Kome yake?

Haka nakasa bacci banda juyi Akan katifata babu abinda nakeyi

A yayinda daddy ma yakasa zaune yakasa tsaye, yakasa ci Dasha, haka kowanne ya kwana da damuwa

*** *** ***

Washe gari Yaya Shahid yace nashirya muje Inga sabon gidan, muna tafiya ahanya nace Yaya yaushe Wai zakai aure? Yace aure Amal, ba yanzu ba kuma banda wacce nakeso, nace aikuwa Yaya nasan bazaka rasa yanmata ba

Yace da gaske babu Amal, saide ki samomin

Nace aikuwa na samo Maka Yaya wata hadaddiya wallahi, yace wacece? Nace muje gidan nafadama, haka muka qarasa gidan, muna zuwa Naga ko Ina gida yatsaru dakuna har guda biyar, da furniture dinsa da komai anzuba, zama nayi nazuba tagumi a falon gidan, ashe Yaya yana kallo na, yadawo kusa Dani ya zauna yace fadamin qanwata, meyake damunki? Nace Yaya babu komai, yace yaushe kika fara boyemin damuwarki Amal?

Ganin haka yasa nafada masa komai da komai, yace haba Amal, yaushe kawai danya cemin yaro zaki dagawa mijin ki murya? Karki sake kinji? Nace to Yaya, yace Amma Amal daddy yana sanki tunda har yake kishi Akan ki, karkiga laifinsa kinji? Nace to Yaya Anima Ina sansa shine baya kulani, Dan Allah yaya ka daure kaso qanwarsa ko Shima zai Soni, Yaya duk lokacin daya tuna bakasan shahida bayajin dadi, Yaya abinda kayi shi za'a ma, bakasan shahida Shima baya sona

Jikinsa ne yayi sanyi, yace Toshiknn qanwata insha Allah zanyi tunani Akan hakan, nace Yaya shahida tana sanka, idan halinta ne baimaba kana fada Mata zata dena, Yaya a dalilin sanka shahida hawan jini takamu dashi, itace BURINAH awajanka Yaya, ka auri shahida please

Hannayena ya riqe yana murmushi yace to Amal, zan iyayin komai saboda ke, insha Allah daga yau zan fara kula da shahida, Amma fa saboda ke, nace nagode yayanah

Wayata nadauko acikin jakata na kunna ta, nadauki Tasa wayar na saka number shahida aciki, duk yana kallo na, nace gashi kira mana ita

Zubamin ido yayi yana kallo na, yace ni gaskiya kunyarta nakeji wallahi, saide kiyi mata magana saiki bani ita, daria ce takama Amal, Dan haka kawai saita kira shahidan awayarsa tasaka wayar a hands free

*** *** ***

Yaci suit ruwan suminti yana zagaye falon nasu, shahida da momy suna kallansa, wayarsa tayi qara, cikin sauri yadaga yace ya ake ciki? Daga daya bangaren akace, ranka ya dade me number nan munga no cewa tana jigawa state, maigatari local government

Ajiyar zuciya yasauke me qarfi yace ok nagode,

Cikin sauri yajuya zaibar falon, yaji wayar shahida tayi qara juyowa yayi zaiyiwa momy sallama

Kawai yaji shahida tace laaa anty Amal, layin waye wannan kika samu?

Cak yadakata, kenan gida tatafi? Ya tabbata kenan itace mai niqab din da akace angani

Daga dayan gefen Amal tace anty shahida babu lokacin bayani, yanzu de gawaya zaki gaisa da wani

Shahida tace wani kuma? Kafin Amal ta Bata amsa shahid ya karbi wayar tareda sallama, gaban shahida yafadi

Cikin in Ina tace Shahid

Adaya bangaren Shahid yace na'am ammata yajikin naki?

Ai batasan lokacin datasa daria ba tayi cikin daki, momy tabita da kallan farin ciki

Shikuwa daddy hararar Bayanta yayi, wato ita wannan yarinyar ta gyara Tata soyaiyar, Amma shi a dalilin ta Tasa soyaiyar zata lalace

Yasan duk aikin Amal ne wannan, to shikwa idan bai nemi yarinyar nanba ai Sai Allah ya tambayeshi, ficewa yayi da sauri yanufi Mota yana waya da jb Akan anganta

Sakawa yayi aka kawo masa mask irin wadda maza suke sakawa lokacin sanyi yasaka a fuskarsa, banda idonsa da baki da hanci babu inda kake gani

Mutane zasu bishi ya dakatar dasu, yashiga motar da kansa qirar Mercedes Brabus, yadau hanyar jigawa

*** *** ***

Yayi Nisa ahanya police suka tareshi zasu duba boot din motarsa, yana daga ciki ya bude musu suka duba babu komai

Yayi gaba wasu ma suka sake tareshi, ina driving license din ka? Yadauko ya bayar, ina takardun Mota yaudauko yabayar

Dan sandan yace kai gaskya ni banma yarda dakai ba, katashi kaboye fuska kamar barawo, kawai kawo na goro kayi gaba, daddy da takaici ya cika shi yadauko dubu goma yabashi, nan da nan dansandan yafara fara'ah

Yace aaa kace yau nayi babban kamu, zaka iya tafiya, daddy yace nine da godia ai, menene sunan Kane?

Cikin washe baki yasanar dashi, yace to ngd yaja motar yayi gaba

Yana tafiya yakira commissioner yace adakatar da aikin wannan police din

Kuma yasameshi shida dansandan a office next week

Haka yayita tafiya wasu su dubashi saboda Allah, wasu Kuma su karbi cin hanci, haka Shima daya wuce zai bada umarnin dakatar dasu daga aiki

Har ya shiga jigawa, sannan yadena cewa a kamasu, yazo wani Gari kiyawa ruwan motar yaqare, haka yafuto yadaki tayar motar, Kai wannan yarinya ta cuceni, banda yana Santa tayaya zai tsaya wasu qananan yan Sanda suna masa tambayar renin wayo, haka yafuto yaje wani gidan mai yasamu ruwa yazubawa motar sannan yaci gaba da tafiya

Sanadin tsaye tsaye dayayi ahanya hakan ne yasa bai qaraso Garin ba Sai dare, hadari yahadu gabas da yamma, dakyar da tambaya yagane gidan su Amal

Yana futowa daga aka tsuge da ruwa mai karfin gaske, yaqarasa kofar gidan harsun rufe gida, ya qwanqwasa, yaji shiru gashi Ana ruwa, abinka da me zazzabi nan da nan jikinsa yafara rawa

Umma na daga falo taji kamar Ana bugawa tatashi zata fita, Amal da Gabanta yake faduwa tun dazu tace umma zauna Ana ruwa, bari naje nabude

Kafin umma tayi magana tayi wuf tafice daga falon taje bakin qofar ta Bude ahankali

Dashi tayi tozali, ga ruwa anayi, duk yafara jiqa musu jikinsu

Idanu suka zubawa junansu kowa yakasa janye nasa idanun

Juyawa tayi zata koma ciki, yasa hannu ya fuzgota jikinsa

Amal cikin kuka tace Nika sakeni banaso

Kasakeni banas..... Bata qarasaba yayi saurin hade bakinsu waje daya, yanayi mata wani irin mahaukacin kiss

(idan akwai me qorafi zai iya fadamin, Kar amanta da Sharhi please inajin dadin hakan)

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

Tsawon minti biyar suka dauka atsaye, yaqi sakin Bakinta, ruwa duk ya yagama jiqasu

Daqyar Amal ta tureshi Gabanta yana faduwa, wani irin yanayi takeji atare da ita wanda Bata saba Jin kamarsa ba

Kallanta yake sosai kamar yau yataba ganinta

Ahankali yace "sanyi nakeji"

Kallansa tayi, saiya Bata tausayi, daure wa tayi tayi gaba tabarshi anan,tanaso tadan ja masa aji, shikuma dayaga tayi gaba saiya biyo Bayanta

Tana dauke qafarsa yake maida Tasa

Har sukaje cikin falon, umma ce taganta tashigo da mutum Dasauri ta tashi tace a'a kice baqo mukayi, karaam Kaine atafe da wannan Daren?

Yana Dan karkarwar sanyi yace wallahi nine umma, Amma kansa aqasa yakasa hada ido ta ita, tace sannu da zuwa shigo mana, qaraso muje wajan Malam suna ciki shida Shahid

Bayanta yabi suka shige, Amal kuwa da sauri tayi cikin Dakinta, tafada kan katifar ta, tana maida numfashi, me Yaya daddy yake nufi da wannan abin dayamin? Idanunta take juyawa alamar tunani, ahankali takai Hannunta kan Dan qaramin lips dinta tana shafawa

Acan kuwa baba mamaki yayi ta yi dayaga daddy Bayan sun gaisa ne, yace karaamullah ashe kana hanya, Muda muke ta shiri gobe zamu taho muyi muku godia, ai angama gida, sosai yayi kyau muna godia sosai wallahi, daddy da kansa yake sunkuye yace a a babu komai

"dama tace tanasan ganinku ne shine nace tazo Sai nazo mu tafi, saimu tafi gaba daya goben insha Allah "

Abba yace to Babu damuwa Allah yakaimu, Shahid kuje yaci abinci saika hadashi da Amal yaje yahuta

Shahid yace to baba, yatashi suka koma falo,suna zama Shahid yace inasu shahida?

Maganar tabawa daddy mamaki, shi kansa Shahid din yarasa dalilin dayasa yayi tambayar

Murmushi daddy yayi yace "suna lafiya" umma ce takawo musu abinci kadan daddy yaci yace yaqoshi, Shahid ya qwalawa Amal kira, tana futowa yace ki rakashi daki yayi wanka ya kwanta, akwai kaya aciki saiki nuna masa, ni zanje wajan baba, ahankali tace to Yaya

Dubansa tayi tace zo muje

Tashi yayi yabi Bayanta suna Zuwa, yabi Dakin da kallo, shi be taba kwana a'irin wannan Dakin ba, Amma saboda ita yau zai fara, Amma Kuma babu laifi Dakin yayi, Babu tarkace

Ruwan wanka tahada masa a toilet, zai shiga ne yadubeta yace inajin zazzabi ko zan samu magani?

Batace komai ba tafice daga Dakin, Kallanta yayi, yaga alama de har yanzu Ana fishi dashi

Toilet yashiga yafara wanka

Taje wajan umma tace umma Wai zazzabi yake ko akwai magani? Umma tace dama yanda ruwa yadakeshi Kam ai dole

Jeki dauko adaki, kibashi yasha, Amma duk da haka kitafi da ruwa mai sanyi ki temaka masa ya goge jikinsa, zai rage zafin zazzabin

Tace to, tana dauko maganin, tatafi Dakin tana tunanin maganar umma, in temaka masa it means fa nice zanyi masa hakan ko

Itade jiki asanyaye Takoma Dakin, dauke da ruwa da magani, tana shiga yafuto daga wanka daure da towel din Shahid ajikinsa

Batare data kalleshi ba tace ga maganin nan Ina zuwa, tafice

Dawowa tayi dauke ruwa awata yar qaramar baho Sai qaramin towel ta ajiye agefensa

Kallan maganin data kawo tayi, ta ganshi dam ko tabawa be yiba

Kallansa tayi tace meyasa bakasha maganin ba? Idanunsa akanta yace ai baki bani ba

Kai ita tarasa meyasa yake mata wannan abubuwan

Maganin ta ballo guda daya tabashi ahannunsa, ta miqa masa ruwan ya karba yasha

Yadubi ruwan Gabanta yace"mezakiyi da wannan ruwan? "

Kame Kame tafara, tace am.. Um.. Dama fa umma ce tace waika goge jikinka dashi zaka denajin zazzabin

Kallanta yake yanda duk ta rikice, yace ai bazan iyaba, saide in zaki temakamin, kaina ciwo yake kuma zazzabi nakeji, ga sanyi danakeji, har mura duk damuna take

Kallan mamaki tamasa menene abin jero wannan jinyoyi?

Ahankali ta matsa kusa dashi, kusan tayi kusa har tanajin hucin numfashinsa, tsoma towel din tayi acikin ruwan ta matse, sannan tafara goge masa jikinsa

Kallanta yake yakasa dauke idonsa akanta, ahankali yakai hannun sa kanta yacire Dan mayafin data rufe kanta dashi

Yana cirewa kuwa gashin Kanata ya sakko har Saman Fuskarta

Yasa hannu ya maida mata gashin baya

Yaci gaba da aikin Kallanta, jiki asanyaye taci gaba da goge masa Jikin, tagama goge masa ko'Ina sannan tafara goge masa Kirjinsa da duk gashi ya kwanta

Abinda ya lura dashi shine tafi goge wajan, to Kode tana so ne?

Yanata tunani harta gama ta dauke mayafin ta, da ruwan zata fice yayi sauri yariqo Hannunta

Yana riqe da hannun nata yatashi tsaye yamatso dab da ita, yakama Fuskarta da hannayensa biyu bakinsa dab da nata yace "meyasa kika tafi kika barni?"

Gabanta ne yake aikin faduwa takasa wani Motsin kirki

Idonta ne yaciko da qwallah, Bata iya dakatar da zubowarsu ba, cikin kuka tace fada kakemin

Tasa hannu zata goge hawayen,yayi saurin kawar da Hannunta yace "no yakai bakinsa kan kumatunta ya lashe hawayen tas"

Yana riqe da itan yace, "BABY please karki sake tafiya ki barni, kin Riga da kin zama wani bangare na jikina

Yakai bakinsa saitin kunnanta cikin rada ya furta I love you

Ai Amal najin haka batasan lokacin data qwace tayi Dakinta ba, tana zuwa ta rufe kofar harda kullewa

Tafara Tsallen murna, kan gadon tafada Sai birgima take tana murna

Nan take tadau waya ta kira maisah, anan take cewa gobe tazo gida da safe zasuyi magana

Maisah da batasan da zuwan Amal dinba tace lafiya kuwa? Amal tace kede kawai kizo, dahaka sukai sallama

Shikuwa daddy da murmushi yabita da kallo, sai shine ya kawar da bahon, sannan yabude jakar Shahid yaduba wata jallabiya yakasa

Sai adakin baba Shahid yakwana, yayinda masoyan biyu suka Kasa rintsa wa kowa yana tunanin dan'uwansa

*** *** ***

Washe gari Yaya Shahid ne yayi musu komai, yayi wanka, suka shirya, har daki umma takai musu abinci, suna gamaci Shahid yake danyi masa fira haka jefi jefi duk da bawani sabawa sukai ba

Amal kuwa bacci tasha me dadin gaske, saida Gari yayi haska sosai sannan ta tashi tayi wanka, ta kira maisah, sannan tafice wajan umma taci abinci, umma tana hankalce da ita Bata nemi abincin dazata kaiwa mijinta ba, kenan da ba'a Kai musu haka zaiyi ta zama, Kai wannan Yaro yana hakuri

Maisah ce tashigo gidan tana ganin Amal suka rungume juna, Bayan sun gaisa da umma sukai ciki, Amal tabata labarin abinda yakawo ta gida, maisah taita mamaki tace yanzu Wai Dan Allah yana gidan nan? Amal tace wallahi yana ciki maisah ai ingaya miki dayaji bala'i dakansa yafada

Maisah tace meya fada qawata? Tace yana ciki

Aikuwa suka sa daria, maisah tace kice shikkenan de yanzu an wuce wajan, ke wallahi garama da kika taho

Daria nasa nace eh wallahi

Wayarta ce tadau, qara tana dubawa taga shamsu ne, cikin haushi tace nikam nashiga uku nah, Amal tunda mutumin nan yarasaki shikkenan yadawo kaina, yakade min hankali wallahi

Amal tace wakenan? Maisah tace Yaya sham mana

Amal tace alhamdullahi, wallahi wannan Abu yayi, maisah ki aure shi Dan Allah

Kallan mamaki tabi Amal dashi tace Amal kanki daya kuwa, tsohon saurayin kinefa, a a bazan iyaba, Amal tace to menene? Tsohon mijinane? Kokuma a kanmu aka fara? Kinga ni yanzu Yaya daddy nakeso, Babu sham acikin zuciyata

Kiyi tunani maisah, BURINAH Inga kinyi aure kema, Dan haka nide indan tanine karki damu, Allah yasa mudace gaba daya, maisah cikin sanyin jiki tace zanyi tunani insha Allah

Shima yace to tayaya zamu tafi ni ban shirya ba? Ke kinci kwalliya nikuma ko oho

Tace shikkenan jeka, yi sauri

Tana zaune Zaman jiransa ta nayi tana duba agogo hannun ta

Yafuto, ya wuce yaje wajan kayansa

Yana duba qananan kayan dazai saka, yaga sabbin kaya aciki,daukosu yayi, yakalli Amal

Allah Sarki ashe shi ta saiwa wannan kayan lokacin da sukaje Germany

Murmushi yasaki yadauka yasaka

Yadawo Gabanta yadauki abincin yace taso kici abinci, banaso kije kinacin wani Abu agaban mutane

Babu musu tasauko qasa idonta akansa, tana kallan yanda kayan yayi masa kyau

Shida kansa yaciyar da ita, sannan yace Shima tabashi, spoon din tadauka zata bashi yace no da hannun ki nakeso

Haka tasaka Hannunta cikin abincin tafara bashi

Ahankali take bashi abincin yanaci har wani lumshe ido yake

Tana gama bashi ta tashi zataje ta wanke Hannunta, ya dakatar da ita ta hanyar riqe hannun ta yace bari kiga yanda ake qarasa aikin lada

Maida hannun yayi cikin bakinsa yana yana sudewa, saida yagama sudewa sannan yakama Dan ya tsanta daya yafara tsotsa ahankali

Gaba daya yafara kashe mata jiki da wannan salon nasa

Cikin rashin kuzari tace baka gama bane, sai a sannan yadawo hankalin sa

Yacika mata hannun taje ta wanke tadawo Dakin

Kamota yayi yace muje muyi maganar mu tafi

Zama sukai agefen gadon yakama hannayenta ya riqe, yace baby kiyi hakuri Akan abubuwan dasuka faru abaya, naji dazu ma kina fadamin maganar gate, ban kori iliya Dan yamin komai ba, saidan Ina kishin ki, banasan abinda zaisa wani Abu yahadaki da maza, bazan yafewa kainaba

Kiyi hakuri kinji? Banayin komai saida dalili

Sim card ya miqo mata yace wannan sabon layin dazakici gaba da amfani dashi ne, anbude miki account dashi, da sauran kudinki aciki, zaki dinga tura musu wanda na ciyar da yaran nan da kikai alqawari, Bayan wata biyar, saboda ancire na wata shida

Wannan kuma ATM dinane idan kina buqatar kudi Sai kije kicire yanda yimiki

Sannan maganar koya miki Mota, bansan Yaya za'ai ba, shahida tayi aure dasai takoya miki

Amma kiyi hakuri zuwa lokacin da zamu samu fita zuwa wata qasar Sai na koya miki

Amal mamaki yakashe ta zaune, ta dube shi tace Amma Yaya daddy yazaka bani atm dinka? Mezan yi da wani kudi kuma Bayan nawa na wajena?

Yace incase, wasu zasu iya neman temako awajanki saiki dauka aciki kibasu, karki damu, dukiyata Dani kaina nakine Amal

Mun Riga da munzama mallakinki, daddy naki ne halak Malak

Ajiyar zuciya tasauke tace Yaya daddy ni banida wanda zan temaka wa Sai mutum daya dayake Raina

Yace waye?

Tace wanine hamza, daya temakamin lokacin dazan tafi jigawa

Yace ok kice shine ya nuna miki hanyar guduwa ko? Amal tace Yaya daddy ba abinda kake tunani bane, nide kawai Ina San temaka masa ne

Kafada yadago yace saide kisa ayi masa komai Sai afada masa daga kene

Amma banasan ku sake haduwa dashi, tace to Yaya daddy nagode

Agogo ta kalla tace Yaya daddy mu tafi ko? Kallan ta yayi yace wai kina nufin wajan dinner? Tace emana

Yace haba baby tayaya zan barki kije da wannan uwar kwalliyar? Wallahi inkika fita mutuwa zanyi, Wai kinsan yanda nake sanki kuwa?

Dadi yakama Amal sosai acikin ranta

Matsota yayi yana shakar qanshin dake tashi ajikinta yace wanne irin turare kika saka ne? Inshaqa Nima?

Daga masa Kai tayi

Haka yafara bin jikinta lungu da saqo yana shaqar qamshin jikinta, daga nan labari yafara sauyawa, inda tace batasan zancan ba, haka de yabi ya kalallameta saida yasamu abinda yake so

Bayan komai yalafa ne, ya qaqumeta ajikinsa, yanasa mata albarka,cikin rada yace Mata kinji zafin yanzu?

Kanta ta girgiza, wanda azahiri taji zafin Amma ba kamar wancan Karon ba, Amma danta nuna masa dauriyar ta yasa tace bataji komai ba

Daukanta yayi cancak suka shiga toilet zasuyi wanka, inda sukayi suka gama Amma idon Amal a kulle

Saida suka dade suna fira wajan Sha biyu na dare sannan suka koma wancan gidan

Lafiya tashiga Dakinta cikin walwala da farin ciki Shima haka, Babu wanda ya lura dasu, kasancewar akwai sauran mutane yan biki

Kayan jikinta tacire tasaka kayan bacci, Wayarta ta dauka taga maisah ta kikkirata, Bata jiba, saita duba taga ta turo mata message tana fada Mata ansa mata Rana da sham nanda wata daya biki, haka Amal de taita farin ciki Awannan lokaci sannan tayi bacci

*** *** ***

Washe gari aka tafi da shahida jigawa, inda su umma suka karbesu hannu bibbiyu

Ankaita Dakinta, abokan ango suka rakoshi, su nazy nede da okasha, sai tsiya suke musu Wai fada ya zarce soyaiya

Haka Shahid de yakasa tanka musu, shi ya matsu su tashi su tafi koya sake da gimbiyar Tasa

Aikuwa suna tafiya, yacire hula da babbar Riga, ya yaye mata lullubin kanta, yafara janta da fira harta Dan sake dashi, sannan yakawo mata kaji da sauran lemuka sukaci suka Sha, yace ta tashi su gabatar da sallah

Suna idarwa ya kwararo musu addu'ah, sannan yace zata Iya zuwa ta kwanta tahuta, haka kuwa akayi, tana kwanciya Shima yatashi yaje ya kwanta

Shahida tayi tunanin babu abinda zai faru,shiyasa tasaki jikinta tana jinsa yamatso jikinta ya rungumeta , murya kàsa kasa yace amaryata, ahankali shahida tace na'am yace kikwantar da hankalinki kinji ?tace to

Tanaji tana gani yafara lalubarta , duk tatakure ta cure waje daya, tana tunanin wahalar da amal tasha, cikin dabara yace mata duk abinda nayi miki kema kiyimin kinji?

Girgiza kai tayi, yasake cewa amma idan bakimin ba , to zanyi wani abu, tace to

Haka yayi tayi mata wayo har yasamu biyan buqatars

Shahida Idanu suka Raina fata, Amma haka ta daure tayi hakuri, duk da taji jiki sosai

Saida komai yagama wakana sannan yatemaka mata, suka gyara kansu, shahida Sai shagwaba take zubawa, shikuwa Shahid duk ya rikice, sai abinda tace

*** *** ***

After 1 month

Bikin maisah biki yazo, Amal taso daddy yabarta taje tayi ko kwana uku ne, Amma yaqi yarda, dole Sai ranar bikin aka kaisu

Daddy dakansa yagana da mahaifin maisah suka gaisa dashi sosai, dazasu tafi gidan su umma yabashi gudunmawar biki naira miliyan biyu

Haka iyayen maisah sukaita godia

Gidan umma suka wuce, wanda suka dade da tarewa asabon gidansu, Amal da suka hadu da shahida ake ta zubawa juna labari dakyar suka rabu

Haka suka dauko hanyar dawowa saboda dare

*** *** ***

Suna zaune afalo suna breakfast Abba da umma Sai daddy da Amal

Abba yace hajiya opper Shahid ta aiki tafuto, kowanne lokaci zai iya farawa, harma da gida da komai na ma'aikata akwai

Amal naji tace wayyo Abba Dan Allah kace musu su dawo nan gaba daya

Abba yace yata ai wannan ikon yana hannun Shahid, Amma kisani nan da jigawa duk daya

Duk inda suka so zasu iya zama

Tace to Abba, aranta kuwa fadi take Allah yasa Yaya Shahid yayarda su dawo nan

Momy tace to alhaji Babu abinda zamu ce mukam ai Sai godia

Abba yasaki murmushi yayi shiru

Amal ce ta tashi, daddy yabita da kallo

Momy tace bade Harkin qoshi ba?

Cikin yatsina fuska tace momy naqoshi ne wallahi, abincin bayamin tes abakina, qarni ma nakeji

Daddy de yabita da kallan mamaki yakasa magana, tunda shide yasan kalau take cin wannan abincin, Amma Kuma yau tace qarni

Momy tace to jeki kwanta, kokuma kisa adafa miki abinda kikeso ko?

Tace to momy

Ta kalli daddy, ta wuce zata tafi daki, taji Jiri yadebeta, kanta yasara

Nan tafara baya baya alamun faduwa

Daddy ne yatashi Dasauri yaje yatareta, yace lafiya kuwa?

Su Abba ma suka taso, suna fadin lafiya Amal?

Amai taji yataso mata, cikin sauri ta qwace daga hannun daddy, taje toilet taita kwara Amai

Tana futowa ta kwanta Akan gado Bata koma falon ba

Acan falo kuwa Abba ne yasa daddy yakira doctor,daya tashi Kiran saiyasa aturo masa mace, doctor na zuwa suka bita cikin Dakin

Tana kwance, a gado, tana ganin su ta tashi zaune, doctor ta duba ta, sannan tace ta kwanta tahuta

Tajuyo ta kallesu tace alhaji congratulations Her Excellency na dauke da juna biyu na Tsawon sati biyar

Comments

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

26

Daddy najin haka yayi saurin tsugunna wa yayi sujud shukhur

Saida yagodewa ubangijinsa sannan yadago

Abba ya washe baki yadubi doctor din yace a a masha Allah, Wai likita abinda kika fada din hakanne da gaske?

Doctor hauwa tayi murmushi hakane alhaji, haka bincike ya nuna

Abba yace to ai likita kema baza'a barki hakaba, saboda haka kituromin da account number dinki, zakiga kyauta mai tsoka

Cikin farin ciki tace to alhaji insha Allah

Momy ma datake ta farin ciki, tace ai alhaji wannan kyauta Nima baza'a barni abaya ba, ta dubi doctor hauwa tace doctor ki shirya insha Allah dake za'ayi hajjin Bana

Doctor cikin daria tace gaskya hajiya nagode sosai, haqiqa zanso Naga wanne yaro kokuma yarinya za'a Haifa

Momy tace ai mukam duk abinda muka samu bamuda zabi doctor

Doctor hauwa ta gyara glass din idonta tace gaskya ne, yanzu zanje nahado mata magungunan dazata dinga Sha, zai taimaka mata sosai wajan Jin sauqin jikinta, sannan hajiya Dan Allah adena barinta tana ayyuka dayawa, abari Sai cikin yagama qwari tukunna

Momy tace a a karki damu doctor insha Allah za'a kiyaye

Bayan fitar doctor ne, Abba yanata fara'ah yace a a masha Allah Abu yayi kyau, yadubi Amal Yace Amal?

Cikin sauri ta rufe idonta da tafukan hannayenta, Abba yajuya yafice

Momy ta kalleta tace to me kikeso adafa miki ne yanzu Amal? Kanta aqasa cikin kunya tace babu komai momy, banajin yunwa

Momy tace Toshiknn ki kwanta ki huta kinji, itama tafice daga Dakin

Yana ganin fitar momy yahau gadon tare da rungume ta, itama tayi luf ajikinsa

Yashafa Bayanta yace baby nagode sosai

Itama cikin sigar kissa tace a a Yaya daddy Allah zaka yiwa godia

Yace shi nafara yiwa baby, abin kamar almara nine zan baba

Cikin farin ciki ta kalleshi tace kakusa zama daddy ba

Cikin farin ciki yace dama daddyn ne, Amma marar yara

Gaskya bansan wacce irin godia zanyi wa mahalicci naba, yau nine matata take dauke da ciki akaro na biyu

Shafa fuskar ta yayi yace Allah yarabaki dashi lafiya babynah

Amal tasan yatuna da salma ne, yana tsoron itama kada ta mutu shiyasa yayi wannan maganar

Gashin kansa ta shafa tace ka kwantar da hankalin ka, duk wanda kaga yarasu kwanan sane yaqare

Addu'ah zamuyi mata Allah yayi Mata rahma

Cikin sanyin jiki yace amin

Me kikeso asawa Yaron dazamu Haifa? Ina nufin wanne suna kike so?

Jim tayi alamar tunani, sannan tace Kasa sunan Abba idan namiji ne ai yayi ko?

Shima cikin alamar tunani yace eh yayi, Amma nida abinda nake tunani shine musa sunan Shahid

Cikin mamaki tace meyasa Yaya daddy?

Yace saboda yayi jinkirin fada miki yana qaunarki, Sanadin hakan nikuma nasameki

Murmushi tayi tace, Yaya daddy kenan, musa sunan Abba, idan Allah yabamu wani Yaron Sai Asa sunan Yaya Shahid din

Daddy yace Toshiknn, Amma Kuma idan mace ce wanne suna kike ganin yadace mu saka mata

Kai tsaye tace Salma

Kallan mamaki yayi Mata, tace gashi Nima Sanadin ta nasameka, nasamu mijin da bantaba tunanin samun kamarsa ba

Cikin farin ciki daddy yace um me kikace? Dan sake fada please

Babu kunya tace Yaya daddy nace nasamu mijin da ban taba tunanin samun kamar saba

Yace Dan Allah kidena cewa Yaya daddy dinnan haba baby

Tace Toshiknn my dear

Bakinsa yakai saitin wuyanta yayi kissing sannan yace I luv u, tace I love you too

Wayarsa yadauka yakira jb

Daga daya bangaren jb yace abokina ya akai?

Daddy yace jb bakasan zama, yau kana nigeria to gobe za'a ji ka koma India

Murmushi yasaki yace Toya za'ai tunda sunqi saki na, sun riqeni

Daddy yace to yayi kyau, duk abinda kake de Toya kasan ce nanda 8 months kana nigeria saboda alokacin zan zama baba

Wai da gaske kake? Allah mutumina kace harta harbu

Daddy yace wato kafara shaqiyancin naka, nide nafadama lokacin nayi ka tattaro kadawo gida

Jb cikin farin ciki yace ai dole, Amma fa abokina gaskya kodan wahalar danasha wajan neman Amal yaci ace sunana zakasa idan namiji ne

Murmushi kawai daddy yayi yakashe wayar

Amal duk tana kallansa, tana farin ciki

Number Shahid yakira, shahida ta daga, Bayan sun gaisa ne yace Mata Ina shi shahid din?

Tace Yaya gashinan yana bacci

Yace to ki fada masa antynki ta samu ciki, kifadawa su umma ma

Cikin ihun murna shahida tace wayyo Allah anty Amal

Ihun murnar datake ne yasa Shahid tashi daga baccin dayake ajikinta

Yace fiancee lafiya kuwa? Sake rungume shi tayi tace fiance anty Amal ta samu ciki, yanzu Yaya yakiraka yace nafadama

Murmushi yasaki yace alhamdullahi, Amma gaskya nayi farin ciki

Tace sosai ma, nakusa zama momy

Hararta yayi yace ko? Tace emana

Yace no ban yarda da wannan maganar ba, Nima nawa nakeso

Kasa tayi da idonta, Dan Bata manta karonta dashiba

Cikin sauri ta tashi, ganin yanayi mata wani irin kallo, tace bari inje in sanar da ummatah, ta tashi tafice da sauri, yabita da kallan qauna

*** *** ***

Next day

Sunyi kyau sosai cikin manyan kaya, yaruqo Hannunta yar wajan umma, shahida Sai janye Hannunta take, Amma Shahid yaqi sakinta, saida sukaje har wajan umma

Umma na kallansu aranta tace wannan rashin kunya ta yara yan zamani dayawa take

Ta kawar da kanta kamar Bata gansu ba, har qasa suka tsugunna suka gaisa, Shahid yace umma zamu wuce, tace a a basai gobe ne tafiyar ba? Yace a a umma gara muje yau din Dan mu qara tayasu murna

Umma ta dora Hannunta ahabarta, tace Shahid kamar akanku aka fara haihuwa? To duk Dan da aka cika so baqin jini yake

Gaba dayansu sukasa daria

Shahida tace umma karfa yazo ki ganshi gaba daya ki rikice, kice saishi

Umma tace a a ku riqe abinku banayi

Shahid yace ai umma ba wannan maganar ce kadai zata kaimu ba, har maganar aikin nan da Abba yayimin

Tace Toshiknn, gaskya Kam gara kuje din, Allah ya kiyaye, idan babanku yadawo saina fada masa, inyaso kaima saika kirashi awaya

Yace to umma

Ta kalli shahida tace yata ki kula da kanki sosai kinji? Shahid yayi saurin cewa umma nikuma banda ni?

Umma tace Dan Allah ku tafi Shahid

Haka suka futo harabar gidan, da kansa yabude mata gaban motar tashiga sannan yazagaya yajasu suka dau hanya

*** *** ***

Yaya daddy Dan Allah kafita daga Dakin nan, su Momy fa suna falo, karsuyi tunanin wani Abu muke

Qugunta yakama yana daga Bayanta, ya rungume ta, ya dora kansa awuyanta yace shikkenan ma kinga nahuta idan suka fahinci wani abun din, basu ne suka San yara ba

Tace to ai ansamu, Dan Allah katashi ka shirya kashiga office, Nima indomie nakesan dafawa, ita nake sha'awa

Yace no karkiyi da kanki, zan fadawa momy Sai Tasa ayi Miki

Tace Yaya daddy banajin dadin na masu aikin, inaso ne inyi da kaina

Yace Toshiknn

Wayarsa ce tayi ringing, yana dubawa yaga Abba ne me Kiran

Yadaga wayar yace yau ka manta da fita office ne?

Babu kunya daddy yace ah... Abba dama yau bazan fita ba

Abba yace ok to shikkenan

Amal ta kalleshi tace meyasa zakace bazaka ba, idan Kuma wani Abu yataso fa? Yace nariga nasanar dasu yau bazan shiga ba, yarinyata tace in zauna inbata kulawa

Cikin mamaki tace wacce yarinyar kenan? Cikinta yashafa, yace gata acikin nan

Murmushi tasaki tace to Bari inje inyi girki na

Kallanta yayi, cikin shagwaba yace please baby, kawai gaisawa zamuyi da babynah, tace Amma Kuma Yaya daddy su umma fa....

Shima kan gadon ya nuna mata yace please ko Yaya ne

Yakamata Hannunta suka yi gadon, daga nan suka Lula duniyar ma'aurata, inda Amal taji dadin abin sosai, shikuwa gogan baisan Ina kansa yakeba, Jin tasake wani irin dadi

Saida komai yalafa,tace my dear yunwa nakeji, kuma kahanani yin girki da wannan gaisuwar

Yace sorry baby na wallahi ke dince, ta daban ce, bari inje in dafa miki da kaina, aide indomie ce ko? Tokinsamu yanzu

Yatashi yayi toilet domin wanka, Amal ta bishi da kallo Itade tasan cewa bai iya komai ba, Amma tayaya zai iya dafa wata indomie, Amma bari tazuba masa ido

Yana futowa daga wanka, yashirya yace tashi Nakai ki toilet din, kiyi wanka, kafin ki futo indomie tana jiranki

Sarai zata iyayin komai da kanta Amma saboda ya dauke tan ta miqa masa

Hannayenta, yadauke ta yakaita toilet din, sannan yafice

Yana zuwa falo Sai momy ita kadai, tana kallan labarai

Taga yayi kitchen da kansa, ta daga murya tace wani Abu kake buqata ne? Keyarsa ya Sosa yace a a momy Amal ce takesan indomie, shine nace bari inyi mata

Momy aranta tace ikon Allah sabon Salo, to Bari muga wannan girkin yanda zai qare

Afili tace Toshiknn, Allah yabada sa'ah

Aikuwa babu kunya yajuya yashige kitchen din

Yana zuwa yadauki tukunya, ya wanke ya dora sannan yadebo ruwa yazuba saura kadan ruwan yakai Rabin tukunyar

Yadauko noodle din guda daya babba yabude yasaka acikin ruwan, magin daya gani aciki yabudesu duka biyun yazuba, yadebo salt yazuba, sai mai

Yana rufewa kuwa tafara tafasa, ya tsaya harta dahu, yadauko flet yajuye aciki, duk ruwa yacika indomie din, gata tayi fari fat

Yadauko yafuto falon, alokacin Amal harta futo falon itama, har Gabanta yakai mata abincin yace sauko kici gashinan

Ta kalleshi ta kalli indomie din, tace to

Momy dake gefe tana kallansu

Amal aka saka hannu zuciya daya, takai indomie Bakinta, cikin sauri ta furzar, tace Yaya daddy gishiri

Wacce irin indomie ce wannan?

Ta dauke flet din tayi kitchen dashi, Shima tashi yayi yana Sosa kansa zai bita kitchen din, yakai kallansa ga momy yaga dariyar ta take ita dakai

Yana shiga kitchen din yaga ta ajiye indomie din ta dora wata, ya kalleta yanuna mata wadda ya dafa din, yace wannan din bayarwa zakiyi?

Kallan mamaki tayi masa tace, ai babu Wanda zai iyacin wannan indomie din, duk wanda yaci kuwa to mutuwa zaiyi, gishirin dayake cikinta, shine zai kasheshi

Kansa ya kawar, yayi shiru

Yana gani tadafa wata, sannan taja kujera a kitchen din tafara ci, Shima dayaga haka, saiya dauki Tasa yasa spoon aciki yadiba yakai bakinsa, ai tuni ya furzar yana yamutsa fuska, ruwa yanema yasha

Sannan yaje wajanta yasa hannu sukaci tare

Sunkusa gamawa sukajiyo karadin shahida, aikuwa dukansu sukayo falon

Shahida na ganin Amal taje da gudu ta rungume ta, daddy yace ke kalau kike kuwa? Kiyi mata ahankali mana

Saida yafada ne sannan yajuya yaga momy da Shahid suna kallansa

Saiyayi fuska kamar ba shine yayi maganar ba yanemi waje ya zauna

Momy ce dakanta taje Tasa aka shirya musu lafiyaiyan abinci, sunaci shahida tanata tsokanar Amal

Bayan sun gama ne momy takira Abba awaya, yana zuwa suka sake gaisawa sannan yabawa Shahid opper sa, sosai yasake murna da godia

Abba yace ai babu wata matsala ko? kunada kudi cikin account? Shahid yace eh Abba akwai 7 millions

Murmushi su na manya yayi yace ai bakwa kashe kudin ma Shahid, kuyi abinda ranku yakeso fa, zuwa gobe ma insha Allah zansa aturo muku wani kudin

Dagashi har shahida ne wannan Karon sukai masa godia, sannan Shahid yace ai mungama magana da baba ma, yace nadauketa mudawo nan din saboda aiki, saimu dinga tafiya can muyi weekend

Abba yasake murmushi yace Toshiknn Allah yabada sa'ah

Dukansu sukace amin

Saida suka wuni agarin sannan sukai haramar tafiya jigawa, inda zasuyi shirye shiryensu sudawo

*** *** ***

After 2 week's

Suna zaune afalo dukansu, daddy Sai zungurin Amal yake, yana kyafta mata ido, yana nufin ta tashi su tafi daki

Ita kuma taqi tashi, yana sake zungurin ta saita juya masa idonta, tana nuna masa su Abba

Alama yayi Mata da kansa ta tashi su tafi, haka ta sunkuyar da kanta, tadena kallan sa

Basusan Abba da momy duk suna ganin su ba

Wayar daddy ce tayi qara, yana amsawa daga daya bangaren akace yallabai yau ne zakuyi wannan meeting

Kansa yashafa yace meeting? Kaga a daga shi zuwa next week

Yakashe wayar

Abba yace ba meeting zakayi da wasu ba?

Kansa ya Sosa yace yace Abba dama Yan majalissar jiha ne zamuyi meeting dasu

Abba yace to ai babu dadi karya alqawari, yakamata katashi katafi

Babu yanda ya iya haka yatashi jiki ba qwari yashirya yafita

Amal na rakashi itama tayi Dakinta

Momy tayi Ajiyar zuciya tace alhaji Yaron nan bayasan fita office yanzu, narasa dalili

Abba yace to tsakaninsa ne da iyalinsa

Momy tace to ai idan yafita itama yarinyar kanta zata Dan huta

Murmushi Abba yayi yace Toya za'ai, aide batada damuwar komai ko? Momy tace babu komai alhaji

Washe gari da daddare suna gama cin abinci suka yiwa su Momy saida safe zasu tafi Abba yace kudawo dama inasan magana daku

Dawowa sukai suka zauna Abba yace nasa ashirya min ma aikata tareda doctor's guda biyu mata, Amal zata tafi Malaysia domin renon cikinta

Saboda nan din inaga hayaniyar mutane zata dameta

So angama komai zaku iya tafiya gobe ko jibi idan ka sanar a office, idan ka rakasu saika dawo bakin aikinka

Comments

Comments

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

27

Gaban daddy ne yayanke yafadi, wacce irin tafiya kuma yana Zaman zamansa da matarsa?

Amal ma jikinta yayi sanyi dajin furucin Abba, to Amma Yaya zatayi dole zata hakura da mijinta tabi umarninsa tunda kamar mahaifi yake awajanta, dole akwai abinda ya hango shiyasa yafadi hakan

Dan haka ta yunqura zata tashi taji caraf daddy yariqe Hannunta

Hannun nasa tabi da kallo sannan ta zauna

Daddy yace Abba mungode da hukuncin daka yanke akanmu, Amma Abba banqi takaba, saide Ina neman alfarma daya awajanka, wallahi Abba zan Bata ko wacce irin kulawa, insha Allah Babu abinda zai faru, Abba nayima alqawari, nide kar'arabamu

Abba ya kalli momy tareda ajiyar zuciya, Lalle zamani yazo qarshe, rashin Kunya qiri qiri

Sannan yace to ai babana Nima ba komai ne yasa nace hakanba, Naga ita yarinyar zata samu hutu babu hayaniyar jama'ah, sannan Kai kanka zakafi tsaida hankalinka waje daya game da aikinka

Momy tace hakane Kam, kaga daddy bakasan fita office tun daga yanzu ma da Amal ta samu ciki

To kuma idan ta haihu inajin tattaro komai naka zakayi ka zauna agida, karfa ka manta haqqin mutane ne akanka kakula dasu, nasan cewa Amal itama haqqinta na kanka but su jama'ar Gari alqawari kadauka zaka kula dasu kabawa kowa haqqinsa

Shekaran jiya ba kaje office ba, kuma babu wani dalili me karfi, sannan jiya meeting kansa zakuyi Amma Babu kunya kace a daga daddy

Haba babana, Allah fa dole zaiyima tambaya Akan hakan

Shiru su daddy sukayi, maganar momy gaskya ne, Amma tayaya suke tunanin zai iya rayuwa batare da Amal ba? Matarda bikin qawarta za'ai makusanciya Amma yahanata Koda kwana daya ne, sai a ranar sukaje suka dawo, tayaya zasuyi wannan tunanin?

Abba ne ya katse musu tunanin da fadin to kunji wasu daga cikin dalilan dazaisa tatafi

Daddy yace hakane Abba, insha Allah zan kiyaye, wallahi kullum zan dinga fita inde Akan office ne, ni wallahi kafin ku tashi daga bacci na nafita

Gaba dayansu babu Wanda bai murmusa ba Akan maganar daddy

Abba yace to ai shikkenan, ku tashi ku tafi, Allah yayi muku albarka

Suka amsa da amin

Amal tayi hanyar Dakinta, Shima daddy yabi Bayanta, tunawa yayi da iyayensa suna wajan a zaune, Dan haka cikin Sosa qeya yadawo Shima yanufi hanyar dakinsa

*** *** ***

Washe gari da safe suna breakfast gwanin sha'awa su hudu, momy ce dakanta ta zubawa kowa, saboda batasan Amal tayi aikin komai, kowa yanacin abinci ahankali cikin nutsuwa Amma Amal hannu baka hannu qwarya takeci

Tas ta cinye nata, tadau flet tasake zuba wani

Daddy yazuba mata ido yana mata kallan mamaki, wanna wanne irin cin abinci ne?

Abba ma da kansa saida yayi mamaki

Amma Kuma babu Wanda ya tanka acikinsu

Wanda ta zuba dinma tasake cinyewa, momy tace a a yata yaude kice bakyajin qarnin

Cikin murmushi tace eh momy banajin.... Bata qarasa maganar datake ba taji wani irin Amai yataso mata

Aguje tayi hanyar Dakinta, tana rufe Bakinta

Daddy ya kalli iyayen nasa, yatashi Shima cikin sauri yabi Bayanta

A toilet yasa meta tanata Amai, yakamata ya riqe saida tagama, yatayata tagyara jikinta

Sai numfashi take saukewa kamar wanda tayi gudu

Agefen gadon ya sauketa yanayi mata sannu

Kawai kanta ta daga masa, ta kwanta ahankali gamida rufe idonta

Momy ce ta turo kofar tashigo tareda Abba, sannu suka sake yimata

Abba yace babu abinda yake miki ciwo de ko? Tace babu komai Abba

Momy tace to ai kinyi Amai Amal, nasan babu komai acikin ki, me kikeso adafa miki?

Tace momy babu komai, idan naci ma Amai zan sake yi, yanzu ma ji nake

To Amal zama haka ai bazai iyuba, ko tea ne bari inje inhado miki

Cikin sauri tace momy ni banason tea

Momy tace Tome kikeso?

Kai tsaye tace goruba

Momy ta kalli daddy dayake tsaye, tace to Kai kaji

Daddy yashafa lallausar sumar kansa, shi yanzu Ina zaije yasamo wata goruba? Toshi rabon dayaga goruba ma ai tun yana yaro qarami

Abba ne yasake dubanshi yace kaje Kasa asamo mata, sannan ya kalli momy tace hajiya ni zan fita, idan akwai matsala ayi saurin sanar Dani ta waya, zan turo doctor tasake duba Jikin nata

Momy tace to alhaji Allah ya kiyaye hanya

Abba tare suka fita, shida daddy, Abba nafita daddy yakira daya daga cikin ma'aikatan gidan yace yana son anemo masa goruba

Mutumin yace to yallabai za'a same ta insha Allah

Hannu yasa cikin aljihunsa, mutumin yayi saurin cewa haba yallabai

Ai karka damu, wallahi Bana buqatar kudin komai awajanka, wannan ai Abu ne na marmari

Bari inje asamo, daddy yace no please karbi kaje

Babu yanda mutumin ya iya haka ya karbi wannan uban kudi awajan daddy

Har zai tafi daga falon daddy yace masa please dayawa nakeso, mutumin cikin girmamawa yace angama yallabai

Ajiyar zuciya yasauke yakoma Dakin nata

Bai dade da zuwa ba doctor hauwa taqaraso

Duba Amal din tayi sosai, sannan Tajuyo ta kallesu tace hajiya wannan aman dama dole ne saitayi shi, Amma kada ku damu zuwa Dan wani lokacin zata dena

Ta dubi Amal tace ranki yadade ai kina iya cin abinci ko? Tace inaci sosai doctor, ni abincin danake Cima yayi yawa, kamar me cutar yunwa

Daria doctor tayi tace to hakuri zakiyi, baby ne Shima yakejin Tasa yunwar Bayan taki

Yanzu bari nabaki wannan maganin insha Allah zai temaka miki wajan rage aman dakike

Godia sosai sukayi mata sannan tafice

Futowa momy zatayi daga Dakin, Amal ma tabita, momy tace bazaki huta bane Amal? Ki kwanta ki huta

Tace momy babu abinda nakeji, muje falon

Daddy ma abaya yabisu, suna Zuwa falon momy tabata magungunan tasha

Ba'a dauki Dogon lokaci ba, akayi sallama falon da buhun goruba

Ba Amal kadai ba hatta momy saida tayi mamaki, tace Ina zamukai buhun goruba ni juwairah?

Daddy ne ya sallami ma'aikacin, yace momy ni nace akawo dayawa Sai Tai taci

Momy tace kuma daddy har buhu?

Yayi shiru yakasa magana

Amal kuwa tashi tayi, taje tabude ta dauki guda daya, tadawo ta zauna takaita Bakinta

Wani Tsalle daddy yayi yariqe hannun ta, yace yi hakuri, kawo naje na wanke miki

Hanashi tayi ta zuba masa ido, ya marairaice yace please

Sannan tasaki, yaje yaqaro wasu, yashiga kitchen da kansa ya wanke su, yakawo mata

Momy tana kallansu yanda suke birgeta

Amal kuwa yana Bata tafara ci kamar ba gobe

Daddy yazuba mata ido yana mata kallan tausayi, to duk wanda yake iya cin wannan abun ai abin tausayi ne

Ita kuwa Amal ko ajikinta, data gama da qwallo daya zata ajiye tasake daukar wani

Saida tagama, sannan tayi ajiyar zuciya, ta maida Kallanta ga tv

Shima daddy waje yanema ya zauna, tana wannan kallan bacci me nauyi yadauke ta, momy ta dubi daddy tace dauketa kakaita daki

Babu musu yadauke ta ya kwantar da ita sannan ya sumbaci goshinta yafuto

*** *** ***

Next day

To shahid har kun futo? Eh baba mun gama zamu tafi, baba yace to kaji de abinda nafadama, kariqe yarinyar nan Amana Shahid

Karka manta yar'uwarka tana gidansu, duk abinda kayi mata to haka za'a yiwa qanwarka, Dan haka Dan Allah ku riqe junanku Amana

Shahid yace baba insha Allah Babu matsala, zan riqe ta Kamar yanda zan riqe Amal, ba zanyi sakaci da ita ba

Umma dake gefe tace to Allah yayi muku albarka, idan kunje ku gaida su hajiyan da Amal

Shahid yace to umma zasu ji, shahida ce tafuto itama cikin shirinta, Bayan sun gaisa dasu umma ne, sukai musu sallama, Shahid yace to umma Sai weekend insha Allah

Umma tace nikam kuyi zamanku ma Shahid

Shahida ce tace a a umma gaskya zamu dawo banasan narabu dake

Murmushi umma tayi tace to yata Allah yakaiku lafiya

Dahaka suka fice daga gidan sukadau hanya

*** *** ***

After 2 week's

Daddy ya maida hankalin sa sosai wajan aikinsa, Koda yaushe baya zama agida saide idan yadawo ne zai kebe da iyalinsa

Haka kuma duk tsawon wannan lokacin bai qara zuwa wajan Amal da wata buqatar sa ba, idan yaje ma kullum cikin bacci take, Koda ace yana burin su kasance tare Awannan Daren haka zai ganta tana aikin bacci saide ya hakura

Kullum dataci abinci Sai bacci kamar me cutar bacci

Haka ya daure yake hakuri

A yayinda su shahida suke zamansu lafiya, gwanin sha'awa da birgewa

*** *** ***

Karfe hudu na yamma yau agida tayi mishi,direct Dakin Amal ya wuce, yau yayi sa'ah tana gaban madubi tana kwalliya, yana zuwa yafada kan gadonta yace baby I miss you sosai wallahi

Juyowa tayi tace kaida ka share ni kullum kana office kamar bakada mata

Murmushi yasaki yace banasan rigima, Bayan kullum nadawo kina bacci

Nikuma banasan tashin ki a bacci shiyasa

Fari tayi da idonta tace to naji, tashi muje kayi wanka Kaci abinci saika huta

Cikin shagwaba yace baby nide anan zan shirya yau

Amal tace my dear karmuyi haka dakai Dan Allah tashi muje

Hannayensa ya miqo mata alamar ta dagashi, taje takama jansa takasa karshe de shine ya fuzgota tafada jikinsa

Kissing din wuyanta yayi sannan yace to muje

Hannunsu sarqe da juna suka futo sukai dakinsa

Dakanta tacire masa kayan sannan takaishi har toilet din tafuto

wardrob ta nufa ta dauko masa kayan shan iska, sannan ta kalli Dakin, yana Dan buqatar gyara, haka tafara tattare kayan Dakin

Ta gyara shi tsaf, yanata qamshi

Yana futowa ta karbi qaramin towel din dake hannun sa yana goge ruwan fuskar sa

Qarasa goge masa ruwan tayi, tajashi har gefen gadon suka zauna, ta dauko mai tafara shafa masa

Shikuwa Sai binta yake da kallan birgewa da tsananin so

Yana zaune tana shafa masa man, taushin Hannunta dayake yawo ajikinsa ne yahaifar masa dajin wani irin yanayi atare dashi

Man ya karba ya ajiye yana binta da wani irin Mayan kallo, nan da nan ta gane manufarsa

Batayi masa musu ba lokacin daya janyota jikinsa da niyyar yin abinda yake so, tunda ita kanta tasan cewa yayi Mata hakuri

Basu dau tsawon lokaci ba suka Lula duniyar ma'aurata

Sosai suka murji junansu, sannan sukai wanka suka sake shiryawa, daddy Sai nishadi yake,

Amal na fesa masa turare yaga tana yatsina fuska, da mamaki ya kalleta yace baby lafiya kike kuwa?

Saurin boye damuwar ta tayi tace my dear babu komai

Yace no idan kinajin wani muje asbiti

Tace karka damu babu komai, Hannunta yana cikin nasa suka futo daga Dakin

Suna Zuwa falo ta riqe cikinta, tace wayyo Allah na Yaya daddy ciki na

Lokaci daya Daddy ya hargitse, yarasa Yaya zaiyi, kamata yayi yace Amal!!

Takasa amsawa Sai murqususu take ta riqe cikinta

Cikin tsananin tashin hankali yace Amal!!!

Hakanne ya janyo hankalin Abba da momy dasuke daki, Aguje sukayo falon

Suna Zuwa momy tace subhanallah meyasa meta daddy?

Idanunsa jajir yace momy Wai cikinta ne yake ciwo

Jikin momy yayi mugun sanyi ta dubi Amal da Bata Motsin kirki, ta janyo ta jikinta ta dubi Abba tace alhaji mu tafi asbiti

Abba daya zama gunki yana tsoron Kar itama ta mutu cikin mutuwar jiki yayi waje

Momy ta cewa daddy dauketa muje, yana dagata sukaga jini awajan

Momy tace innalillahi wa inna ilaihir raju'un

Daddy kuwa yana ganin haka Sai kuka

Suna futowa harabar gidan sukayi kicibis da Abba doctor hauwa, wadda inde jinya ce ta mata agidan to ita ake turo musu saboda qwarewarta wajan aiki

Momy Gabanta yana faduwa tace alhaji yarinyar nan fa jini take zubarwa

Cikin tashin hankali Abba yadubi momy yace kinga abinda nake fada miki ko?

Daddy kuwa baya um bare um um, hawaye yake sharewa kawai

Cikin sauri doctor ta karbeta sukayi asbitin cikin gidan

Babu Bata lokaci likitoci suka shiga Bata temakon gaggawa

(comments dinku yanayin kadan fan's)

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

28

Momy Sai zirga zirga take agaban Dakin da aka shiga da Amal, cikin zuciyar ta tana tsoron Kar yar mutane ta mutu ahannun su, mezasu fadawa iyayen ta?

Abba ne me yar nutsuwa acikinsu, daddy kuwa yana zaune Idanu sunyi masa jajir

Shi tunda yaji maganar momy tana cewa Amal na zubar da jini yasan cewa kawai shikkenan bari zatayi, shikuma haka Allah yayi shi bazaiga jininsa aduniyaba

Suna wannan Zaman jiran har tsawon wani lokaci

Doctor tafuto, Gaba dayansu kamar hadin baki suka nufeta suna tambayar doctor ya ake ciki?

Ta dubi daddy da gaba daya kamanninsa suka sauya

Tace ranka yadade babu damuwa zamu iya qarasawa office

Babu musu suka bita, Bayan tagama rubuce rubuce tadago tace alhaji gaskiya Badan anyi kokarin kawo ta asbiti da wuri ba da tuni cikin dake jikinta ya zube, muma kanmu munyi mamakin rashin zubewarsa kasancewar ta zubda jini mai yawa, Amma Allah cikin ikonsa ya temaka,kuma muma munyi bakin kokarin mu wajan ganin cikin be fita ba

Daddy Kasa boye ajiyar zuciyar sa yayi, Dan har saida yadora hannun sa Akan Kirjinsa yasaki wata nannauyar ajiyar zuciya yana qara godewa Allah

Momy tace to alhamdulillah, Abba ma yace to Allah mungode Maka

Doctor tace saide alhaji wani hanzari ba gudu ba, gaskya yakamata abarta tahuta, ina nufin ta bangaren zamantakewar aure, aikata wannan abun shine dalilin faruwar wannan matsalar

Abari tukunna har cikin yayi qwari, Amma Awannan lokacin gaskya idan aka matsa cikin zai iya fita

Daddy cikin sauri yace babu komai doctor insha Allah za'a kiyaye, Abba yasaki murmushi ganin daddy yagano dalilin dayasa tun farko suka so tura Amal wani qasar daban

Miqewa yayi yace doctor zan iya ganinta? Tana murmushi tace ranka yadade tana buqatar hutu yanzu saide nanda awa uku haka

Yace ok babu damuwa

Gaba dayansu suka futo, basu koma gida ba saida lokacin da doctor ta diba yacika

Sannan suka shiga Dakin

Suna shiga daddy yayi saurin qarasawa gadon, idonta biyu, da murmushi ta tareshi, hakanne yasake kwantar masa da hankalin sa

Yace baby yajikin naki? Tace lafiya Yaya daddy banajin komai yanzu, saide yunwa, ta qarasa maganar tana daria

Shima dariyar yasaki yace karki damu, da kaina zan dafa miki abinda kikeso kinji?

Daria tasaki tace tab gishirin zanci

Abba ne yayi gyaran murya ganin kamar basusan da mutane adakin ba, hakanne kuwa ya fargar dasu

Cikin kunya daddy ya matsa daga gadon kadan yakoma kujerar dake gefe ya zauna ya zuba mata Idanu

Momy tace sannu Amal, cikin murmushi tace yauwa momy

Abba yace bakyajin komai de yanzu ko? Tace Abba kalau nake jina babu damuwa, kawai mutafi ciki, banasan Zaman nan wajan

Abba yace to alhmdlh, Allah yaqara kiyayewa Amma de kibari ki sake hutawa tukunna

Doctor hauwa ce tashigo ta dubi Amal tace ranki yadade babu damuwa de ko? Tace babu damuwa doctor banajin komai yanzu

Cikin murmushi ta dubi daddy tace to ai zaku iya tafiya ma

Abba yace eh haka tacemin ma Wai mutafi batajin dadin nan din

Shine nace tabari tasake hutawa tukunna

Doctor tace ai alhaji Babu damuwa zata Iya tafiya dakanta ma, munyi mata allurai

Abba yace to alhmdlh

Allah yaqara kiyayewa de, dukansu suka amsa da amin

Amal tafara kokarin saukowa, daddy yayi saurin matsawa kusa da ita yace idan bazaki iyaba na daukeki

Ba doctor kadai ba, hatta iyayen saida suka murmusa, sosai suka birge doctor, yanda suke kula da junansu

Amal tace Yaya daddy Allah zan iya

Yace to taka mugani, daria Tasa sannan takama hannun sa suka futo daga Dakin

Momy ta rungume ta ajikinta, suka yi Cikin gida

Suna qarasawa ciki momy ta dubi daddy tace kuje daki, bari naje nakawo mata Dan abinda zata ci

Daddy yace to momy

Suna shiga Dakin kuwa ya kwantar da ita a gado, Amal tace ni narasa wannan lallabawa dakakemin Yaya daddy nace ma lafiya kalau nake jina

Zama yayi akusa da ita yakama Hannunta ya riqe, yace baby kiyi hakuri, Naja miki rashin lafiyar da takusa Tasa mu rasa babyn mu

Cikin alamun tambaya tace kamarya? Me kake nufi?

Saida yayi kissing Bayan Hannunta sannan yace doctor tace abinda mukayi dazu ne yasa kika fara zubar da jini, tacema Wai da bamu kaiki da wuri ba datuni kinyi bari

Shiyasa nake sake baki hakuri, Akan abinda yafaru, nasan kinsha wahala sosai, Amal tasaki Ajiyar zuciya tace

Yaya daddy dama haka ake bari?

Shima cikin tausaya wa yace hakane baby, tun lokacin da momy tace kina zubar da jini gabana yafadi, saboda nasan cewa mun Riga da mun rasa babynmu

Amma Sai gashi Allah cikin ikonsa ya tsayar dashi, Babu abinda da zance da ubangijina Sai godia

Amal tace to Yaya daddy, ni ai banga wani laifinka anan ba, Abu ne wanda ni dakai babu Wanda yasan hakan zata faru aida bazamuyi ba

Daddy yace shiyasa yanzu na daukarwa kaina alqawarin hakura, har Sai lokacin da cikinmu yayi qwari, baby shekaru qaruwa suke, ina zaune banida da ko daya nawa

Allah Bai rageni da komai ba saita wannan fannin, kuma gashi yadauka yabani, yaushe zanyi sakaci dashi?

Tace hakane Kam Allah ya kiyaye gaba, yace amin baby nah

Yanzu saura wata bakwai ki haihu, Inga jini na aduniya Nima, cikin mamaki tace Wai har qirgawa kake?

Shima cikin mamaki yace kinsan yanda na matsu Inga me zaki Haifa mana kuwa baby? Ai qirge yazama dole, sannan Ina roqon Allah yasa suyi kamarki

Amal tace meyasa Yaya daddy? Bayan kowanne uba yanasan yayansa suyi kamar sa

Cikin sauri yace a a banda ni baby, nafisan suyi kamarki, wallahi zanfi sonsu ma Allah yagani

Daria yabata sosai, tana cikin daria kuwa momy tashigo da farfesun kaza ahannun ta, ta kalli daddy tace wato kana nan kana damun ta

Yace momy kawai labari nake Bata, momy tace to naji, yata tashi Kisha farfesun nan, Amal tace to momy

Flet din daddy yadauko yasa a Gabanta yasaka spoon yafara Bata da kansa

Murmushi momy tasaki tafice daga Dakin, wannan rashin kunya ta daddy Sai shi

*** *** ***

Next day

Anty Amal yajikin naki? Ajiyar zuciya tayi tace lafiya anty shahida, ai naji sauqi

Mayafinta tacire tace wallahi da momy tafadamin jiya bakiji yanda naji ba ga fiance baya nan, bare mu taho

Nide na keta tunani

Amal tasaki murmushi tace inye au fiance

Shahida tayi murmushi tace nide yanzu Dan Allah Babu abinda kikeji? Wallahi Bama San abinda zai taba lafiyar babyn nan

Amal tace to kema saiki dage ki samo mana wani

Ajiyar zuciya tasauke tace anty Amal kenan nifa auren nan yafara isata, ace kullum cikin Abu daya, Allah nagaji

Me Amal zatai inba daria ba

Tace aikuwa haka zakiyi hakuri kibar yayana yayi abinda ransa yakeso, ni Sanadin hakan ne yasa jiya na kwanta jinya

Shahida tace Wai Dan Allah da gaske?

Tace wallahi anty shahida

Jinjina Kai shahida tayi tace to ai ke dince duk kin haukata mana dan'uwa, ba dole ba

Amal tace bawani hauka, kawai de Allah ne yakawo

Shahida tace to Allah yasawaqe, yasaukeki lafiya, tace amin sis

Saida suka wuni agidan itada shahid sannan suka tafi gidansu

*** *** ***

Me ciki kwana biyu

Daga bangaren ta tace maisah yagida ya amarci

Lafiya kalau Amal, yagida yasu baban baby?

Au har ya zama baban baby? Maisah tace to me za'a jira

Kede kawai yanzu kowa ke yake jira ki haifo mana musha bikin suna

Gaskya ne Bama tani kukeba ko maisah?

Maisah tace sorry qawata, kema kinsan kece first ai, kamar yanda kike first lady

Daria tasaki tace to nagode kema ya angon naki, maisah tace yana lafiya wallahi

Ganin shigowar daddy ne yasa Amal tace to Dan Allah ki gaidashi, sai mun sake waya

Maisah tace to zaiji bye

Qarasawa tayi ta karbi jakar hannun sa, tace sannu da zuwa Yaya daddy yace yauwa baby

Bani paper da biro please

Cikin mamaki tace to lafiya? Yace kede yi sauri

Daki tashige ta dauko joter da biro tace masa to gashi

Janyo ta yayi dab dashi ta zauna, sannan yadubeta yace yauwa me kike ganin yadace muyi oder na baby ne?

Ajiyar zuciya tasauke tace yanzu Yaya daddy haihuwar daba yauba ba gobe ba? Sannan Kuma nasan su Momy mafa zasu Sai komai

Kallanta yayi yace kema kikace su Momy, wannan kuma na baban baby ne da kansa

Ya sunkuyar da kansa yana jero kayan yara, ta kalleshi tace to yanaga kana saka bibbiyu?

Yace eh idan namiji ne kinga gashinan ansiya, idan mace ce ma itama gashinan

Idan Kuma dukansu Allah yabamu shikkenan kinga mun huta

Daria tasaki tace Dan samu har yara biyu? Yace to shikkenan kina wasa ko?

Yadaga hannun sa sama yace ya Allah kabani yan biyu

Cikin sauri takamashi tana sauke masa hannun sa qasa, tace a a Yaya daddy wallahi akwai wahala

Rubutun sa yaci gaba dayi, hatta takalmin da zasu saka da keken koyon zama, dana koyon tafiya, Babu abinda yabari

Amal na kallansa tana murmushi

*** *** ***

Babana yakamata kadauki hutu fa a office, ka raka su Amal, kaga inda zasu zauna dakuma yanayin Garin

Amal ce ta kalli Abba cikin sauri, ita tarasa meyasa Abba yakeson nesantata da daddy

Kallanta takai wajan daddy ko zai fadi abinda zai karesu, Amma ga mamakin ta saitaji yace to Abba insha Allah zansa mana lokaci saimu shirya mu wuce

Abba yace to Allah yayi muku albarka

Zaku iya tafiya

Cikin sanyin jiki Amal ta tashi, suka hada ido da daddy tasakar masa harara tayi Dakinta

Shima bai lura da iyayen nasa suna falon ba yabi Bayanta, yana shiga Dakin yaganta Akan gado tana kuka

Cikin sanyin jiki yaqarasa gadon ya janyota jikinsa yafara bubbuga bayanta alamar rarrashi, qwace jikinta tayi tace Nika rabu Dani, baso kake arabamu ba? Ai shikkenan

Sake kamota yayi ya rungume ta sosai ajikinsa, baby bazata gane ba, shi kansa idan yacika magana a halin yanzu to zai iyayin kukan Shima

Cikin rawar murya yace "baby"

Kiyi hakuri, ni kaina bazan so abinda zaisa muyi Nisa da juna ba, kema kinsan Ina kaunarki fiye da komai

Amma baby maganar Abba akwai gaskya aciki, likita tace abarki ki huta zuwa wani lokaci

Baby Ina ganinki Koda yaushe akwai lokacin da bazan iya hakura ba, dole ne mu take dokar doctor, Bayan kuma hakan illa ne ga lafiyar ki data babynmu

Sanin kanmu ne kowa yadauki BURIN duniya ya dorawa wannan cikin, musanman ni danafi kowa buqatar sa

To tayaya zanso in aikata abinda zaisa narasasu? Baby idan Ina ganinki gaskya bazan iya hakura ba, bazan jure ba baby nah

Dagota yayi yakama Fuskarta ya riqe da hannayensa biyu, yace nayi miki alqawarin zan dinga zuwa Ina ganinki akoda yaushe kinji?

Daga masa Kai tayi, tana hawaye, ahankali yasa harshen sa yashare mata hawayen duka, sannan yahade bakinsu waje daya

Saida yayi kissing dinta sosai, sannan yadago da fuskar sa yace kin hakura?

Cikin sanyin jiki ta rungume shi, tana Ajiyar zuciya

(Ummy Abdul Nima comment dinki yatafi Dani kamar yanda BURINAH yatafi dake😄)

Gaskya babu abinda zance da masoyan wannan novel, tsakanina daku Sai godia □□

Godia ta mussaman ga masoyan BURINAH na Facebook, haqiqa inajin dadin yanda kuke zuba Sharhi Akan BURINAH, but Dan Allah karkuce yayi kadan Dan nasan Hali 😄😄😄

Mrs Usman ce ✍BURINAH □

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

29

Haka suka zauna tana rungume ajikinsa har tsawon wani lokaci, yana ta faman bubbuga bayanta alamar lallashi, har bacci ya dauke ta

Ahankali ya kwantar da ita Akan gadon sannan yayi kissing goshinta yafita daga dakin

Direct dakinsa ya wuce Shima, yafada kan gadonsa gamida rufe idonsa

Koda wasa bai taba tunanin soyaiyar wata yarinya zata yi masa mugun kamu kamar hakaba Bayan salma

Sai gashi zai shiga wani Hali saboda rabuwarsa da baby

Ko Yaya zai iya rayuwa Bayan Bata nan?

Bayajin yanda yake tsananin kaunarta zai iya wata biyu batare daya sakata acikin qwayar idon saba

Murmushi yasaki lokacin daya tuna da darun datayi masa na dazu, Wai ya nasan arabasu

Baby kenan Uwar rigima

Dena murmushin yayi lokacin da maganar salma tafado masa arai, yatuna lokacin dasuke wasa da fillo a falon su Momy yace

"salma kibani wannan fillon "

" gwalo tayi masa tace bazan baka ba saikayi murmushi "

" inkinga murmushi na to amarya ta nake yiwa

Ashe kuwa hakanne, gashi yanzu yanayin murmushin ga baby akoda yaushe

*** *** ***

After one week

Rana Bata qarya, inji bahaushe

Suna tsaye acikin airport din gaba dayansu

Amal na Jikin momy Sai kuka take, momy tace Amal kiyi hakuri mana, ai Zaman nadan wani lokaci ne zaki dawo kinji yata?

Cikin kuka tace momy ni banasan rabuwa dake

Jikin momy yayi mutuqar sanyi, ita kanta batasan rabuwa da yarinyar, juyawa tayi ta kalli Abba

Shima cikin ransa quna yake, Dan haka cikin sauri yakawar da kansa Dan karsu gane halin dayake ciki

Yadubi daddy yace to karaam, ai babu wata matsala ko?

Cikin dauriya yace Abba babu damuwa, insha Allah idan munje zanyi kokarin samar mata da komai

Abba yace to kace baka buqatar doctors dinma

Daddy yace Abba ai can ma sunada qwararrun likitoci, jb yahadani da wani doctor zanje wajansa mu tattauna saiya bamu qwararrun likitocin mata zasu yi Mata komai

Abba yayi Ajiyar zuciya yace Toshiknn, Allah yakaiku lafiya

Shahida ta rungume Amal ajikinta, tana sake rarrashin ta, Shahid ya matso yace duk kune kuke sake shagwaba yarinyar nan fiancee

Yadubi Amal Yace qanwata, Allah yakaiku lafiya

Hararar wasa tasakar wa Shahid din, daddy yana kallansu yana murmushi

Komawa yayi wajan jama'ar da sukayi dandazo wajan rakoshi airport

Haka yayita meqa musu hannu, suna sake musabaha sannan yajuyo yakamata hannun Amal yariqe

Sukayi sallama dakowa suka yi ciki

Babu Bata lokaci aka bada umarnin shiga jirgi, Kai tsaye inda manyan mutane suke zama acikin jirgi suka nufa, kamar govnors da sarakuna

Basufi minti goma da shiga jirgin su ya Lula zuwa Malaysia

*** *** ***

Already yariga yayi musu booking din komai na inda zasu zauna zuwa wani lokaci

Dan haka Kai tsaye jirgin su na sauka direct gidan aka kaisu

Sosai gidan yayi masifar haduwa, daga wajansa ya qawatu da shuke shuke masu gwanin sha'awa

Bawani babban gida bane Amma yanda aka tsarashi ne kadai zaisa ya birgeka

Cikin falon komai milk and ash color ne hatta dining table din haka kalar su take

Cikin kitchen Din kuma komai green ne, dakuna ne guda biyu da aka qawata su da furnitures launin pink da baqi

Shine yayi Mata jagora har cikin gidan, ita Kam Sai Kalle Kalle take

Dubanta yayi yana cire babbar rigar jikinsa, ya ajiyeta Akan kujera yace kihuta baby, zanje in dawo

Kallansa tayi tace Amma my dear ni gaskya tsoro nakeji

Daddy yace babu abinda zai sameki baby, nuni yayi Mata da kofar falon yace dubafa akwai megadi, ki shiga kiga gidan idan akwai abinda bai miki ba saiki fadamin idan nadawo, dama ni na ganshi awaya tun kafin muzo

Cikin shagwaba tace to Amma karka dade

Yace angama baby nah, yasakai yafice daga falon

Tashi tayi ahankali tana kallan gidan, saida ta zagaya ko'ina, tanata murmushi ita kadai, gaskyar Abba dayace tana buqatar waje marar hayaniyar mutane, yanzu de duba yanda gidan nan yayi sosai, komai ya birgeta

Saide matsala daya zata zauna tsawon wani lokaci babu BURIN ranta atare da ita

Ajiyar zuciya tasauke, ta janyo jakar kayansu tayi cikin daki da ita

Rigar bacci ta janyo ta ajiye Akan gadon, sannan tadaukowa daddy nasa kayan baccin

Sannan ta daura towel tashiga wanka, tana futowa ta Bude jikinta da turare

Takama gashin kanta tayi kalba qwaya daya dashi, jelar gashin tasauko agadon Bayanta

Hijabi ta nema tayi sallolin da ake binta, sannan ta cire hijabin tafuto falo

Bata dade da zamaba, daddy yadawo

Akan kujera ya zube yana cewa wash baby

Cikin daria ta dube shi tace kagaji ko Yaya daddy? Sannu, tashi muje kayi wanka da sallah saika kwanta kahuta

Kallanta yayi cikin sauqin so yace ai nayi sallah awaje, naje nasiyo abinda zamu ci ne, sai kuma wajan doctor danaje Akan maganar ki, insha Allah gobe zai turo mana da doctors din dazasu dinga lura dake da babynmu

Daya zata dinga zuwa da safe har dare

Dayar kuma zatazo da daddare Sai Washe gari da safe idan yar'uwarta tazo saita tafi gida

Kallan mamaki tayi masa tace Yaya daddy saikace wata yar Sarki?

Hannunta yakama ya riqe sannan yace ai awajena kinfi Sarkin ma baby

Tace to naji, muje kayi wankan yanzu

Yace no Zona fara baki abinci tukun, idan na tabbatar babynmu ya qoshi sainaje nashirya Nima inzo kibani nawa

Kallansa take da tsananin mamaki, wannan wanne irin so yakewa wannan cikin?

Batace masa komai ba Takama hannun sa tana janshi, tace bazan ci komai ba, saina tabbatar kaima ka gama komai, saimuci abincin mu kwanta, Naga kagaji sosai

Binta yake da kallan luv, ashe Shima an damu dashi haka

Babu musu yatashi sukaje ciki yayi wanka, itace ta taimaka masa yashirya, sai shagwaba yake zuba mata

Falon suka dawo, suka fara cin abinci, shida kansa yadinga Bata harta qoshi

Sannan Shima yaci nasa

Dakanta ta tashi taje ta Bude fridge a kitchen, komai da komai akwai, hatta kayan fruit Ba'a bar komai ba

Ruwa da just tadauko musu tareda cup

Bayan sunsha ne,daddy yatashi da kansa yaje ya maida

Daukarta yayi cak suka koma kan doguwar kujera, tana kwance a Kirjinsa

Cikin rada yace baby kinsan me?

Kanta ta girgiza masa batare datayi maganaba

Yace lokacin da mukaje Germany natuna, kowa baya kula dan'uwansa

Sai yanzu ne Naga babban gangancin dana tafka wajan rashin kula dake

Dagowa tayi da kanta tana kallansa ta rufe masa baki da Hannunta

Cikin daria tace Dan Allah kabari

Karkasa natuno halinka nada daria tayimin yawa

Kallanta yake yana zuba mata murmushi yace menene halin nawa nada?

Kwaikwayon maganar sa tayi tace "idan kin gama zamu fita"

Sannan tasake cewa "karki batamin lokaci minti goma nabaki"

Daddy baisan lokacin da yasa daria ba

Yace kai baby banda sharri fa

Hararar wasa ta sakar masa tace bawani sharri

Haka sukai ta tuno abubuwan dasuka faru dasu abaya suna daria

Daga qarshe suka kira yan nigeria kowa da kowa suka gaisa sannan sukayi cikin daki suka kwanta

*** *** ***

Amma gaskya Shahid babu abinda zance dakai saide nace Allah ubangiji yayi muku albarka gaba dayanku

Shahid yace amin baba

Qwallah ce ta cika idon baba hamani afili yace Allah yaji qanka ibrahima, Allah yamaka rahma

Shahid yace baba kayi shiru haka mana, umma dake gefe tace a a Shahid wannan abun farin ciki ai yafi karfin ayi shiru

Wayarta ta dauka ta kira layin dasu Amal suka kirasu dashi, tana shiga wayar na hannun daddy

Shine yafara dagawa saida suka gaisa sannan yabawa Amal wayar

Suna gaisuwa umma tace Amal din baba, yayanki fa yabiya mana umara nida shi da babanku dakuma shahida, ankusa gama komai cikin wani satin zamu tafi

Cikin farin ciki Amal tace wayyo Allah umma tah

Umma Dan Allah idan kunje nide haqorin makka nakeso, da turaren wuta irin na larabawa mai qamshi, da abaya

Umma ce ta dakatar da ita tace to shashasha, kede kullum bazaki girma ba, memakon kice abaki Shahid din ki sake yimasa godia kokuma abaki babanku kiyi masa murna a a Sai kika hau lissafi

Cikin shagwaba tace Kai umma to Naga Yaya Shahid din yayanane

Umma tace keni Sai anjima

Wayar umma ta kashe tabar Amal da waya a kunne

Daddy dayakejin duk abinda suke fada, baisan lokacin da yasa daria ba yace me haqorin makkah, a a kaga hajiya Amal

Fillon dake gefenta ta dauka tafara jifansa dashi

Yana kaucewa, haka sukai tayi dashi suna zagaye cikin falon

*** *** ***

Atamfa ce ajikinta light blue Sai adon pink da baqi ajikin atamfar

Sosai dinkin ya karbi jikinta

Farar fatar ta tafuto Shar aciki

Fuskarta tasha makeup, tasaka pink din Jan baki a yan qananan lips dinta

Daurin datayi akanta ne yabawa gashin kanta damar zubowa agadon Bayanta

Yana tsaye cikin ash din suit, tana daura masa agogo qirar Gucci

Fuskarta babu alamar farin ciki

Takalmin sa ta dauko qirar Italy ta tsugunna Takama kafarsa ta Zura masa takalmin

Temako daya yayi Mata shine daga mata kafarsa

Sumar kansa ta taje masa, sai sheqi take, sannan tashiga fesa masa turare

Tana gamawa ta ajiye turaren tayi hanyar falo idanun ta nazubar da hawayen data Kasa riqewa

Cikin sauri ya fuzgota jikinsa

Babu Bata lokaci ya rungume ta tsam ajikinsa

Hawaye ne suka sakko asaman kyakkyawar fuskar sa, yayi sauri ya goge karta gani yasake kashe mata jiki

Kuka take sosai, harda sheshsheka, cikin sanyin murya yace kiyi hakuri baby

Insha Allah bazan wuce wata daya ba zanzo naganki tareda babynmu kinji?

Kuka take tasake qanqameshi, Shima kansa kuka zuci yake, Yama rasa wacce kalmar zaiyi amfani da ita wajan rarrashin ta

Kamota yayi suka futo falon, yace Dan Allah baby kiyimin alqawarin zaki kulamin da kanki da baby na, kidinga cin abinci sosai, karkibar babynmu da yunwa

Duk abinda kike buqata kifadawa doctor's dinnan zasuyi miki, akwai me aiki dazata fara zuwa anjima

Ban yarda ki dauke ko tsinke ba

Duk abinda baiyi miki ba

Kawai kisanar Dani tawaya

Yana fadar haka wani irin kuka yazo masa kusa, wani qullulun baqin ciki ya tokare masa wuya

Cikin sauri yajuya yabar falon yana goge hawayen idonsa yafita harabar gidan yashiga Mota suka wuce airport

Kan kujera tafada tasaki wani irin kuka mai ciwo, sai yau taji ta tsani mulki a rayuwar ta

Gashi asadinsa anrabata da daddynta

Kuka take sosai, cikin sauri daya daga cikin doctor me kula da ita tafuto daga Dakin dayake kusa dana Amal ta janyo ta jikinta tana aikin rarrashin ta, cikin harshan turanci

*** **** ***

Tunda daddy yatafi tazama wata irin shiru shiru, Bata magana sosai, kullum cikin tunanin sa take, abinda yake hanata shiga damuwa daya ne yanda zai Bata tsawon lokaci yakirata awaya suyi ta waya yana sakata daria

Saikuma video call a computer daya zama qa'ida kowanne dare, harta saba kullum yakira waya saita dage rigar ta ta nuna masa cikin yagani, banda ruwan pictures datakeyi tana tura masa

Gaba daya ta kumbura, cikin jikinta daya cika wata biyar yayi wani irin girma, abin har tsoro yake Bata, saboda ba haka take ganin na sauran mata masu ciki ba

Duk ranar Allah Sai doctor ta matsa mata kafarta saboda yanda suka kumbura

Haka doctor zata Sata agaba suyi ta zagaye gidan, saita gaji ne sannan zasu dawo ciki

Batta da aiki Sai shan fruit, kullum shine take wuni tanaci, batada damuwar komai banda rashin ganin mijinta

Idan ta zauna afalo anan take wuni, saboda cikin nauyin sa yafi karfin ta, wani lokacin tayi sallah a zaune, wataran kuma idan tanajin dama dama tayi yanda tasaba

Taqara wani irin kyau jikinta yayi bulbul ta murje, Taqara zama yar hutu kamar ka latsa jikinta jini yafuto

A bangaren daddy kuwa yafita zumudin San ganinta, so yake kawai Rana daya yayi Mata zuwan bazata, ayyukan gabansa yake burin yaga yayi sosai, yanda dazaran ya ware wajan babynsa babu me nemansa

Mrs Usman ce ✍BURINAH

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

Second to the last page

30

Fiancee banga perfume din danake using dashi ba Ina kika sakamin shi?

Dawowa tayi kusa dashi tace wallahi yana cikin kayana fiance, qamshin nakeso, shiyasa na sakashi cikin kayana Dan su dinga yin qamshin turaren

cikin rashin damuwa yace ok bari nayi amfani da wannan

Yasa hannu yadauki wani yana fesawa

Haka ya budawa jikinsa turare kamar sabon ango

Cikin dauria ta to she hancinta, tana turashi gaba

Da mamaki ya kalleta yace lafiya?

Cikin to she hanci tace bansan wannan qamshin turaren fice daga Dakin nan

Jikinsa ne yayi sanyi yazuba mata kyawawan idonsa yana Kallanta

Cikin sauri ya matso kusa da ita yace lafiya kike kuwa?

Jin qamshin akusa da ita ne yasa cikin azama ta tureshi tayi cikin toilet da gudu tana kwara Amai

Bin jikinsa yayi da kallo yana janyo rigar jikinsa yana shaqar qamshin turaren

Yarasa me taji dahar zaisa ta yin Amai

Ahankali ya zare rigar daga jikinsa yakasan ce dagashi sai dogon wando da farar vest ajikin farar fatar sa

Toilet din yabita, yakamata ya riqeta saida ta gama sannan ya wanke mata Bakinta da fuskar ta, yariqota yanayi mata sannu suka dawo Cikin Dakin

Ajiyar zuciya take ita kadai?

Shahid yace sannu

Bata iya bashi amsaba illa daga masa Kai datayi

Yace meyake damun kine? Tace babu komai fiance

Yace no, tashi muje asbiti

Tace da gaske nake, Babu abinda nakeji, kawai qamshin wannan turaren daka fesa ne banaso

Kin tabbatar babu abinda yake damunki?

Babu komai fiance

Yace ok

Tashi yayi yacire wandon Jikin nasa yasauya wasu kayan, zuwa kalar brown manyan kaya, yabude cikin kayanta yadauko turaren data dauke

Yafesa sannan yaje kusa da ita yace wannan yayi ko?

Ahankali ta tashi ta rungume shi, tana shaqar qamshin turaren

Shide Shahid yana tsaye mamaki yana neman kashe shi

Ahankali yasa hannu ya rungume ta, suna tsaye ahaka har tsawon wani lokaci sannan yajata zuwa gadon yace ki kwanta ki huta to Nima zanje office

Riqeshi tayi tace ni inasan wannan qamshin please karka tafi

Babu yanda ya iya haka ya zauna agefenta, yana shafa Fuskarta

Ahankali bacci me nauyi yadauke ta

Tashi yayi ya kunna mata esi ya rufeta da blanket sannan yafice zuwa wajan aiki

*** *** ***

Yau tunda safe tatashi tashirya, da kanta tashirya Dakinta, taci kwalliyar ta cikin doguwar Riga ta atamfa

Bawani daurin wahala tayi akanta ba, me sauqi tayi

Ta feshe jikinta da turare

Tafuto falo ta ganshi tsaf agyare

Abinci tazuba me mugun yawa, ta cinye shi tsaf

Zuwa yanzu harta saba da mugun cin abinci kamar yan kwallo

Kuma hakan bazai Hana anjima taci wani abincin ba

Tana gamawa ta dauki Wayarta zata kira daddy kawai kuma saita fasa

Takira maisah

Tana shiga maisah ta daga Kiran daga bangaren ta

Tace Allah Sarki yar'uwata yanzu nake cewa bari inkira me cikin nan inji Yaya take da cikin jikinta

Amal tace kede bari maisah wallahi nagaji da wannan Zaman

Jira nake wani yazo daga gida wallahi kafata kafarsa zan biyoshi mutaho gida

Nagaji

Maisah tace haba me ciki kwana nawa nema yarage

Cikin sauri Amal tace kede bazaki dena fadamin wannan sunan ba, kedinma kwana nawane kin samu naki

Ajiyar zuciya maisah tayi tace albishirinki, ai yanzu ma inada abina harna wata daya

Gani ya sham dina yana tattalina dana babynsa

Amal tace Karde ki fadamin magana wallahi, kinsan cewa Badan matsalar dana samu kwanaki Akan cikina ba, Babu abinda zai rabani da daddy nah

Kuma yanzu ma jira nake yazo, wallahi Dani zai koma

Maisah tace kinga ni wasa nake miki, garama de ki biyo abinki kudawo gida adora daga inda aka tsaya

Daria Amal Tasa tace kinga ni Sai anjima tun kafin ki fara shaqiyancin naki, Allah yarabamu da wannan abin lafiya, maisah tace to amin

*** *** ***

Tun dazu yake tsaye a kofar kitchen din yana Kallanta tana aikinta cikin nutsuwa

Juyowar dazatai Sai ganin mutum tayi

Dasauri ta dora Hannunta Akan Kirjinta, tace oh wallahi harka tsorata ni

Shigowa cikin kitchen din yayi yana rungumota jikinsa yace sorry fiancee

Jug ta meqo masa cike kunun madara da kwakwa tace ungo kaimin wannan dining

Babu musu ya karba yakai, yadawo kitchen din yace Dame zan tayaki?

Albasa ta bashi da wuqa tace ungo yankamin wannan qanana

Karba yayi yafara yankawa, yanayi Idanu yana cikowa da hawaye

Qanshin albasar dataji ne yasa nan take wani irin Amai yataso mata, cikin sauri tayi waje da gudu

Kallan mamaki yabita dashi, sannan ya ajiye wuqar hannun sa ya wanke hannun yabi bayanta

Lokacin daya shiga Dakin harta gama tafuto daga toilet tana goge Fuskarta da towel

Baice mata komai ba, yadauko mata after dress ta dora Akan kayan jikinta yabata dankwalin abayar tayi rolling, suka kama hanyar fita waje

Suna Zuwa harabar gidan, yayi saurin Bude mata gaban motar tashiga, yazagayo yashiga yajasu Sai hospital

*** *** ***

To babana harka shirya ne haka da wuri?karfe takwas fa yanzu

Kansa ya Sosa, yayi masifar kyau cikin farin yadin da aka yiwa ado da ash din zare

Babbar rigar ta karbi jikinsa

Hular kansa kala daya da takalmin kafarsa, sai tashin qamshi yake kamar wanda zaije wajan daurin aurensa

Yace momy ai gara inbi flight din dazai tashi da wuri

Tace to ai ka tsaya kayi break ko

Agogon dake daure a tsintsiyar hannun sa ya kalla

Yace ai momy babu damuwa idan naje can sainaci

Kallan mamaki momy tayi masa tace, kace baka sanar da ita zakaje ba, tayaya zakayi maganar zakaci abinci idan kaje

Kaga muje Kaci abinci saika wuce

Babu yanda ya iya haka ya wuce dining yaci abincin kadan, momy tatashi ta dauko masa wata Leda tace gashi to saika Kai mata

Ai bazaku wuce sati biyu ba zaku dawo gaba dayanku ko?

Fuskar sa yashafa yace eto gamu nande momy, da inaso mu wuce Saudia ne daga can

Momy tace banasan shirme daddy, yarinyar da tsohon ciki zaka Diba kuyita tafiya yawo? Kabari idan Allah yadauke ta lafiya saikuje

Yace to momy saikun ganmu, kifadawa Abba idan yafuto nawuce

Cikin ranta tace yauga zumudi lale

Afili tace to zaiji, Allah yakaiku lafiya

*** *** ***

Doctor ya dubesu yace inajin ku meke tafe daku?

Shahid yace wallahi narasa gane kanta ne doctor, yau tace batasan qamshin wannan Abu, gobe tace batasan qamshin wannan

Hartakai yau Albasa wannan da ake abinci da ita dagajin qamshin ta tafara Amai

Nace mata muje asbiti tace a a lafiya kalau take, shine nace yau de bari nakawo ta aduba ta agani ko batada lafiya ne?

Murmushi doctor din yayi yace Toshiknn bari Akira nurse tazo suje ayi mata text

Babu Bata lokaci nurse din tazo, sukaje akayi mata gwajin fitsari dana jini

Basufi minti talatin ba, likita ya baiyana musu cewa tana dauke da ciki tsawon wata biyu

Nan take farin ciki yakamasu gaba dayansu

Shahid yadaga hannu sama yana zubawa Allah godia

Haka suka taho gida cikin tsananin murna

Suna qarasawa gida shahida tayi hanyar kitchen, cikin sauri yace fiancee me zakiyi?

Tace abincin zan qarasa, yace inaaaa ai daga yau wannan aikin yadawo nawa, zauna kede kawai ki huta

Wayarsa yadauka yakira umma yafada mata ko kunya babu, sannan aka turawa momy text

Yakira number daddy taqi shiga alokacin suna cikin jirgi yakashe wayar, saiya kira Amal yafada mata yayarta tana daukeda juna biyu na wata biyu

Amal farin ciki kamar tayi me, qawa ciki, ga kuma anty shahida ma ta samu nata, Allah Sarki rayuwa

*** *** ***

Da yamma Bayan tagama motsa jikinta, suna dawowa gida tayi wanka tasaka doguwar Rigar material medan fadi

Ta tattara gashin kanta ta daure da dankwalin rigar

Sai tashin qamshi take

Ta zauna afalo tana kallo, tanata sakin tsaki ita kadai wato yau Kiran wayar daya saba yima bazai nemeta ba, saide ita idan ta matsu ta kirashi kenan

Aikuwa bazata kirashi ba itama

Ita kadai de tana kallo dataga tunanin nasa bazai qareba saita dau wayar ta kirashi, Amma Kuma saitaji wayar a kashe

Afili tace to lafiya kuma yau yakashe wayar?

Sake gwadawa tayi still wayar a kashe, dole Sai hakuri tayi ta gumi tareda zubawa TV din Gabanta ido, Bawai Dan tana fahimtar komai ba

*** *** ***

Jirgin su na sauka yahau Mota aka kawo shi har kofar gidan, tareda ambassador nigeria dayake qasar dakuma wasu tsiraran mutane, yana futowa suka sake gaisuwa dasu sannan yashiga cikin gidan cikin farin ciki

Da maigadi suka fara gaisawa sannan yanufi falon cikin takunsa na qasaita

Tana Nan a zaune tana aikin tunanin sa taji anturo kofar falon

Qin kallan kofar tayi, tasan bazai wuce doctor ko me aiki ba

Idanunsa ya zuba mata, yana takowa ahankali har zuwa kusa da ita

Qamshin turaren dataji akusa da itane yasa Tajuyo Dasauri

Mamakin ta ne yakasa boyuwa

Cikin wata irin murna taqarasa wajansa ta sauri, tuni ya rungume ta bakinsa yaqi rufuwa kamar gonar auduga

Yaya daddy!!!

Dama Kaine? Wayyo I miss you wallahi, takai wa bakinsa wani irin kiss me tsayawa arai

Fuskarta yakama da hannayensa guda biyu, yace baby nah

Dafatan de Kuna lafiya keda babynmu? Dukan wasa takaiwa Kirjinsa tace shine kaqi dawowa har munyi wata uku Bama tare

Yace Tuba nake baby nah, kema kinsan dole ce Tasa hakan, idan a kaga wannan Watan nafita, wani Watan ma haka, wasu bazasu duba abinda yake kawo ni ba zasu fara yimana mummunan zato

Yanzu ba gashi nazo ba, cikin shagwaba tace Allah yaya daddy bazaka tafi kasake bari naba

Bazan juri rashin ganinka ba

Kallanta yake cike da qauna, ko waye yace Mata Shima zai iya qara sati daya batare da itaba?

Afili yace Mata aike da nigeria saikin haihu yaro yana gudu zamu tafi

Turo baki tayi cike da shagwaba

Sake janyo ta yayi jikinsa yakai hannun sa kan cikinta ya tsugunna dede inda cikin yake yace Yarona, yauga babanka yazo dafatan zaka barshi yagaisa dakai sosai

Cikin daria tajanye jikinta, daga nasa, takama babbar rigar sa tacire masa sannan tajashi ciki tace muje kayi wanka ka shirya

Ledar daya shigo da ita ya nuna mata yace gashi inji momy, kallan Ledar tayi tace to

Saida takaishi har toilet inda daqyar yabarta tafuto sannan ta dauko masa kayan dazaisaka tafuto falon

Ledar ta janyo taduba, magani ne aciki na mata, Murmushi tasaki lokacin data karanta rubutun dake Jikin takardar Ana cewa Asha da nono Koda madara

Afili tace momy kenan, wato yanzu anbamu dama muyi komai kenan,tunda gashi harda gudunmawa, Amma da antashi anraba mutum da mijinsa

Takardar ta yage daga jiki saboda kada daddy yagani, taje kitchen tasaka acikin dozbin sannan tadebo madara dayawa a cup

Ta ajiye, sannan taje Dakinta takawowa daddy abinci, aqasa ta ajiye sannan ta Bude maganin tazuba acikin madarar tafara Sha

Aranta tana cewa gara tasha Dan tasan wannan mutumin yanda yayi hakurin nan na Tsawon lokaci yau bazasu wanye lafiya ba

Tana cikin Shane yafuto Shima cikin qananun kayan shan iska, abincin ya zuba da kansa yana cewa ai gara dakika kawo abincin nan Dan banci abincin kirki ba nataho Ina murna zanzo naganki

Kafin tayi magana yakarbi kofin Hannunta yace muga me kike Shane haka?

Kokarin karba take, Amma yarigata karbewa yadebo yakai bakinsa yasha

Miqo mata yayi yace ungo babu ma dadi, Hararar wasa tayi masa tace to maganin mutuwa ne

Daria yasa yace shikkenan kinga saimu mutu tare

Abincin tadiba tabashi aspoon sannan ya karba yafara ci

Yana gamawa yajata kan kujera suka kwanta, rigar jikinta ya yaye yana shafa cikin yace baby wannan yarinyar tahana na rungume ki yanda ya kamata

Gashi cikin Naga yayi girma sosai, ko yan biyu zaki Haifa?

Amal zuciyar ta daya tace bawani yan biyu, ai kasan inacin abinci dayawa inajin shiyasa yakesa Yaron ciki yazama qato

Shima abinka da besan komai Akan wani masu ciki ba, bai taba ganiba, sai Akan salma, Dan haka yace eh kuma gaskya kina cin abinci sosai, inajin shiyasa Yaron

yake da girma, Amma kinga salma lokacin dazata haihu ma cikin bekai hakaba, inaga Dan Bata kaiki cin abincin bane

Cikin kwanciyar hankali Amal tace emana, Allah yaji qanta, yace amin baby

Gashin kanta yafara shafawa yace inyi miki kitso? Tace kaidin ne ka iya kitso? Yace bazai nakoya Akan matata ba

Yacire ribbon din kanta yana shafa gashin nata sunata firar su cikin farin ciki

Amal tace Yaya daddy namanta ban fada maba, dazu Yaya Shahid yakirani yace wai anty shahida nada ciki har watansa biyu

Cikin fari ciki yace alhmdlh, Amma nayi musu murna, Allah yasaukeki lafiya, tace amin, kuma maisah ma haka

Cikinta yashafa yace a a masha Allah kice Yaron da zamu Haifa zaiga qanne dayawa

Daria Tasa tace emana

Suna manne da juna babu abinda yake rabasu Sai sallah, suna idar wa zasu koma suci gaba da firar su

Suna idar da sallar isha'i, ya zauna tana zaune Akan cinyarsa suna fira suna kallo, wayarsa yadauka yakira su Abba dasu Shahid suka gaggaisa sannan yabawa Amal wayar suna gaisawa yazubawa Kirjinta ido

Yawani qara cika sosai, ahankali yakai kansa wajan yana kissing tareda lasar su

Cikin sauri ta yiwa su Shahid sallama ta kashe wayar

Dubansa tayi tace Yaya daddy waya nakefa, shiru yayi Mata yana ci gaba da abinda yake

Kansa tafara dagowa daga jikinta Amma yaqi Bata damar hakan

Daga qarshe itama tayi shiru tana karbar saqon, Idanunsa dasukai ja yadago yana dubanta dashi yace muje daki?

Kanta ta daga masa, Dan Bata iya bashi amsaba, daukan ta yayi cimak Sai cikin dakinsu, inda yahade bakinsu waje daya yashiga nuna mata yanda yayi missing dinta, sosai tabashi hadin Kai, Awannan dare haka suka kwana cikin farin ciki da annushuwa

Tunda yazo kuma kula da ita da duk wani Abu datake so yadawo hannunsa, sosai yake Bata kulawar data dace, yana Mutuwar tausaya mata yanda yaga tana riqiniya da wannan cikin, kuma Koda wasa Bata hanashi haqqinsa idan ya nema, saide shida kansa ne zai nuna mata bayaso, wani lokacin kuma tayi masa yan dabarunsu na mata

Hatta matsa mata kafafu baya bari doctor suyi Mata da kansa yake zama tana zaune Akan kujera shikuma yana qasa yanayi mata, aikin doctors kawai suyi Mata awo dakuma duba lafiyar ta da sauran su

Yawo kuwa haka zai jata suje wajajan dasuke kusa, hakan baifi motsa jiki ne agareta ba

Watansu daya a Malaysia suna shan soyaiyar su, sannan sukayi shirin dawowa nigeria

Ganin yanda cikinta yakeda mutuqar girma ne yasa sukabi jirgin yamma, suka iso cikin dare

Amma duk da hakanma jama'ar de suna nan danqam, haka suka tafi government house shida tawagarsa, inda babu Bata lokaci kafafen Yada labarai suka fara watsawa duniya cewa maigirma govnor yayi saukar sirri daga Malaysia zuwa nigeria shida mai dakinsa

*** *** ***

After 3 month's

Babu abinda ya sauya daga kulawar da Amal take samu daga wajan daddy

Yanzu abinma yafi nada, kulawa take samu sosai baga Abba ba, baga momy ba, bare kuma shi kansa uwa uba

Cikinta ya tsufa sosai haihuwa yau ko gobe suna nan sun tanadi komai saide fatan Allah yaraba lafiya

Yayinda cikin shahida yacika wata shida, na maisah kuma biyar

(Facebook fan's, kuyi hakuri jiya ban samu damar yimuku posting ba, nasan kun jira kinji shiru, na danyi busy ne, dafatan zakumin uzuri □□□□ Ina yinku sosai kamar yanda shahida takeyin Shahid 😄😄😄)

Mrs Usman ce ✍BURINAH □

(A Romantic love story)

Writing by Amnah El yaqoub

Bismillahir-rahmanirraheem

Dedicated to readers of this book BURINAH

Last page

31

Zaune suke a main falo itada momy, labarai suke kalla, Amal na kallo Tana shan just

Abba ne yashigo da sallama cikin murmushi momy tace alhaji sannu da zuwa

Amal tafara kokarin tashi ta nayi masa sannu da zuwa

Abba cikin tausaya wa yace a a Ina zakije ne Amal?

Tace Abba Lemon nan nakesan qarowa

A a kuma banda abinki menene amfanin ma'aikata, momy tace bari nadauko miki yata, nafada miki kidena kokarin tashi, kede kawai kiyi Zaman ki, kifadi abinda kike buqata

Cikin kunya Amal tace to ai momy zan iya daukowa, ki barshi

Momy tace a a yi Zaman ki

Taje ta dauko mata wani, tace gashinan Kisha kadan banasan yawan shan abin zaqin nan dakike

Cikin murmushi Amal ta karba, suna zaune suna kallo aka hasko daddy a government day secondary school bununu inda yakai musu ziyara

Abba cikin farin ciki yace babana kullum ka tabashi sai yace shide bayasan wannan mulkin Amma duba kiga yanda yadage yake aiki tuquru

Cikin Jin dadi momy tace ai alhaji daddy idan yaso akwai aiki, mutane nasansa narasa meyasa bayasan mulkin

Abba yace shirme ne kawai irin nasa

Amal najinsu tana murmushi, Wayarta ta dauka ta turawa daddy text tana me qara qarfafa masa gwiwa Akan mulkinsa, yakuma gaida yaran da yakai musu ziyara

Adede lokacin daya daga cikin security ya miqo masa wayar sa

Amma Bai amsa ba

Cikin ranta tace tofa Lalle sarakan aiki

Suna nan zaune inda su Momy suka ci gaba da kallan labarai suna tattaunawa

Amal ta tashi ahankali tashige daki danta kwanta tahuta

Tun jiya take danjin Bayanta na ciwo kadan kadan, ga wani irin ruwa datake zubarwa Shima kadan, Amma dayake ciwon Dan kadan ne saitayi shiru Dan karta daga musu hankali, tasan dole da sunji tana Dan rashin lafiya zasu tashi hankalin su, shiyasa ta danne tayi hakuri

Tana kwanciya bacci ya dauke ta

*** *** ***

After one hour

Acan falo kuwa su Abba suna kallo shida momy daddy yayi sallama yashigo duk Agajiye yana zuwa yafada cikin kujera tareda dora kansa Akan kafadar momy

Abba yace ikon Allah yau kuma antuno baya kenan

Momy ce ta shafa kansa tace daddyn momy ai dama haka yake

Yace momy nagaji wallahi, tace ai yanzun nan muka gama ganin ziyarar dakakai makaranta, Allah yatemaka yabada sa'ah

Amin momy

Ahankali yatashi yayi hanyar Dakin Amal iyayen suka bishi da kallo

Yana shiga Dakin yaganta aqasan tayils tana murqususu

Cikin sauri ya qarasa wajanta yadauke ta cak, yana Kiran Amal! Amal!!

Duk ya gigice, yasan cewa yanzu Kam haihuwar ce ta tashi, innalillahi yanzu Badan yashigo dakinba Yaya zatayi

Su Momy suna falo a zaune suka ganshi yafuto da ita, ai gaba dayansu sukayi kanta

Momy tana ganinta tace wannan haihuwar ce tazo

Muje, muje asbiti da sauri

Abba ne yayi azamar Kiran doctor, dayake acikin gidan asbitin yake nan da nan doctors suka qaraso da gado, aka dorata akai, suka turata zuwa cikin Dakin labour

Daddy yakama babbar rigar sa yacire, bemasan waya meqawa ba, shide yasan yabawa mutumin dayake gefensa

Ana shiga Dakin da ita suka rufo kofar Dakin

Daddy Sai zagaye yake awajan, momy ce me kwantar masa da hankali itada Abba

Shiru shiru tun suna qirga awa daya, har saida suka je kusan awa uku Amal shiru babu labari

Doctor ce tafuto, suna ganin futowarta sukayi caaaaa akanta da tambaya, tace alhaji kuyi hakuri har yanzu de tana naquda, dasaura haihuwar, Amma idan taqara wasu awoyin zamu shiga da ita operation room

Tun kafin yagama Jin karshe zance yasaka kansa cikin Dakin

Tana kwance tana kuka, gashin kanta duk yabaje Akan fillon datake Kai, duk gumi yajiqa mata jiki

Hannunta yakama yace baby, sannu baby

Cikin kuka tace Yaya daddy kayafemin mutuwa zanyi

Ai tana ambatar mutuwa daddy yafara hawaye, ba komai ne yasashi kuka ba Sai kasancewar ta Awannan halin dakuma salma daya tuno, itamafa acikin wannan halin tarasu

Kamar tababbe yace a a! A a! Dena wannan maganar Dan Allah, baby bazaki mutu ba, insha Allah lafiya zaki haihu

Cikin kuka tasake damqe hannun sa tace Yaya daddy mutuwa zanyi kayafemin duk abinda nayima

Gaba daya Tasa jikinsa yayi mugun sanyi

Yariqe ta Yana hawaye, Idanunsa jajir, doctors din dake kanta suka zuba musu ido suna kallan me girma govnor da kansa, yana kuka tuquru kamar bashi ba

Abba ne yashigo Dakin da ruwan rubutu acikin yar qaramar jarka yabata daqyar ta'iya Sha tana daga kwance

Cikin ikon Allah ba'afi minti talatin ba naquda Ganga Ganga ta tashi

Abba ne ya janye daddy suka fice, suna fita kuwa momy tana cewa alhaji Yaya Jikin nata?

Yace a a alhmdh saide fatan Allah yaraba lafiya

Cikin Dakin kuwa doctors suna qara temaka mata wajan cewa kiyi hakuri ranki yadade

Wasu na danna mata cikinta, wasu Kuma suna fadin yi nishi, yi nishi

Tana qwaqwqwaran nishi kuwa Sai kuka sukaji, doctor din datake Gabanta ce tatemaka mata wajan janyo kan babyn

Ana ciroshi yacika Dakin da kuka

Doctor din cikin murna tace congratulation ranki yadade kinsa mu baby boy

Amal Kam batasan inda kanta yakeba ma, domin kuwa still wani ciwon takeji

Acan waje kuwa sunajin kukan jariri daddy ya tsugunna yayi wa Allah godia ta hanyar sujjada

Momy tace alhamdullah

Tasauka

Amal kuwa wani irin ciwo tasake ji yataso mata, batasan lokacin data kaiwa doctors din dake kanta wani irin riqo ba, ta rintse idonta, tana hawaye Sai ga kan wani Yaron yafuto

Nanma aka ciroshi

Aka hadashi da dayan aka gyara su, ita kuwa Uwar baccin wahala ne yadauke ta

Kayan sanyi farare qal aka dauko aka sakasu aciki Sai kuka suke

Cikin baccin ta tasaki wata irin qara tana salati

Doctor ce ta matso cikin sauri tana dubata ta kalli sauran doctors din tace akwai Yaron acikinta

Gaba dayansu suka cika da mamaki, aiki be qare musu ba kenan

Amal kuka da ihu tanata salati su kuma suna aikin rarrashi, saida sukadau kusan minti talatin Ana Abu daya sannan ta haifi danta namiji Shima

Gaba dayansu yaran kamarsu daya babu banbanci lafiyaiyu dasu

Dakin haihuwa yacika da kukan yara

Dayan Yaron aka shirya Shima irin sauran yan'uwansa, likitoci sukayi musu alamar yanda za'a Gane nafarko da masu binsa

Yara bul dasu masha Allah Sai motsi suke suna kuka, idonsu Kar Akan wutar lantarki

Wahalallan bacci ne yasake dauke Amal Bayan angyara mata jikinta

Doctors har rige rigen daukar yaran suke, sunga abin mamakin daba'a cika samun suba aqasar hausa triple kuma duk maza

Babu wadda Bata dauki pictures dinsuba awayarta, za'a nunawa jama'ah wannan abin mamaki

Su daddy suna waje Sai gani sukai doctor's sun futo da yara

Fuskarsu dauke da murmushi suka meqa masa

Mamaki ne yakashe su gaba dayansu su ukun

Daddy yayi saurin karbar su yana kallan Abba da hawayen farin ciki yace Abba triple

Abba cikin tsananin daria yace ka godewa Allah babana

Juyawa yayi wajan momy itama da tsananin murna yahanata magana takarbe daya ta riqe, Abba ma ya karbi daya, Gaba dayansu yaran basu bar komai na ubansu ba, gashi ne kawai sukayi na Amal

Amma hatta yatsun kafarsu irin na daddy ne

Daddy yace likita zanyi muku kyauta ta mussaman Bayan nadawo nutsuwa ta

Zan iya ganin maman su? Cikin daria suka bashi damar ganin ta, aikuwa cikin sauri yashiga Dakin

Yana shiga Dakin ya zauna agefen gadon datake kwance

Yakama Hannunta yariqe yana zubawa ubangiji godia daya mallaka masa Amal

Be dade da zama ba tafarka, sake matsawa kusa ita yayi, yace sannu baby, Allah yayi miki albarka

Cikin murmushi tace Yaya daddy Mena Haifa?

Kafin yabata amsa su Abba suka shigo da kin da sauran yaran ahannunsu

Suka jere mata su a Gabanta, Abba yace ga yaranki nan yata

Cikin kunya ta rufe idonta da tafi Hannunta

Daddy yace keda kika tambaya, to ga Sunan Allah yabamu yan'uku baby duk maza

Momy tace ai babu abin godia Kam Sai Allah, haqiqa Amal kinyi kokari Allah yayi muku albarka kuda yaranku duka

Ta dubi Abba tace alhaji kagafa ikon Allah, shekara da shekaru muna fatan samun qarin zuri'ah acikin mu, Allah Bai bamu ba, Amma gashi lokaci daya yabamu yara har uku

Abba yace hakane Kam hajiya, haqiqa Allah yanuna ikon sa anan

Amal de tayi shiru tana kallan yaran gaba dayansu kama suke da daddy, wata irin qaunar yaran tana ratsa jikinta

Jama'ah suka gani suna shigowa cikin Dakin,suna taya daddy murna, cikinsu harda Yan jarida inda suka fara haska wa yara pictures Suda maman su da babansu

Abba yace ya akai kuka sani ne,,? Wasu daga cikin security sukace ai doctor's ne suka fita waje suka sanar dasu

Kafin kace me daki yacika danqam da jama'ar alamina, wasu sunzo kallan yan uku wasu Kuma suna taya me girma gwamna murna, ganin irin tsawon shekarun daya debe Allah Bai bashi haihuwa ba

Sai dare aka sallamesu daga asbitin suka koma gida

Inda nanma de basu rabu da wata jama'ar ba, shahida da Shahid sunfi kowa zaqewa Akan yaran, anty mufy kuma Sai gobe zata qaraso

Daga ita har yaran Dakin momy suka koma, mutane kuwa da wannan yafita wasu zasu shigo

Daddy babu kunya yacewa momy Ana jagwalgwala su, adena bari Ana daukar su

Momy tace to sannu me yara

*** *** ***

After 6 day's

Dakin momy yashigo Allah yasoshi Bata Dakin, daga Amal Sai yara

Kallanta yayi cike da sha'awa yace baby wallahi nayi missing dinki, jama'ah basa bari ma ingana nida yarana

Hannu yasa yadauki daya yace dafatan sunayen dana fada miki sunyi ko? Tace Yaya daddy sunyi Allah yarayasu

Yace amin baby, kuka daya daga cikin yaran yafara yace baby kibashi nono yasha may be yanajin yunwa ne

Cikin shagwaba tace Allah yaya daddy Nagaji, yanzu fa nabasu madara, kuma ni idan sunasha zafi nakeji, da karfi suke Sha

Daria ce takamashi yace basa yi ahankali kamar niko?

Fillo ta dauka ta jefa masa yace to naji sorry

Yanzu de Dan daure kibashi ko Dan kadan ne kinji Badan halin muba

Daukar Yaron tayi tafara bashi, yanasha tana rintsa ido

Tana kwantar dashi yayi bacci kamar sauran

Daddy ya janyo ta jikinsa, yana shaqar qamshin dake tashi ajikinta, yace baby nayi missing dinki dayawa

Bata gujeshiba tace Nima haka Yaya daddy

Bakinsu yahade waje daya, yakai hannunsa gadon bayanta yazuge zip din rigar ta, yana kissing dinta yana shafa jikinta

Ahankali momy ta turo kofar Dakin tashigo, Kai wannan yaro da jaraba yake, abinda ta guda kenan fa tadauke Amal din tadawo da ita Dakinta, ashe nan dinma ba'a tsira ba

Batare da tace masa koma ba ta nuna masa hanyar waje, Shima babu musu yafice kansa aqasa

Ferfesun Hannunta ta ajiyewa Amal tace gashinan dauki ki cinye tas, kuma kici gaba da biye masa kinji, basai nafada ba aikinji wahalar dakika dandana awajan haihuwa

Amal kanta aqasa cikin ranta tace Kuma fa hakane wallahi, tsaf zata Iya samun wani cikin, dole ne tayi taka tsan tsan

*** *** ***

Washe gari aka radawa yara suna, nafarko yaci sunan mahaifin Shahid Ibrahima Ana kiransa da suhail, Nabiyu yaci sunan Abba, Abdallah anan kiransa da salim saina qarshe yaci sunan Muhammad hamani Ana kiransa da sadat

Salim, sadat, suhail

Mutane da dama sun halarci taron sunan, inda me jego take shiga tana fita cikin kaya iri iri, da temakon anty mufy

Inda me girma gwamna yayi sanarwa yana gayyatar jama'ar bauchi dama kewaye kowa yazo ayi taron suna dashi yaci yasha

Aikuwa jama'ah ba'a nemesu Bama Yaya aka qare bare kuma an nema

Mutane sosai suka zo, ciki harda wasu daga cikin gwamnonin wasu jihohin

Dole Sai Wikki hotel ake Kai mutane, wasu Kuma aka kaisu Zaranda hotel

*** *** ***

After 3 years

Ummi kinga suhail yafasa min bakina

Remote din Hannunta ta ajiye tace mugani, bakin yabude mata tagani, Babu wani alamun fashewa tace yi hakuri, zan kamashi na zaneshi kaji salim

Tana cigaba da kallan widad ta taho tace ummi boyeni sadat zai dakeni

Amal batasan lokacin data dafe kantaba, yaran nan zasu haukatata

Adede lokacin daddy yashigo, yaran suka tafi da gudu sunayi masa oyoyo

Amal tace gara da kazo danna gaji da Raba fada

Daddy yace ku taho nan abokai na

Zama sukai Akan kujera dukansu daddy yafara Jin Qarar kowa sannan yabasu hakuri

Yadubi Amal datake da Dan qaramin ciki yace shikkenan naraba fadan tace eh, Dan Allah idan zaka fita kakaisu wajan momy wallahi nagaji

Sadat yace eh akaimu, Amma banda widad

Salim yace ummi ba zamuje da sadat ba nida widad da salim zamu

Widad tace eh ummi

Suhail ne ya hararеta, daddy da Amal suka kallesu sukasa daria

Itade widad duk lokacin da tazo gidan suhail ne abokin fadanta

Daddy ne ya Hadasu ya rungume su gaba daya, yace to naji, dukanmu zamuje gidan momy, Daganan muje musha ice cream

Gaba dayansu sukace yeeeee

Haka rayuwar gidansu take gudana cikin farin ciki da annushuwa, Amal tana daukeda wani cikin, yayinda Shahida Takeda yarta daya maisunan momy suna kiranta da widad

Maisah ma tana can a jigawa da danta namiji daya maisunan baban sham

Tunda tenure su daddy taqare yace bazai sake neman takaraba, dama wannan ma bashi akayi, Dan haka yahada da gidansu nafarko yahada da wani filin yayi musu tanfatsetsen gida nagani nafada, inda suke gudanar da rayuwar su cikin Jin dadi

TAMMAT BI HAMDULLAH

Anan nakawo qarshan wannan novel na BURINAH Ina roqon Allah yabamu ikon yin amfani da abinda muka tsinta aciki me amfani, ya Allah kayafemin abubuwan dana fada aciki wanda yasabawa shari'ar musulunci

ATAKAICE

Littafin BURINAH yana nuni ne Akan Abu biyu, nafarko yiwa iyaye biyaiya, daddy da Amal burinsu suga sunyiwa iyayensu biyaiya, inda sukaga hakan yahaifar musu da farin ciki me dorewa

Na biyu hakuri da kuma daukan qaddara, Shahid yayi hakuri yadauki qaddara harta kaishi ga auren Shahida, inda daddy yayi hakuri yadau qaddarar rashin matar sa kuma yaga ribar hakan

ABUBUWAN BIRGEWA

gaskya nide abinda yafaru birgeni shine miskilancin daddy, yana so yana kaiwa kasuwa, dakuma yanda shahida take Mutuwar San Shahid

MUTUMIN DAYAFI KOWA BIRGENI

shine baba hamani danda

KARBUWA

novel din BURINAH haqiqa yasamu karbuwa ta yanda banyi zato ba, nagane hananne ta hanyar kirana da wasu sukeyi ta waya wasu Kuma suna turomin saqo ta privet, haqiqa naji dadi hakan

JINJINA GA :

A and F HAUSA NOVEL

UMMY UMMEE NOVEL

MAMAN ABBA NOVEL

AYSHA UMAR NOVEL

AMNAH EL NOVELLA

JINJINA TA MUSSAMAN GA JAMA'AR FACEBOOK GABA DAYANTA

MORE ESPECIALY HAFSAT HAUSA NOVELS (H2)

DAGA QARSHE

DUK ME BUQATAR YAGA PICTURES DIN TRIPLE YAYIMIN MAGANA TA PRIVET

saimun hadu asabon novel dina wanda zaizo muku a kowanne lokaci Bayan Ramadan insha Allah mai suna

WAZAN ZABA?

Ina fatan zakuji dadinsa fiye da BURINAH

Karku manta da Sunan

WAZAN ZABA?

Mrs Usman ce ✍